# KWATANCIN BORIN HAUSAWA DA NA GBAGYI

**NA**

**HALIRU MUSA KUTA**

**APRIL, 2014**

# KWATANCIN BORIN HAUSAWA DA NA GBAGYI

**NA**

**HALIRU MUSA KUTA**

**M.A./ARTS/01242/2008-2009**

**A thesis submitted to the School of Postgraduate Studies, Ahmadu Bello University, Zaria - Nigeria**

**In partial fulfilment of the requirements for the Award of Degree of Master of Arts in African Languages and Cultures (Hausa).**

**Department of African Languages and Cultures, Faculty of Arts**

**Ahmadu Bello University, Zaria-Nigeria.**

**APRIL, 2014**

## DECLARATION

I declare that the work in the thesis entitled “Comparative study of Hausa and Gbagyi bori cults” (Kwatancin borin Hausawa da na Gbagyi) has been performed by me in the Department of African Languages and Cultures under the supervision of Dr. M.Y. Tsoho. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this thesis was previously presented for another degree or diploma at any University.

HALIRU MUSA KUTA

| Name of student | Signature | Date |
|---|---|---|

## CERTIFICATION

This thesis entitled "COMPARATIVE STUDY OF HAUSA AND GBAGYI BORI CULTS" (KWATANCIN BORIN HAUSAWA DA NA GBAGYI) by Haliru Musa Kuta meets the regulations governing the award of the degree of Master of Arts in African Languages (Hausa) of the Ahmadu Bello University, Zaria, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

Date

_____

_____

Dr. Magaji Yakawada Tsoho

Chairman, Supervisory Committee

Date

_____ _____

Prof. Munnir Mamman

Member, Supervisory Committee

Date

_____ _____

Dr. Balarabe Abdullahi

Head of Department

Date

_____ _____

Prof. A.A. Joshua

Dean, School of Postgraduate Studies

## SADAUKARWA

Na sadau}ar da wannan bincike ga Allah (S.W.T) wanda Ya ba ni ikon kammala wannan bincike lafiya. Sai kuma Iyayena, marigayi Malam Musa Kallamu da Malama Habiba, da kuma iyalina, musamman uwargidata Malama Maryam. Allah Ya saka musu da Aljanna Firdausi. Amin!

**ACKNOWLEDGEMENTS**

All praise is to Allah, most high, full of Grace and Mercy; the greater of all, who endured man with spiritual insight, so that man should understand nature, understand himself and know Allah through His wonderful signs. May the peace and blessings of Allah be upon His Apostle, Muhammad (S,AW.), his companions and followers to the day of resurrection.

I am indeed indebted to Dr.Magaji Yakawada Tsoho, of the Department of African Languages and Cultures for introducing me to the area of this study and for supervising the work. His useful suggestions, comments and criticisms have been of tremendous help to me. So also my profound gratitude goes to Professor Munir Mamman for his criticism and beautiful comments on the thesis.

My profound gratitude also goes to all the Lecturers and non academic Staff of the Department of African Languages and Cultures, especially, Prof. [alhatu Muhammad, Dr. Balarabe Abdullahi, Prof. Muhammad Lawal Amin, Dr. Salisu Kargi, Malam Adamu Ibrahim Malumfashi, Dr.Shu'aibu Hassan, Malam Muhammad Rabiu Tahir, Malama Halima Kabir Daura, Malama Hauwa Muhammad Bugaje, for their advice and beautiful contributions on the thesis.

I am similarly grateful to Prof. Aliyu Muhammadu Bunza, Nigerian Languages Department, Usman [anfodiyo University, Sokoto. For his beautiful assessments on the thesis as an external Examiner and Malam Musa Muhammad Sani, Department of Hausa, Niger State College of Education, Minna for assisting me with some materials that made this work possible. My sincere appreciation also goes to Dr. Aliyu Muhammed Busa of Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University Zaria. for his

contribution and brotherly advice on this work. Malam Kabir Muhammed [an'asabe, Director, Niger State Council of Arts and Culture, has also been wonderful towards seeing to the success of this work. I am grateful.

Let me also thank other people collectively, whose names are numerous to mention here, that have so much contributed to the smooth completion of this work. Most especially old men and old women in different communities like: In Niger State, include: Kuta, Shakwata, Chanchaga, Bosso, Minna, Gussoro, Kurebe, Pandogari, Alawa, Chikuba, Bwari, Lokoto, Gawun Babangida, Erana, Galadiman Kogo, Suleja. Gwagwalada, Kwali, Abaji in Federal Capital Territory Abuja. In Kaduna State, include: Udawa, Birnin Gwari, Kujama, Buruku, Chikunu, Kasaya, Gwagwada, Zankoro, Kafari etc. for providing authentic information on how Bori was performed in the olden days and how it is performed today.

Lastly, I wish to thank my immediate and extended family for their patience, understanding, and encouragement. My friends and well wishers who assisted me in one way or the other, either physically, or through prayers, for the successful completion of this study deserve my recognition. I thank you and pray that the Almighty Allah (S.W.T.) will reward you abundantly. **Alhamdu Lillah.**

**{UMSHIYA**

**Shafi**

Title page.....ii

Declaration.....iii

Certification .....iv

Sadaukarwa .....v

Acknowledgement (s) .....vii-xiii

Abstract (Tsakure) .....xi-xii

**BABI NA [AYA: GABATARWA**

1.0 Shimfi]a .....1

1.1 Dalilin Gudanar da Bincike .....2

1.2 Muhimmancin Bincike .....2

1.3 Farfajiyar Bincike.....3

1.4 Matsalolin Bincike.....3

1.5 Hasashen Bincike.....4

1.6 Tarihin Hausawa da na Gbagyi.....4-21

1.7 Dangantakar Hausawa da Gbagyi.....21-35

1.8 Borin Hausawa.....35-41

1.9 Borin Gbagyi.....41-45

1.10 Na]ewa.....45

## BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Shimfi]a.....46

2.1 Wallafaffun Litattafai.....46-50

2 2 Kundayen Digiri.....50

2.2.1 Kundayen Digiri na Uku.....50

2.2.2 Kundayen Digiri na Biyu.....51-54

2.2.3 Kundayen Digiri na [aya.....54-56

2.3 Ma}alu.....56-58

2.3.1 {asidu.....58-60

2.3.2 Mujallu da Jaridu.....60-61

2.4 Na]ewa.....61

## BABI NA UKU: HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

3.0 Shimfi]a.....62

3.1 Ganawa.....62-64

3.2 Sakamakon bincike ta dabarar yin amfani da tambayoyi.....64-65

3.3 Ganawa ta baka da Tattaunawa da Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba.....65-68

3.3.1 Jadawalai.....68-76

3.4 Matsalolin da aka fuskanta wajen tattara bayanai.....76

3.5 [akunan Karatu.....76

3.6 Yanar – Gizo.....77

3.7 Na]ewa.....77

**BABI NA HU[U: KWATANCIN BORIN HAUSAWA DA NA GBAGYI**

4.0 Shimfi]a.....78

4.1 Kwatancin Borin Hausawa da na Gbagyi.....78-80

4.1.1 Sunayen Iskoki ko Aljannu.....80-88

4.1.2 Halayen Iskokin Borin Hausawa da na Gbagyi.....88-90

4.1.3 Tufafin ‘yan Borin Hausawa da na Gbagyi.....90-92

4.1.4 Girka.....92-98

4.1.5 Kayan ki]an Bori.....98

4.1.6 Amfanin Borin Hausawa da na Gbagyi.....99-101

4.1.7 Kamancin Borin Hausawa da na Gbagyi.....101-103

4.1.8 Bambancin Borin Hausawa da na Gbagyi.....104-105

4.2 Na]ewa. .....105-106

**BABI NA BIYAR: KAMMALAWA**

5.0 Shimfi]a.....107

5.1 Na]ewa.....107-108

5.2 Kammalawa.....108-110

5.3 Shawarwari.....110-111

Manazarta.....112-117

Rataye na [aya.....118-120

Rataye na Biyu .....121

Rataye na Uku.....122-142

## TSAKURE

Wannan bincike ya kwatanta borin Hausa da na Gbagyi (Gwari) domin nuna kamanci da bambanci da ke tsakaninsu. Samuwar Iskoki dai wani imani ne da kowace al'adar al'ummar duniya ta yi imani da shi. Imanin mutanen duniya game da Iskoki abu ]aya ne ta fuskar kasancewarsu ~oyayyu, buwayayyu, masu ban tsoro, masu karkatar da mutane, kuma masu }arfi a kan mutane. Shi kuma bori a matsayin bautar Iska da]a]]iyar al'ada ce, da ke cikin hanyoyin addinin gargajiya na Hausa da kuma Gbagyi. Don haka, ha]uwa da zamantakewa da Hausawa suka yi da Gbagyi ya haddasa sauye-sauye na yanayin aiwatar da borin Gbagyi ta fuskokin sunayen Iskoki ko Aljannu da halayen 'yan bori da tufafin 'yan bori da kayan ki]an 'yan bori da girka da kuma amfanin 'yan bori ga jama'a. Wannan bincike ya fito da wa]annan sauye-sauye a fili domin a fahimci kamanci da kuma bambancin borin al'ummun guda biyu. Daga cikin batutuwan da aka tattauna akwai tarihin Hausawa da Gbagyi, da borin Gbagyi na asali kafin su ha]u da Hausawa. A farkon wannan bincike, an kawo borin Hausawa, sannan an nuna dangantakar Hausawa da Gbagyi ta yadda suka ha]u har borinsu ya haddasa sauyi a kan na juna musamman a manyan garuruwan Gbagyi da aka yi bayanin ha]uwarsu kamar: Kuta da Minna da Suleja duk na jihar Neja da kuma Birnin Gwari ta jihar Kaduna. A }arshe, binciken ya gano matsanancin tasirin da borin Hausawa ya yi a kan na Gbagyi ta yadda a yau, kusan dukkan 'yan borin Gbagyi, suna aiwatar da bori ne ta salon yadda suka ga 'yan borin Hausawa na aiwatarwa.

## ABSTRACT

This research is a comparative study of Hausa and Gbagyi bori cults. It compares and bring out the similarities and differences between the two cults. Every society of the world has the belief in the existence of spirits, they believe that the spirits or jinns are invisible can influence human behaviour because of their power over human beings. Bori as a way of worshipping spirits, is an old culture and a traditional religion of the Hausa and Gbagyi people. Interaction between Hausa and the Gbagyi has brought about changes in the original mode of bori practice, especially in the aspects of; names of the spirits, the character of the possessed persons, mode of dressing, musical acompaniments, mode of initiation, the status and importance of the bori cult. This research brought out the changes such as the similarities and the differences between the bori cults of the two societies. Issues discussed at the beginning of the thesis are; the history of the two people (Hausa and Gbagyi), the bori of the Gbagyi and Hausa before their interaction, and the relationship between the two which brought about changes in mode of bori practice of the Gbagyis, particularly the selected towns which include: Kuta, Minna, Suleja all in Niger State and Birnin-Gwari in Kaduna State. At the end, the research is able to find out that the Hausa bori activities has influenced that of the Gbagyis today, they now practice bori similar to the way it is performed by the Hausa bori possessed persons.

## BABI NA [AYA: GABATARWA

### 1.0 Shimfi]a

Bori a matsayin bautar Iska yana ]aya daga cikin hanyoyin addinin gargajiya na Hausa, wato al'ada ce da ta da]e a wurin Hausawa. Sun fara ta tun lokacin da suke duk Maguzawa ne kuma har yanzu da kusan dukkansu Musulmi ne wasun su ba su daina ba. (Ibrahim, 1982:35). Haka ma al'amarin yake a wajen Gbagyi su ma sun da]e suna tsafi da bauta wa gumaka da Iskoki a matsayin addininsu na gargajiya. A bayan zuwan addinin Musulumci ne a sanadiyyar ha]uwarsu da Hausawa, da yawansu suka Musulumta amma har a yau wasunsu ba su fasa yin borin ba, amma a salon irin na Hausawa.

Dangane da wannan bayani na bisa, za a iya cewa al'ada ta }unshi tafarki wanda wata al'umma take rayuwa a cikinta dangane da yanayin addini da abinci da tufafi da muhalli da aure da kasuwanci da shugabanci da bukukuwa da sauran abubuwa wa]anda suke da ala}a da haka.

Ibrahim (1982:35), ya ce:

> Al'adun al'umma, abubuwa ne masu rai wa]anda
> sukan shafi dangogin rayuwa daban-daban. Al'ada
> na da mazubi faffa]a.Wasu al'adu na al'umma
> sukan ]ore, su ci gaba da bun}asa, sannan kuma
> sukan dakushe har a kai lokacin da za a watsar da
> su saboda tasirin ba}in al'adu. Ta haka ne al'adu
> suke zama da]a]]u ko sababbi wato al'adu na
> gargajiya da na zamani.

Wannan bincike zai kwatanta borin Hausawa ne da na Gbagyi. Abubuwan da za a duba a wannan babi sun ha]a da: Dalilan gudanar da bincike da muhimmancin bincike da farfajiyar bincike da matsalolin bincike da hasashen bincike. Sai kuma tarihin al'ummun biyu wato Hausawa da Gbagyi da bayanai a kan dangantakarsu da yanayin borinsu.

### 1.1 Dalilin Gudanar da Bincike

Dalilan wannan bincike za su kasance kamar haka:

- An yi nazarce-nazarce da yawa a kan borin Hausawa, misali, Badejo (1980) da Ibrahim (1982) da Dutse (1989) da Besmer (1977) da Bunza (2006) da Gobir (2001) da sauransu. Sai aka lura cewa an yi watsi da wannan fanni da ake neman amincewar gudanar da bincike a kai wato: Kwatancin Borin Hausawa da na Gbagyi', kuma wani muhimmin ~angare ne na al'adun al'ummar, Shi ya sa aka ga ya dace a yi nazarinsa domin cike wannan gi~i.

- Cu]anyar Gbagyi da Hausawa, ya sa aka sami sauyi da ya haddasa Gbagyi suka koma yin bori irin na Hausawa. Don haka ne ya sa za a gudanar da bincike domin fito da wa]annan sauye-sauye da aka samu a fili.

### 1.2 Muhimmancin Bincike

Wannan bincike zai zama wani harsashi ne na kafa wani bincike kan kwatancin borin Hausawa da na Gbagyi domin gina ko bun}asa al'adun al'ummun guda biyu. Rashin nazari a wannan fage ya }arfafa muhimmancin wannan binciken.

Wannan bincike idan aka ci nasarar kammala shi, zai ilmantar da mutane musamman wa]anda ba su san borin Gbagyi ba, wa]anda suka sani kuma, zai zama tunatarwa ko kuma }arin haske ne a gare su.

Har ila yau, idan wannan bincike ya sami kar~uwa, zai zama ci gaba ne a kan bincike da kuma rubuce-rubucen da idan akwai wa]anda suka fara yi a kan bori amma ba su samu kammalawa ba, wannan zai }ara masu }arfin gwiwar cigaba da nasu binciken da suka fara.

Idan an kammala binciken, za a buga shi ya zama kundi da littafi, sannan a kai shi ]akunan karatu da ke makarantu daban-daban tare da saka shi a yanar-gizo don amfanin manazarta.

Sannan kuma, wannan bincike zai zama wata hanya ce da za a yi amfani da ita wajen adana tarihin }asar Hausa da na Gbagyi da addinan gargajiyansu da Borinsu da yadda ake yin su da can da yanzu.

### 1.3 Farfajiyar Bincike

Duk da an bayyana cewa ba a yi wani katafaren aiki a fagen nazarin kwatancin Borin Hausa da na Gbagyi ba; kama da yadda Gbagyi ke aiwatar da Bori jiya gabanin ha]uwarsu da Hausawa ‘yan Bori da yadda suke aiwatar da shi a yau, ba za a yi kandamau ba a wanan bincike ta hanyar nazartar dukkanin ~angarori na Bori a dukka garuruwan Gbagyi ba. Za a yi }o}arin kwatanta Borin al’ummun biyu domin gano kamanci da bambancinsu a fannonin: Sunayen Iskoki da halayen Iskokin ‘yan Bori da tufafin Bori da kayan ki]an Bori da Girka da kuma amfanin ‘yan Bori.

Idan aka ga an ta~o bayanai a kan tarihi da dangantakar Hausawa da Gbagyi, an yi haka ne domin a }ara haske ko kuma a kyautata kwalliyar bincike, domin ba bisa su ne binciken zai ta’alla}a baki ]aya ba.

Da yake binciken zai ta’alla}a ne kan kwatancin borin Hausa da na Gbagyi, za a ta}aita bayanai ne a kan za~a~~un manyan garuruwan Gbagyi da suka ha]a da: Minna da Kuta da Suleja (Abuja a da) da ke jihar Neja da Birnin Gwari a jihar Kaduna.

### 1.4 Matsalolin Bincike

Matsalar da ta sa aka za~i gina wannan bincike a kan kwatancin Borin Hausawa da na Gbagyi, ba ta rasa nasaba da lura da aka yi da ]imbin kamanci wajen aiwatar da Borin Gbagyi ya yi a yau da na Hausa, al’ummar Gbagyi ba ta farga ba, don haka za a gudanar da bincike don magance wannan matsala.

Har wa yau akwai matsalar }arancin nazarce-nazarce kan sauye-sauyen da aka samu a Borin Gbagyi a dalilin ha]uwarsu da Hausawa, wannan binciken zai taimaka wajen kwatantawa domin fito da kamanci da bambanci na Borin Hausawa da na Gbagyi fili.

## 1.5 Hasashen Bincike

Domin }o}arin kawar da wasu daga cikin matsalolin da suka dabaibaye wannan fage kamar yadda aka ambata, ya sa wannan bincike yin hasashe kamar haka:

- Kamar yadda Besmer (1975), da Nicole (1991), da Yahaya da Wasu (1992:88), da Gobir (2001) da Bunza (2006:21), suka nuna cewa bori a matsayin addinin gargajiya na Hausawa, yana faruwa ne ta rashin lafiya da ya danganci ha]uwa da Iska wanda a wasu lokuta kafin a samu waraka ko a zaunar Iska a kan majinyaci, sai an ha]a da girka. To ko a borin Gbagyi ma haka zancen yake?
- Binciken zai yi }o}arin gano ko sauye-sauyen da borin Gbagyi ya samu ya faru a dalilin cu]anyarsu da Hausawa kuma ko shi ne ya kawo ~acewar salon na Gbagyi a yau?
- Binciken zai yi }o}arin fayyace shin ko shigowar addinin Musulumci da na Kirista cikin }asashen Hausa da na Gbagyi ya }arfafa aiwatar da bori ne ko ya gurgunta shi ne?
- Shin akwai wata ala}a tsakanin Hausawa da Gbagyi kafin shigowar addinan nan biyu (Musulumci da Kiristanci)?

## 1.6 Tarihin Hausawa da Gbagyi

Magana a kan tarihi da asalin Hausawa tana da fa]i kuma akwai ra'ayoyi mabambanta juna dangane da asalin wannan al'umma. Dalili a nan shi ne, (saboda) Hausawa sun bazu a }asar Afirika ta Yamma a lokuta daban-daban, kuma bisa dalilai daban-daban. Duk da haka suna tafe da wannan harshe nasu. Wato 'Hausawa' masu magana da harshen Hausa shi ne sunan da suke kiran kansu da shi. Sannan da dama daga cikin wasu 'yan }abilun masu makwabtaka da su, sun san su da wannan

sunan wato “Hausawa”. Sai dai akwai wasu }abilun da suke kiransu da wani sunan ba Hausawa ba duk da yake suna nufin Hausawan ne da harasansu. Kamar misali, Fulani suna kiransu “Ha~e”. Jukunawa na kiransu “Abakwai” (Abakwariga) Yarbawa kuma na kiransu “Gambari” da dai sauransu. Hausawa su ne mutanen da ke zaune a }asar Hausa.

Akwai ra’ayoyi daban-daban dangane da asalin Hausawa. Wa]annan ra’ayoyi sun ha]a da ra’ayin malaman tarihin da ra’ayin masu nazarin harsuna, wato masana harsuna, sai kuma ra’ayin su kansu Hausawan da suke fa]a a duk lokacin da aka bukaci su fa]i asalinsu wanda suke danganta shi da zuwan Bayajidda Daura.

Ta ~angaren malaman tarihin an sami ra’ayoyi daban-daban game da asalin Hausawa. Wa]annan malamai sun yi rubuce-rubuce da aikace-aikace masu tarin yawa dangane da asalin Hausawa. Domin su samar da ingantattun hujjoji kuma kar~a~~u. Dalili shi ne a lokacin da can kafin }arni na goma sha shida ga alama Hausawa duk da ka]aitar harshensu da al’adunsu, ba su ha]a kansu sun sami wani suna guda ]aya da za su kira kansu da shi ba. Sai dai kowa ya yi ta}ama da garinsu kawai. Saboda tarihin ya nuna kowane gari na }asar Hausa a da can zaman kansa yake yi. Kowani sarki yana mulkin kansa babu wani abin da ya ha]a sarakuna da juna sai ya}e-ya}e da hare-hare. Sai daga baya ne mamayar mulkin ba}i kamar daular Songhai da ta Barno da ta Kwararrafa ta fara ha]a kawunansu. Daga nan kuma sai jihadin Shehu Usmanu [an Fodiyo ya zo ya da]a ha]e su wuri ]aya. Fagge (2000:4)

Ra’ayoyin wa]annan malamai sun ha]a da ra’ayin  Johnson cikin littafinsa mai suna *The Fulani Empire of Sokoto volume II* (1967), ya nuna cewa wani lokaci wasu mutane da ake kira Berbers sun ratso sahara zuwa }asar ba}ar fata. Suka yi auratayya da ba}a}e wanda wannan shi ne ya yi sanadiyyar samuwar Hausawa. Ya }ara da cewa wannan abu ya faru ne tsakanin }arni na (1050-1100).

Wani masanin tarihin mai suna M.G. Smith a littafinsa mai suna *The Beginning of Hausa Society* (Asalin Al'ummar Hausa) ya yi bayani cewa akwai }aura da ta faru daga gabas zuwa wurin da yau ake kira }asar Hausa. Wannan }aura ta faru ne tsakanin shekara ]ari da casa'in zuwa dubu ]aya wato (190-1000 A.D.) ya kuma nuna cewa a dalilin yin wannan }aura shi ne Larabawa suka ya}i mutanen Arewacin Afirika. Wannan ya yi sanadin tasowar mutanen wannan wuri zuwa kudancin wurin da suke kira }asar Tukururu, a nan suka yi auratayya da mutanen wurin wanda ya yi sanadiyyar samuwar Hausawa.

A ra'ayin masana Harsuna, Abdullahi Smith (1978) da Sutton (1979), Smith ya danganta asalin Hausawa da wani lokaci da Hausawa suke zaune a wani wuri da a yau yake yankin }asar Nijar. Shi wannan masani ya nuna cewa kimanin shekaru masu yawa da suka shu]e cewa shi wannan wuri ya ni'imtu da bishiyoyi da ciyayi da ruwa. Bugu da }ari, rabin wannan wuri yana da wata wadatacciyar }orama wadda aka ta~a samunta a wannan wuri da ta taimaka wajen gudanar da rayuwa da cigaban al'ummar da ke zaune a wannan wuri na wannan lokaci. Smith ya cigaba da cewa daga baya, kwatsam sai abubuwa suka fara canzawa saboda sauye-sauyen yanayi na duniya wanda daga bisani shi wannan wuri sai ya fara canzawa zuwa daji, sannan sai ya koma Sahara. Ita kuwa wannan }orama sai ta }afe }ar-}af aka kuma neme ta sama da }asa, ba ita ba dalilinta a wannan yankin. A ~angaren gabashin wannan wuri bai ha]u da wannan matsala ta }afewar ruwan ba wanda a yau ake yi masa la}abi da tafkin Chad.

Smith ya nuna cewa a sandiyar wa]annan matsaloli ne Hausawan da suke zaune a wannan wuri sannu a hankali suka dinga }aura suna komawa kudancin wannan yanki saboda ganin ni'imar ta koma wannan ~angaren. Smith ya bayyana cewa wurare kamar Kano, da Katsina da Daura da Gobir da Zazzau da sauransu na daga cikin wannan yanki da Hausawa suka mamaye.

Sutton (1979), Shi kuwa danganta asalin Hausawa ya yi da cewa al'adun Hausawa sun samo asali ne daga }asar Ha]eja. Shi dai wannan masani ya bayyana cewa ni'imar da take yammacin

wannan yanki na Tafki wani ~angare ne da ke cikin Kano da kuma Ha]eja. Kuma mutanen da suke zaune a tsakanin Kano-Ha]eja sun dogara kacokam ne wajen sana'ar su, (Kamun Kifi) wajen tafiyar da rayuwarsu. Sutton ya cigaba da cewa, su wa]annan mutane su ne suka fara }ir}irar al'adun Hausa kuma daga wurin su ne tushen asalin al'adun Hausawa da kuma harshen Hausa sannan daga bisani suka bazu zuwa arewacin da kuma yammacin yankunan da suke zaune kama ya zuwa sauran }asashen Hausa da muka san su a yau.

Ra'ayin Hausawa game da asalinsu a nan shi ne labarin da suke bayarwa wanda suke danganta shi da zuwan Bayajida }asar Hausa da yadda ya tafiyar da mulkinsa. Bisa bincike da kuma rubuce-rubuce da ake da su na tarihin, akwai }aurace-}aurace da aka yi ta samu daga }asashen Asiya zuwa }asashen Afirika. To a sanadiyyar haka ne Hausawa suke cewa asalinsu shi ne wai wa]ansu mutane ne da suka yiwo }aura, suka taso daga Kan'an suka zo Falas]inu suka zauna. Sai wani da ake zaton kaka ne a wajensu wato Najib wanda ya taso da iyalansa ya komo Libiya. An ce a wannan wuri ne wani ]ansa mai suna Abdud-Dar ya nemi sarauta, da bai samu ba sai ya taso da iyalinsa ya yiwo kudu har ya zo wata }orama ya zauna. Wannan wuri an ce shi ne tsohon birnin Daura na yanzu. An ce wannan mutum ya sauka ne a bakin wani rafi wai shi Kusufu, (tsohon birnin Daura). Nan ne garin da mutanen suke zaune kafin su yiwo }aura zuwa Sabon Birni, wato garin Daura na yanzu. Garin yana nan misalin kilomita bakwai arewa da garin Daura na yanzu.

A wannan wuri Abdud-Dar ya zauna, ya hayayyafa. An ce 'ya'yansa ne suka ci gaba da sarautar wurin, kafin Magajiya Daurama wadda ita ce ta tara a jerin matan da suka mulki Daura. Ga sunayensu kamar haka:

Yakano
Gafani
Yakari
Kafara
Kadanta

Gidir-Gidir

Waiwana

Awairama

Daga Awairama sai Sarauniya Daurama, wato Daurama ta gaji yarta Awairama, ta zama magajiya, wadda aka ce an killace ta. Wato bisa al'ada akwai wasu abubuwa da ake yi wa wadda ake sa ran za ta yi sarauta, ta yadda ba za ta damu da maza ba. A lokacin da Daurama take mulki da ma kafin ta, a wannan lokacin yanayin zama ya sa tilas mutane su yi wa ruwa kyakkyawar kulawa da kuma adana shi. An ce akan gina rijiyar kamar kusan gaba hamsin zuwa tamanin kafin a sami ruwa. Su kuma dabbobi a wannan lokaci gaba ]aya ake ha]awa a bayar da su zuwa wurin kiwo, ko a ha]a wa 'yan-a-sako, mai su da yawa ya hayi wa]anda za su yi masa. Idan dabbobi sun dawo daga kiwo, idan rana ta yi sai a kai su bakin rijiyar domin ban ruwa.

A irin haka ne sai aka lura cewa akwai wani bajimin sa a garken Sarauniya wanda ]abi'arsa ce kullum ya ware kansa shi ka]ai, ya gudu zuwa wani sur}u}i ya sha ruwa ba tare da 'yan'uwansa ba. Da aka lura da haka, sai aka sanar da Sarauniya halin da ake ciki, sai ta ba da umarni cewa a faki idonsa, a sace, a bi shi a ga inda yake zuwa da kuma abin da yake yi a wurin kamar kullum. Ranan an je kiwo an dawo, an ratsa da dabbobi wajen shan ruwa, sai aka ga wannan sa ya bar bakin rijiyar, ya kauce. Sai wani ya bi shi a baya har suka shiga wani wuri mai duhu. Can sai wannan mutum ya ga san ya dur}usa a wani wuri, ya da]e sannan ya taso ya dawo. Da san ya wuce sai mutumin ya }arasa wurin, sai ya le}a, sai ya ga ashe wani rami ne cike da ruwa mai kyau. Da zuwa gida ya je ya ba wa Magajiya labari.

Jin wannan, sai Sarauniya ta aika da mutane aka je aka gyara wurin ya zama rijiya. Jama'a suka sami wurin ]ebo ruwa cikin sau}i. Samun wannan wuri ke da wuya, sai wata matsala ta taso, wato sai aka sami wata macijiya ta fito daga cikin wannan rijiyar tana hana jama'a ]ibar ruwa a kullum sai dai Juma'a. Wannan macijiya sunanta "Sarki".

Daga wannan lokaci ne sai Allah ya kawo wani mutum wannan gari wato Bayajidda wanda ya biyo ta Barno kafin ya isa Daura. An ce sunan Bayajidda na asali shi ne Abu-Yazid wanda yake shugaba ne na wata }abila ta Larabawa, da suka taso daga Madina suka biyo ta Afirika ta Arewa har suka zo Barno. Wasu suka ce a'a asalinsa shugaban wata ]ari}a ce ta Musulunci mai suna "Khawaji" wai cewa wa]annan mutane sun zo Afirika ta Arewa, suka ya}i sarakunan Kairo (Cairo) su kuma suna bin ]ari}ar Shi'a ne. Suka zo Borno daga nan suka tashi zuwa Daura. A wata fa]ar kuma, an ce dokinsa girdi, ya hau ya gudu shi da matarsa. Fagge (2000:8)

An ce wannan mutum ya zo Barno ya zauna tare da mutanensa. A lokacin da Bayajida ya sauka a Barno, rundunarsa ta fi ta sarkin Barno yawa. Saboda haka sai mutanensa suka ba shi shawarar su kashe sarkin Barno su gaje sarautarsa. Da fadawan sarkin Barno suka sami wannan labari sai suka gaya wa sarkinsu. Da ya nemi shawararsu a kan abin da za su yi, sai fadawan nan suka ce ai ba wani abin yi illa ya ba shi 'yarsa ya aura. Don in ya zama surikinsa ba zai cuce shi ba. Sai sarkin Barno ya aura wa Bayajida 'yarsa mai suna 'Magaram'. Bayan an yi auren sai sarkin Barno ya fito da wata dabara don ya raunana }arfin rundunar Bayajidda. Wato kullun idan za shi ya}i }asashen waje, sai ya nemi surukinsa ya ba shi aron wasu daga cikin dakarunsa don su taya shi ya}i. Saboda sarakuta, sai nan da nan Bayajidda ya aiko da dakaru. Idan sarkin Barno ya tafi ya}i, bayan ya yi nasara ba zai dawowa Bayajida da mutanensa ba, maimakon haka, sai ya na]a musu sarautu a garuruwan da ya ci da ya}i. Idan ya dawo sai ya shaida wa Bayajida cewa mutanen da ya ba shi aro sun nuna jaruntaka a fagen ya}i, don haka ya yi musu tukuici da sarauta a wasu garuruwa. Duk wannan bai sa Bayajida ya lura da cewa makirci ba ne, a tunaninsa nasara ce, sai ya yi murna an ce jama'arsa sun yi }o}ari. Haka dai sarkin Barno ya yi ta yi. Da haka, da haka har rundunar Bayajida ta }are ya rage ba kowa daga shi sai matarsa Magaram. Da sarki ya ga haka, sai ya yi niyyar hallaka shi. Da matarsa Magaram ta sami labari, sai ta shaida wa mijinta abin da yake faruwa. Nan da nan, sai Bayajida ya ]aura wa dokinsa sirdi da daddare ya ]auki matarsa mai tsohon shigar ciki suka bar garin.

A lokacin da suka isa Garun-gabas }asar Ha]ejia, sai na}uda ta kama matarsa Magaram. Saboda haka sai ta ce ya sauke ta a nan, shi ya cigaba da tafiyarsa don kar a zo a kama shi.

A wannan gari Magaram ta zauna ta haifi ]anta namiji mai suna Birom. Daga baya shi ne ya zama sarkin Garun–gabas. Shi kuma Bayajida ya ci gaba da tafiya ya yiwo yamma. A kan hanyarsa ya ratsa ta Gaya, da ya ga garin ma}era ne, sai ya sa suka }era masa takobi, wadda yanzu haka tana nan a cikin kayan sarautar Daura. Daga nan Gaya, Bayajida bai yi zango a ko'ina ba sai a Daura. Ya tarar a lokacin sarauniya Daurama ce take kan gadon sarauta. Da zuwansa cikin dare, sai ya sauka gidan wata tsohuwa mai suna "Ayyana". A cikin daren Bayajida ya nemi ta ba shi ruwa zai bai wa dokinsa. Sai ta gaya masa babu. Sai ya nemi ta ba shi guga don ya je rijiyar ya ]ebo ruwa. Ayyana ta ba shi labarin cewa ai a garin nan duk daga cikin rijiyar ]aya kawai suke samun ruwa, wato rijiyar "Kusugu" kuma a cikin rijiya akwai wata macijiya wadda ake kira "sarki", ba ta barin kowa ya ]ebi ruwan rijiyar daga Juma'a sai Juma'a. Idan kuwa mutum ya kuskura ya je ba ranar Juma'a ba, to macijiyar za ta biyo guga ta fito ta sare shi ya mutu. Wannan magana da Ayyana ta fa]a wa Bayajida ba ta sa ya tsorata ba. Sai ya ce ta ba shi guga ya tafi ya ]ebo. Yana zura guga kuwa, sai macijiyar nan ta biyo igiyar guga ta fito waje don ta kashe mai jan ruwa. Fitowarta ke da wuya, sai Bayajida ya tare ta da mashi ya ]auko takobinsa ya sare kan ya jefar da gangar jikin a bakin rijiyar. Kan kuma ya saka a cikin jakarsa.

Daga nan ya ]ebi ruwan ya sha, ya kuma bai wa dokinsa ya sha. Sa'annan ya ]ebi wani ya tafi da shi a gugan ya kai wa tsohuwa mai masaukinsa.

Gari na wayewa, sai mutane suka ga gawar macijiya jibge a bakin rijiya, sai mamaki ya kama su. Nan da nan sai labari ya je gurin Magajiya wadda ta zo da kanta ta ga wannan aiki. Da sarauniya ta ga haka, murna ta kama ta, ta kuma yi al}awari cewa duk wanda ya yi wannan aiki za ta raba garinta biyu ta ba shi rabi ya yi mulki. Da jin haka sai mutane suka yi ta kwararowa suna zuwa suna cewa su ne suka kashe macijiya. Idan sarauniya ta bukaci su kawo kan don a tabbatar da

hakan sai su yi turus. Wasu kuma sai su je su kaso wasu macizan, su kawo kan, amma da an gwada sai a ga ba na macijiyar ba ne. A cikin haka ne sai tsohuwar nan Ayyana ta ji labari nan da nan ta je fada ta sanar da labarin ba}on da ta yi da daddare wanda yake tare da wata dabbarsa mai kamar saniya. Ta fa]i duk yadda suka yi da shi, lokacin da ya nemi ta ba shi ruwa. A }arshe ta ce bayan ta ba shi guga ya tafi wurin rijiyar, har ma da ya tashi dawowa ya taho mata da ruwa a gugan. Ta ce tana zaton shi ya kashe wannan macijiyar. Sai sarauniya ta sa aka kira shi, ta tambaye shi. Ya kwashe duk yadda suka yi da tsohuwa da kuma yadda ya sare kan macijiyar ya fa]a mata. Ya ]auko kan ya nuna mata. Da aka gwada, sai aka tabbatar shi ne. Sai sarauniya ta bayyana masa alkawarin da ta yi wa wanda ya kashe wannan macijiya. Sai Bayajida ya nuna cewa shi ya fi so ya aure ta, ba ya son a ba shi rabin gari ya yi mulki.

Dama can duk wadda ake sa ran za ta yi sarauta, ana yi mata wasu tsibbace-tsibbace, a killace ta, ta yadda ba za ta damu da maza ba. Don haka sarauniya ba ta da aure, amma a wannan karon sai sarauniya ta yarda ta aure shi. Ya tare a gidanta. Sannan sai ta ba shi }war}wara ya kulle. An ce tun daga wannan lokaci idan mutane za su wurin Bayajidda, sai su ce za mu gidan “Makas-sarki” wato wanda ya kashe sarki (macijiya). A hankali, a hankali, sai mutane suka daina cewa makas sarki, a maimakon haka sai suke cewa “sarki” kawai. To tun daga wannan lokaci ne Hausawa suka fara amfani da kalmar “sarki” wajen ambaton shugabanninsu, (Ibrahim 1982:18). Saboda da can sunan sarautar sarauniya “Magajiya”.

A hankali da tafiya ta yi tafiya, sai }war}warar nan wadda Magajiya ta bai wa Bayajida ta haihu, ta haifi ]a namiji. Sai ta ro}i Bayajida da ya sa wa yaron suna Mun-kar~i-Gari, ya yarda aka sa masa wannan suna. Nufin wannan }war}wara shi ne habaici ne take yi wa Sarauniya saboda ita ba ta haihuwa. Daga baya kuma sai Sarauniya ta haihu bayan an karya asirin da aka yi mata na sarauta. Da ta tashi haihuwa sai ta haifi ]a namiji. A lokacin ita kuma sai ta nemi a sa masa suna ‘Bawo’ wato “kawo” Ma’ana a nan ta rama habaicin da }war}wara ta yi mata saboda ta haifi ]a

namiji da mijin Sarauniya, don tana sa ran bayan Sarauniya ta mutu ]anta ne zai yi sarauta. Saboda sun kar~e gari ke nan. Saboda haka ita kuma sai Sarauniya ta rama, ta ce kawo garin da kuka kar~a.

Bayan mutuwar Magajiya da mijinta, sai Bawo ya kama sarautar Daura. Mutane suna kiransa da la}abin "sarki" A lokacinsa, wato lokacin da yake kan gadon mulki, Bawo ya haifi 'ya'yansa guda shida duk maza. Wa]annan 'ya'yan nasa su ne kamar haka:

Garori
Bagauda
Gunguma
Ubandoma
Kumayau
Zamna-kogo

**Hausa Bakwai**

Tun lokacin mulkin sarauniya Daurama aka fara samun rashin zaman lafiya a wasu }asashen Hausa. Mutane da dama daga ko'ina suna ta kuka a kan yawaitar zalunce-zalunce da kashe-kashe na babu gaira babu dalili. Hakan ta sa har suka kai kukansu suna ro}on sarauniya Daurama wadda ita ce ka]ai take tsaye a kan mulkin }asarta don ta yi musu agaji a kan wannan masifa da ta same su. Misali, kamar yadda Ibrahim (1982:19) ya nuna cewa a Kano tun daga lokacin da Barbushe ya mutu, sai mulkin garin ya fara rauni, ba a kuma samun wani shugaba jarumi mai }arfi kamar sa ba. Ganin haka sai mutane suka yi ta karya dokoki, marar }arfi ya zama abincin mai }arfi. Haka kuma sai ba}i daga garuruwan da suka makwabci Hausawa suna ta kawo musu hari da ya}e-ya}e, su }wace dukiyoyinsu, su kuma kame mutanen su mayar da su bayi. Ana cikin haka ne sai yunwa mai tsanani ta fa]a wa }asashen Afirika, musamman }asashen Afirika ta Arewa. Saboda haka sai Buzaye da Azbinawa suka yi ta }aura daga }asashensu suna komowa }asar Hausa, musamman Kano inda take da albarkar ruwa da abinci. An ce bayan }arewar yunwa, sai wa]annan ba}i da suka zo suka zama al}alai a wurin Hausawa. Sace-sace da zalunce-zalunce suka yi yawa. Sai jama'a suka sake aika wa Daura domin a taimake su a tsare lafiyarsu da ta dukiyarsu. A wannan lokacin

Sarauniya ta rigaya ta mutu; sai ]anta Bawo shi yake sarauta. Da ya sami labari sai nan da nan ya na]a ‘ya’yansa su tafi su yi sarauta a wa]annan garuruwa domin su dawo da zaman lafiya a wurin. Ga yadda Bawo ya yi na]in, da kuma garuruwan da ya tura da wakilai:

Kano – Bagauda

Daura – Garori

Zazzau – Gunguma

Gobir – Uban-doma

Katsina – Kumayau

Rano – Zaman-kogo

Garun–gabas – Birom

Wannan na }arshen, wato Birom ba ]a ne a gurin Bawo ba, }aninsa ne wanda ‘yar sarkin Barno mai suna Magaram ta Haifa wa Bayajidda a Garun-Gabas. Da ya girma sai aka na]a shi sarkin garin. Don haka duk inda aka yi wannan na]i guda bakwai su ne ake la}anta su da asalin garuruwan Hausa Bakwai Wa]anda zuwan Bayajida ya yi sanadiyyar kafuwar daulolinsu, kamar yadda tarihi ya nuna.

**Banza Bakwai**

Dangane da kafuwar daulolin Hausa kuma shi ne wannan }war}wara da Magajiya ta bai wa Bayajidda har ta haifa masa ]a namiji wanda ta bukaci ya sa masa suna mun-kar~i-Gari. An nuna cewa kafin mutuwarsa shi ma ya haifi ‘ya’ya guda bakwai wa]anda ba a tabbatar da samun wata shaida ta sunayensu ba, su ne asalin sarautar }asashen banza bakwai. Wa]annan garuruwa su ne:

Kebbi

Zamfara

Yawuri

Gwari

Ilori

Nufe

Jukun

Wannan shi ne dangane da ra'ayin Hausawa game da asalinsu, koda yake akwai rauni da rashin amincewa a kan wa]annan abubuwa da suka faru a kan maganar zuwan Bayajida Daura wanda aka yi bayani a kan hakan.

Mafi inganci daga wa]annan ra'ayoyi daban – daban a kan asalin Hausawa shi ne ra'ayin malaman tarihi cewa Hausawa da harshensu sun samo asali ne daga wani wuri gabas da inda suke a yau. Misali masana kimiyyar binciken tsofafin abubuwa sun ce kamar a }alla shekaru dubu hu]u da suka wuce fa]in tabkin Cadi ya kai fiye da goman yadda yake a yanzu. A lokacin da tafkin ya fara }afewa sai mutanen da ke zaune a wurin suka ri}a yiwo }aura suna yowa Arewa maso yammacin wurin. Haka kuma a wata fa]ar cewa aka yi Bahaushe daga }asar Habasha ya fito, amma a sanadiyyar }aurace - }aurace aka warwatsu a wurare daban – daban. {aurace - }auracen nan sun faru ne a sanadiyyar ya}e-ya}e da anoba da fatauci da neman ilimi da sauransu. Misali, Malam Kabir Getso (2003:10) ya da]a fito da wannan bayani yana nuna cewa Bahaushe daga }asar Habasha ya fito, saboda ya ce a shekara dubu biyu kafin haihuwar Annabi Isah (AS) akwai dauloli biyu Misira da Habasha. Ya ce Hausawa sun baro Misra ne saboda fa]uwar Misira a ya}i. Saboda }asar Girka da ta Rum Farisa sun cinye ta da ya}i. Ya ce a sanadiyyar wa]annan ya}e-ya}e ne suka warwatsu, suka biyo ta Sahara, wato ta Arewa maso Gabas da Libiya ta yanzu da ]an wani ~angare na Arewacin Cadi. Daga nan suka yiwo kudu inda suka fa]o arewacin Nijeriya ta yanzu. Fagge, (2000:3-15).

Su ma Habib da Wasu (1982:6), sun ce: "Shin Hausawa sunan }abila ne ko sunan

> harshe? Su dai Hausawa, suna ganin kansu }abila ne.
> To amma duk wanda ya tsaya ya bayyana ma'anar
> kabila sosai, sai ya ga Hausawa sun }i shiga.

Misali bisa bayanin marubuta, }abila al'umma ce mai asali ]aya, da harshe ]aya, da kamanni (watau }irar jiki) kusan iri ]aya, da al'adun gargajiya iri ]aya, da sauran irinsu. Kuma lallai ne cikin wannan al'umma kowa yana da'awar shi ]an }abilar ne.

To idan aka biya wannan bayani kuwa, sai a ga bai kamata a kira Hausawa da sunan }abila ba. Sai dai a ce su taro ne na }abilu daban-daban da suka cu]anya da juna, kuma suka taru suke magana da harshe ]aya. Domin ita kanta kalmar "Hausa" a wurin Bahaushe tana nufin "harshe" ne. Akan ji ya ce, "Ban ji wannan Hausar ba", watau bai gane wannan harshen ba ke nan. Ko kuma ya ce ya ji ana "wata Hausa", watau, ya ji ana magana da wani harshe. "Bugu da }ari, idan ka tambayi yawancin haifaffen }asar Hausa, ka nemi ya fa]a maka kabilarsa, sai yace maka, shi Bafillace ne, ko Babarbare, ko Buzu, ko Banupe, ko wata kabila daban. Gashi kuwa a wannan harshen bai san ko sannu ba. Kuma ana samun kabilun da ba su ji Hausa ba, amma su ri}a da'awar su Hausawa ne, misalin Abakwariga na Wukari da Takum da Lafiya".

**Tarihin Gbagyi**

Gbagyi mutane ne da suke }abila guda da asali ]aya da al'ada iri ]aya. Mafi yawansu na zaune ne a wasu sassa na Yammaci da Tsakiyar Arewacin Nijeriya a yau. Yawanci, Gbagyi masu matsakaicin tsayi ne, wato ba su cika tsawo ba kuma ba su cika gajarta ba. Yawancinsu ba}a}e ne, ka]an ne masu farin fata, suna da }arfi da juriya. Da can galibi matansu kan aske kawunansu, su sanya ba}a}en tufa, suna amfani da karan dawa a matsayin ]an-kunne, kuma sukan bar kawunansu babu kallabi, kamar maza da ke ]aura bante da rataya walki. Dattawa kan sa rigunan jamfa su rataya mayafi a kafa]unsu. Sarakuna kuma kan sa dogayen wanduna da babban riga da hular sa}i mai zubin

launin fari da baki. A lokutan bukukuwa, Sarakuna kan sa hula (jar-dara) da rawani, su ri}e sanda, su kuma sanya takalma (silifa). Sauran jama'a kan sa tufafi, maza da hula, mata su ]aura kallabi a kawunansu, al'ada ce kuma ga maza da mata su sha taba da lofe mai tsawon yadi guda.

Dangane da bambanci na kare-karen harshe za a fahimci cewa suna da bambance-bambance dangane da sunayen da suke kiran kansu. Gwarawa mazauna yammacin jihar Kaduna kan kira kansu da suna Gbagyi (Atsitai), su kuma da ke zaune a tsakiya da kuma Gabas maso Arewacin Nijeriya, na kiran kansu da suna Gbagyi (Atsyikokoi). Haka kuma wa]anda ke zaune a yankin masarautar Abuja suma sun rabu gida biyu, a gabas da Abuja akwai Gwari-genge, sannan a yammaci, akwai Gbagyi (Matayi). A }arshe a yamma da Minna akwai Gbagyi (Nkwa). Duk da wa]annan bambance-bambance na karin harshe, Gwarawa na fahimtar juna, wato in wannan ya yi magana, sauran za su fahimce shi. Misali; idan Gbagyi (Matayi) ya ce "Hala ifhe? Ma'ana 'Ina kwana', Gbagyi (Atsitai) da Gbagyi (Nkwa) za su fahimta. Wani misali kuma shi ne, Gbagyi (Matayi) na fa]in "haku ~he", Gbagyi (Nkwa) su ce "ha jhi ko "ha ~he", Gbagyi (Atsyikokoyi) ko Gbagyi (Atsitai) kuma na cewa "hala ~he" abin nufi a nan shi ne dukansu cewa suke yi sannu da zuwa.

A 'yan shekarun baya wato wajajen (1996), al'ummar Gbagyi da ke zaune a jihar Kaduna sun yi yun}urin sauya sunan su daga 'Gwari' (kamar yadda Hausawa da sauran }abilu ke kiransu) zuwa 'Gbagyi' a }ar}ashin wata }ungiya mai suna "{ungiyar Raya Al'ummar Gbagyi" wato (Gbagyi Development Union). Wakili, (2005:11), ya ce "}abilar Hausa na kiran Gbagyi da wannan suna ne saboda ba su da tushen kalma: (Gb) a harshensu kamar yadda yake akwai a harshen Gbagyi, sai dai (Gw)" haka ma ba su da 'gyi' sai 'ri'.

Dangane da asalin al'ummar Gbagyi kuwa, Meek, (1925:137) ya sa Gwari cikin harsunan da ke yammacin Sudan a }ar}ashin }abilar Nupe wanda ya }unshi: Bassa (Benue) da Ebe da Ganagana da Gupa da Gwari da Igbira da Jen da Jukun da Kakanda da Kona da Musu da Somboro da Wurbo da mabanbantan }abilar Koro.

Mamman (1983) ya ce:

> Al'ummar Gwari daga dangin harshen 'Kwa' suka fito, wanda ke }ar}ashin dangin al'ummar yammacin Sudan, reshen 'Kwa' ya }unshi Yarbawa da Igbo da Edo da Urhobo duk da suke a jihohin Kudancin Nijeriya, har wa yau akwai Idoma da Nupe da Bassa da Igbira da wasu }abilu na jihohin Arewa.

Shi kuwa Greenberg (1963:59), ya kira al'ummar Gwari da suna 'Gbagyi', ya kuma ce daga gidan harshen 'kwa' da ke }ar}ashin dangin al'ummar Kwara da Kwango suke.

Har wa yau, akwai tababa tsakanin Masana tarihi da Masana harshe dangane da asalin al'ummar Gbagyi.

Temple (1976:54) cewa ya yi:

> Yana iya yuwuwa }abilar Gwari sun samo asali ne daga Zamfara da kuma gundumomin da suka ha]a da gabashi zuwa kudancin sashen lardin Zariya. Kuma za a iya kwatanta addini da al'adansu da na }abilun Bassa da Kamuku da Kambari wa]anda suka zo daga tushe ]aya. Kuma su masu ]aukan kaya ne a kafa]unsu. (Wato ba sa ]aukan kaya a kawunansu, domin sun fi daraja kai da sauran sassan jikinsu).

Marubuta tarihi, kamar su Kirk Greene da Ryan (1975:34) sun ce:

> Bisa ga al'adar gargajiya ta baka ta Gwari, sun danganta asalinsu ne da mutanen Borno. Gwari suna da ra'ayin ri}au na cewa su Kanuri ko Bari-bari ne. Kuma a wani lokaci da can, da harshen Kanuri suke magana. Ko da yake a yau babu alamar wannan zance. Gbagyi sun }aura ne daga Barno a shekara dubu ]aya da ]ari shida wato 1600 A.D, suka dawo da zama a kan Dutsen

> Dala da ke jihar Kano a yau da wasu sassa na Katsina da Zazzau Kafin su zo su zauna a matsayin al'ummomi daban-daban kamar yadda suke a yau. Su masu magana da harshen kwa ne wanda a ilimin harshe ke da nasaba da harshen makwabtansu Nufawa.

Byanyiko (1979) da Baraje (1991) da Kirk-Greene da Ryan (1975) da wasu da dama sun yi da'awar cewa al'ummar Gbagyi asalinsu daga daular Kanen Barno na da ne da aka gina a jihar Barno na yanzu. Byanyiko (1979) da Baraje (1991) sun }ara da cewa: "Gbagyi sun yi wo }aura daga Barno a shekara ta dubu ]aya da ]ari shida wato (1600 A.D.) sanadiyar jhadin addini da aka kai saboda kafircewarsu".

Wa]annan masana sun cigaba da jayayya a kan cewa Gbagyi na da zanen gado iri ]aya da na Kanuri da halin zamantakewa da siyasa iri ]aya. Sun ruwaito kuma ruwaito cewa mutum na farko da ya kafa garin Kuta wato (Adamu Bwodwo) da ]an uwansa Kangoo Opana wanda ya kafa garin Bosso da Maikunkele a shekara ta dubu ]aya da ]ari shida wato (1600 A.D.) dukkansu Kanuri ne kuma sun yi hul]a ne da harshen Kanuri.

Mamman (1983) ya ce: Gwari na cikin harshen kwa wani ~angare a }ar}ashin iyalin Sudan ta yamma. Wanda ya }unshi; Yoruba da Igbo da Edo da Urhobo da ke kudancin Nijeriya da Idoma da Nupe da Bassa da Gwari da Ebira da wasu harasa na jihohin Arewa.

Armstrong (1986) ya bayyana cewa: Wa]annan ma}wabta na Gbagyi ban da Hausa, suna da dangantaka na Kakanni da Gbagyi. Sun rarrabu da juna ne tsawon shekaru dubu shida wato da suka wuce saboda wasu matsaloli.

Ana iya yarda da wannan bayani na Armstrong, saboda mabanbantan marubuta litattafan ta-rihi da na ilimin harsuna sun gunguta harsunan cikin iyali ]aya. Wa]annan harsuna suna zaune ne a }asa ]aya kuma suna da halin zamantakewa da al'adu iri ]aya. Suna kuma da ala}a na harshe. Wannan bincike ya gano cewa harsunan da suka fi kusa da kuma ala}a na harshe da Gbagyi su ne

Nupe da Gana-gana da Bassa – nge da Yoruba. Misali a }idaya: **innu** na nufin ]aya (1) da harshen Gbagyi, **inni** a Nupe, **gbani** a Gana-gana, **inni** a Bassa-nge, **eni** a harshen Yoruba. **Inta** na nufin uku (3) a harshen Gbagyi, **guta** a harshen Nupe, **guta** a Gana-gana, **guta** a Bassa-nge, **meta** a harshen Yoruba. **Anyi** na nufin hu]u (4) a harshen Gbagyi, **guni** a Nupe, **ayni** a Gana-gana, **guni** a Bassa-nge, **merin** a harshen Yoruba. Haka ma **Awo** na nufin (10) a harshen Gbagyi, **guwo** a Nupe, **ewo** a Gana-gana, **guwo** a Bassa-nge, **mewa** a Yoruba da sauransu.

Nakuta (1999) ya labarta cewa: Asalin al'ummar Gbagyi da ke masarautan Birnin Gwari ya faro ne daga kan wani masanin addinin Islama da ake kira Sharrif wanda ya yiwo }aura daga Katsina zuwa Kuta da ke cikin jihar Neja a yau. Masanin ya yi fa]a da arna, ya kori shugabanninsu, sannan ya kafa shugabanci bisa tafarkin addinin Islama a sansanin wajen shekara dubu ]aya da ]ari shida (1600 A.D.). A zamaninsa a Kuta, 'ya'yansa uku: Gwari da Gayan da Kaguru sun rabu da mahaifinsu, kowanne ya je ya kafa tunga da jama'arsa. Saboda haka bayan an sulhunta, Gwari ya kafa Birnin Gwari da ke cikin jihar Kaduna ta yau wanda ya zama mafarin zaman al'ummar Gwari da harshensu.

Busa (2000) ya lura cewa, da'awar masana dangantakar harsuna da na tarihi ya nuna cewa wasu harsuna da ke yankin tsakiyar Nijeriya kamar Nupe da Gade da Ebira da Kamuku da Tiv da kuma Yoruba da suka fito daga iyali ]aya na harshen Kwara da Kwango tare da Gbagyi, ba su yi da'awar cewa asalinsu daga Kanuri ba. Saboda haka, Gbagyi ma ba za a bar su a baya ba. Ma fi a'ala shi ne a furta cewa yankin tsakiyar }asar nan shi ne cibiyar Gbagyi. Al'ummar Gbagyi ba ma}aurata bane daga jihohin }asashen Hausa na tarayyar Nijeriya ko daga Barno kamar yadda masana ilmin dangantakar harsuna da masana tarihi ke da'awa ba. Ya jaddada cewa Gbagyi sun }aura ta shiyan Arewa ne suka shiga cikin jihohin da Hausawa ke zaune kamar: Katsina da Kano da Zazzau saboda cigaba da musgunawa da }abilar Ebira ke yi musu a yayin yun}urinsu na kamun bayi.

Ya }ara da cewa, yawanci matsugunin Gbagyi ba ya bun}asa da yawan jama'a saboda a duk lokacin da suke zaune a wuri, suka ga ba}i na tururuwa cikin mazauninsu sai su matsa gaba cikin jeji.

Dalilai da aka bayar na wannan canje-canje na mazauni sun ha]a da: Da yake sanannen sana'ar Gbagyi ita ce noma, sun gwammace su yi rayuwarsu cikin jeji inda za su samu isasshen filin noma da amfanin gona mai yawa.

Wasu sun ce Gbagyi sun gwammace zama cikin daji ne saboda kare kansu daga mahara ko abokan gaba, kuma dama can an san su da son zama lafiya, saboda haka ba su so suna hayaniya ko fa]a da ma}wabta ko ba}i. Wa]annan halaye nasu na canza wurin zama ya sa ba su da daular da za a iya kamantawa da na Hausawa da na Nufawa da Igbira da na Yoruba da kuma na Igbo.

Dangane da tarihi, bayanai marasa inganci sun danganta asalin Gbagyi da tarihin Daura inda Bayajida ko Abu-Yazid ya auri Bagwariya wanda ita ce ta haifi 'Munkar~i-gari' wanda shi ne asalin sarakunan }asashen Hausa banza bakwai ha]e da Birom.

Haka kuma Kirk-Greene da Ryan (1975:35) sun ce:

> Har wa yau, al'ummar Gwari sun ]auki kansu a cikin jerin Kawunnai da kuma abokan barkwancin al'ummar Daura. Bugu da }ari, ]aya daga cikin Sarakunan Daura da ya yi nasarar jagorancin adawa da Fulani a lokacin jihadi, an san shi ne da suna Sarkin Gwari Abdu saboda auren Bagwariya da ya yi. Cikin wannan siga na tarihin Daura, matsayin yankin }asar Gwari ya kasance ]aya daga cikin }asashen "Banza Bakwai.

Bayan rubutattun bayanai da aka samu a kan tarihi da asalin Gbagyi, akwai kuma bayanai na baka da dama. Salihu Sarkin Madalla (1969) a nasa bayanai, ya ce ya jiyo daga kakanninsa cewa Gbagyi suna tare da }abilar koro ne a Borno. A lokacin da Kanuri suka kore su ne, suka bazu cikin lardunan Kano da Zazzau.

A wani ra'ayi makamancin haka, Gwarin Genge da ke zaune mil goma sha takwas nesa da Abuja sun ce daga Kano su ke. Dalili kuwa shi ne wasu mutane biyu: Tayabete da Kumbayi tare da mata biyu sun taho yawon farauta a yankin masarautar Abuja a shekara ta dubu ]aya da ]ari bakwai da talatin (1730 AD.)

A wani hira (2008) da aka yi da Sarakunan Lokoto da Shakwata da Gawun - Babangida a jihar Neja, sun ce an ji daga kakan kakanninsu cewa asalinsu mutanen Zariya ne. Watakila wannan zance ba zai rasa dangantaka da wani ]ango a wa}ar Sarkin zazzau Shehu Idris ta shahararren mawa}in nan Marigayi Alhaji Mamman Shata ba, inda ya ce: 'An ce Zazzau mafarin Gwari, yanzu ko birnin Shehu'. Dalilin wannan kirari na mawa}in bai rasa nasaba da cewa lokacin da Kanuri suka kori Gbagyi daga Barno sun bazu ne suka yiwo }asar Zazzau suka kafa tunga wanda suka kira Zazzau, bayan ya}e-ya}en da Sarauniya Amina ta kai masu ne a ka ci su da ya}i sai mulki ya koma hannun Hausawa wanda shi ne asalin masarautar Zazzau na yanzu.

### 1.7 Dangantakar Hausawa da Gbagyi

Wa]annan al'ummu biyu wato Hausawa da Gbagyi sun da]e da ha]uwa, dalili kuwa shi ne ana }iyasin cewa Hausawa sun ha]u da Gbagyi ne tun kafin shigowar Turawa }asar Afirika. Akwai abubuwa da yawa da suka haddasa ha]uwar Hausawa da Gbagyi, wa]anda suka ha]a da: hijira da sana'o'i kamar; kasuwanci da farauta da fatauci. Bayan Haka, akwai dalilai na addini da auratayya da sau}in kai irin na Gbagyi da ya}e-ya}e da bayar da magunguna na gargajiya sun taimaka wajen samar da kyakkawar dangantaka tsakanin al'ummomin biyu.

Zai yi wuya a ce za a ]auki dukkan garuruwan Gbagyi a bayyana yadda suka ha]u da Hausawa ]aya bayan ]aya, a nan zai fi kyau idan aka mayar da hankali a kan manyan garuruwa ko fitattun garuruwan Gbagyi na asali wa]anda suka ha]a da: Minna da Kuta da Abuja (}asar Suleja) da Birnin Gwari. Kafin a yi wani bayani a kan yadda Hausawa suka ha]u da Gbagyi a wa]annan za~a~~un

garuruwa, yana da muhimmanci a yi ]an tsokaci a kan ya]uwar Hausawa da kuma abubuwan da suka haddasa bun}asarsu a }asar Gbagyi kamar haka:

Yin }aura da Hausawa suka yi daga garuruwansu zuwa garuruwan da ke makwabtaka da su musamman na Gbagyi, ya haifar da ya]uwa da bun}asar al'adunsu a wa]annan wurare. {aurar Hausawa zuwa }asashen makwabtansu da]a]]en abu ne. Bincike ya nuna cewa akwai dalilai da suka haddasa }aurar. Dalilan sun ha]a da rashin jituwa a tsakaninsu da almajiranci da ci-rani da wasu sana'o'i don neman abinci da dai sauransu. {aurar ta sa suka zauna a }asashen da ba nasu ba har da }asar Gbagyi suka yi auratayya da 'yan }asa suka hayayyafa. A halin da ake ciki a yau, wasu zuriyar Gbagyi sun zama Hausawa a sanadiyyar auratayya.

Da yake Hausawa na da sana'o'i da dama da suke yi, kuma wasu makwabtansu ba su san yadda ake aiwatarwa ba, ya tilasta hul]a tsakanin Hausawa da Gbagyi.

Sana'o'i irin su: kasuwanci da fatauci da }ira da rini da }ira da noma da dai sauransu sun taimaka wajen cu]anya da bun}asa al'adun Hausawa a }asashen Gbagyi. Kasuwanci da]a]]en sana'a ce a wajen Hausawa wanda ko shakka babu ya taimaka wajen cu]anya da mu'amalar Hausawa da }asashe makwabtansu musamman na Gbagyi.

Daba (1987) ya bayyana cewa, da farko Hausawa sun fara hul]ar kasuwanci ne tsakanin junansu. Wannan shi ne ya yi sanadiyyar kafuwar wasu garuruwa kamar Kano da Katsina da Gobir. A wancan lokacin, Hausawa sukan kai musu irin kayayyakin da suke da su kamar albasa da tumatiri da jitta da gya]a da wake da gero da sauransu, sannan su kuma su sayo wa]anda ba su da su kamar shinkafa da zanin sa}i da man-ka]e da sabulun salo da sauransu.

Hausawa sun kasance masu dabara a fannin kasuwanci, wanda ya sa a duk inda suka sami kansu, sukan yi yadda za a kar~e su hannu bibbiyu. Wato dabarar da Bahaushe kan yi idan ya je garin da ba nasa ba, yakan je ya gaishe da sarkin garin ko }auyen. Idan babu sarki, sai ya nemi mai-

unguwa. A cikin kayan kasuwancinsa, sai ya ke~e na sarki ko na mai-unguwa wanda na kyauta ne. Wannan alheri da sukan yi wa sarakuna, shi yakan haifar da kyakkyawar martabar da sarakuna ke ba Hausawa ‘yan kasuwa, idan zama ya yi zama, sai a ga an ba su sarauta ko malanta ko wani mu}ami a garin ko }auyen. Wannan dangantaka da suke }ullawa da jama’ar gari yakan ba su damar gudanar da kasuwancinsu ba tare da tsangwama ko fargaba ba. Bayan kuma sun sha}u da mutanen gari sai ka ji maganar aure wato sukan auri ‘yan }asa su hayayyafa har a kafa unguwan Hausawa. Idan bu}ata ta taso, sarkin gari ko }auyen kan na]a sarkin Hausawa don jin da]in zaman Hausawa da ke garin ko }auyen. Ta wannan hanya ne Hausawa suka ya]u suka bun}asa al’adunsu wanda ya ha]a da bori a wurare da dama har da }asar Gbagyi.

Binciken nan ya nuna cewa, akwai Hausawa masu ]imbin yawa da suka baro }asar Hausa zuwa wasu wa]ansu }asashe da ha]a da }asar Gbagyi domin neman abin da za su ci. Hausawa makamantansu kan tafi wasu }asashe su zauna musamman inda akwai kyawun noma. Wasunsu sun kasance masu sana’o’in hannu ne don su sami abinci. Wani abin da yasa Hausawa ke zuwa garuruwa makwabtansu shi ne don su sami kayayyakin aikinsu. [an’asabe (2005) ya ce bincikensa ya gano a wajen shekara dubu ]aya da ]ari bakwai das ha biyar (1715) an ce wa]ansu Hausawa ma}era sun bar wani gari da ake kira Likoro da ke }asar Zazzau zuwa }asar Abuja suka zauna a Wuse. Ba wani abu ya kai su ba sai don neman }arafan }ira. Haka ma Katsinawa da dama sun baro Katsina zuwa }asar Gbagyi ba don komai ba, sai don noma. A ta}aice tun }arni na goma sha biyar ne (}.15.) Hausawa suka fara tururuwa zuwa cikin }asashen makwabtansu don neman abinci. Bayan noma, sukan aiwatar da sana’o’i irin su tufkar igiya da yenta da gini da sa}ar zana da ]inkin hula da dai sauransu. Wannan hanya ta neman abinci ta haifar da cu]anya tsakanin Hausawa da wa]anda ba Hausawa ba musamman Gbagyi.

Ya}e-ya}e na ]aya daga cikin dalilan }aurar Hausawa suka koma zama a }asashen ma}wabta har da }asar Gbagyi. Tun da can a tarihin Hausawa, an san su da ya}e-ya}e. Dalilin da ya sa haka

kuwa shi ne don ta hanyar ya}i ne ka]ai ake gane jarumin sarki ko gari. Haka ya sa a kullum ana cikin ya}i ne daga gari zuwa gari ko daga }asa zuwa }asa.

Yadda tarihi ya nuna, Hausawa sun jima suna gudanar da ya}e-ya}e tsakaninsu da wasu }abilu kamar Gbagyi da Nufawa da Barebari da Jukunawa da sauransu. Wannan ya}e-ya}e ya taimaka wajen haifar da cu]anya tsakanin Hausawa da sauran kabilu musamman ma Ggagyi.

A dalilin ya}i, wasu Hausawa maya}a idan sun yi nasarar ya}i, sukan zauna ne a garin. Ire-iren wa]annan maya}a sun taimaka hai}an wajen ya]a al'adun Hausawa a tsakanin kabilun da suka ya}a.

Bayan ya}e-ya}e don nuna jaruntaka, an samu rashin jituwa ko sa~ani tsakanin al'ummomi biyu ko mutane biyu. Da can an fi samun rashin jituwa ne tsakanin sarakuna da 'ya'yansu. Dalilin wannan sa~ani da ya auku tsakanin Hausawa, shi ya haifar da cu]anyar Hausawa da wa]ansu }abilu ciki har da Gbagyi. A wani lokaci, sarakuna ne kan kori mutane idan sun yi laifi ko wani sa~ani ya faru tsakaninsu sais u koma wani gari na wasu }abilu su zauna har su yi aure su hayayyafa su kuma ya]a al'adun Hausawa. [an'asabe (2005:121-122) ya kawo misalai daga aikin Mahdi Adamu (1978) cewa daga 1623-1648 an yi wani sarki a Kano mai suna Ali Wali wanda aka fi sani da Muhammad Kutumbi wanda a lokacinsa ya umurci jama'arsa su musulunta sai suka }i, suka bar }asar Kano suka je }asar Zariya. A }asar Zariya sai suka je kudancin Zariya suka zauna wanda wani ~angarenta ke cikin jihar Filato ta yanzu. Suna zamansu sai wata rana aka kai musu hari daga Zazzau don haka suka tashi zuwa }asar Abuja da wa]ansu wurare. Haka ma Ru}ayya (1986) ta bayyana cewa sarki Kwasau ya baro Zariya ne saboda }in kar~ar sharru]an da Shehu Usmanu [anfodiyo, ya zo da jama'arsa ya kafa garinsa a Abuja (Suleja) har garin ya bun}asa.

A ta}aice, rashin jituwa shi ma ya haddasa ya]uwar al'adun Hausawa ciki har da bori a }asashe daban-daban har da }asar Gbagyi.

Hausawa sun shigo cikin }asashen Gbagyi ne bayan su Hausawan sun kar~i Musulunci Imani da Bori ya fara raunana, sun koma suna neman ilimin islama. Ibrahim (1982) ya nuna cewa Barebari sun riga Hausawa kar~ar addinin Musulunci. Don haka, da Musulunci ya zo }asar Hausa, Hausawa da dama sun tafi }asar Borno don neman ilimin addini. Haka kuma al'ummar da ke ma}wabtaka da }asar Hausa sun barbazu cikin }asar Hausa don neman ilmi wato almajiranci.

Bayan Hausawa maguzawa sun tuba sun daina bautar gumaka da Iskoki sun amshi addinin Musulumci, da kuma bayan jihadin mujaddadi Shehu Usmanu [anfodiyo, Firimiyan Arewa kuma Sardaunan Sakkwato Sir, Ahmadu Bello ya yi }o}arin ya]a addinin Musulunci a }asashen Gbagyi, a yayin tafiye-tafiyensa na ran-gadi ko ziyara a garuruwan Gbagyi kamar Kuta da yankin Minna da Abuja da Birnin-Gwari da sauransu, ya taho da Malaman addinin musulunci Hausawa, duk inda ya tarar ana tsafi ko bautar gumaka sai ya hana da taimakon sarakunan wa]annan garuruwa, ya zaunar da malamin addinin Musulunci Bahaushe a wannan guri domin ya karantar da al'ummar yadda ake addinin. Ta haka al'ummar Gbagyi suka koyi addini a wurin wa]annan malamai, yawancinsu suka daina tsafe-tsafe da bautar iskoki har wasunsu suka je neman ilmi a garuruwan Hausawa kamar Kano da Katsina da Zariya . Da zama ta yi zama, an samu auratayya tsakanin Hausawa da Gbagyi aka kuma hayayyafa wanda a yau idan aka ziyarci ire-iren wa]annan kasashe na Gbagyi, za a ga cewa al'adun Hausawa ya yi tasirin gaske a kan nasu.

Bayan shigowar addinin musulumci, Hausawa da dama sun musulumta, sun daina tsafi da bautar iskoki, amma wasunsu sun cigaba da aiwatar da bori a matsayin sana'a ko kuma harka ta gado da ba za su iya rabuwa da shi ba. To ire-iren wa]annan a yau a yayin yawoce-yawocensu na neman abinci da taimakon marasa lafiya da magani suka kawo sauye-sauye a yanayin tsafi da bautar iskoki na Gbagyi. Saboda da ma can ba duka al'ummar Gbagyi suka musulunta ba. Wannan cu]anya da 'yan borin Hausa suka yi a }asashen Gbagyi, ya }arfafa dangantakarsu da al'ummar Gbagyi.

Zai yi wuya a yi bayanin kafuwar mayan garuruwan Gbagyi ba a ambaci shigowar ba}i kamar Hausawa da wasu }abilu ba. Kuma kamar yadda aka riga aka fa]a a baya cewa abu ne mawuyaci a ce za a ]auki dukkan garuruwa da }auyukan Gbagyi ]aya bayan ]aya domin gano dangantakarsu da Hausawa. Dalilin haka ya sa aka iyakance binciken a garuruwan yankin Minna da Kuta da garin Suleja da ke jihar Neja a yau da kuma Birnin Tarayya Abuja da Birnin Gwari da ke jihar Kaduna.

**Garin Minna:** Abu ne mawuyaci a fa]i tarihin Minna ba a danganta shi da Kuta ba. Asali dai Minna gari ne na }abilar Gbagyi. Garin Minna a harshen Gbagyi aka samo sunan shi lokacin da mahara suka kawo hari }asar Gbagyi, da suka iso Minna, ba su iya cin garin da ya}i ba, sai masu garin suka kama kirari da harshen Gbagyi suna fa]in "~a mi nna", wato ina suka iya. Ta haka aka bai wa garin suna 'Minna'. A yau shi ne babban birnin jihar Neja. Kamar yadda Garba (1995) ya ce Minna gari ne da ya ha~aka a wajen shekara ta 1901 lokacin da aka fara gina hanyar jirgin }asa bayan zuwan Turawa. Wannan ya jawo kwararar jama'a cikin garin domin neman abinci. Hausawa na daga cikin al'ummar da suka fara zuwa Minna don fatauci da aiwatar da sana'o'i kamar }ira da fawa da malamta da wanzanci da dai sauransu. Wannan shi ya yi sanadiyyar kafa unguwanni ciki har da unguwar Limawa a Minna.

Sani (1991) ya bayyana cewa }abilar Gbagyi da ke Minna sun kasance suna zaune ne a tsauni. Bayan saukowarsu daga kan tsaunin sun kasance ne a wuri ]aya, wato sun }i su caku]e da ba}i, tun da har wayau suna da unguwanninsu da kasha casa'in na mazauna wurin asalinsu Gbagyi ne. Wa]annan unguwanni kuwa su ne Paida da Sayako da Ketaren Gwari. Tun can da ma Paida unguwar mashayarsu ne, nan suke taruwa sha giyarsu ta gargajiya da suke kira 'Eje', wato 'burkutu' a Hausance. Minna wanda ta zama babban Birnin Jihar Neja a shekarar 1976, ta da]e da kasancewa babban Birnin }abilar Gbagyi ko kuma hedikwatarsu. Tarihi ya nuna cewa tun daga 1901 zuwa 1950 Minna ta kasance jagoran masarautun }abilar Gbagyi goma sha bakwai. A wancan lokaci, Minna ta jagoranci masarautun Gbagyi wanda ya ha]a da Hakimai da Dagatai har guda

goma sha takwas (18) ciki har da garin Minna. Hakimai da Dagatan da suka kasance }ar}ashin sarautar Minna sun ha]a da; Kuta da Paiko da Galadiman-Kogo da Fuka da Gurmana da Manta da [angunu da Alawa da Bosso da Guni da Kafin-koro da Adunu da Gawu da Minna kanta. Sarkin Kuta shi ne kan gaba a dukkan wa]annan sarakuna guda goma sha takwas. Dalilin da ya sa Minna ta zama babban birnin Gwarawa shi ne don ta kasance a tsakiya kuma hanyar jirgin-}asa da ake ginawa wanda ya yi sanadiyyar kwararowar ba}i suka zo suka zauna a Minna. Wannan albarkaci na ba}i da kuma ha~~akar da garin Minna ke yi, ya sa Turawan mulki suka bu}aci Sarkin Kuta na wancan lokacin wato Sarki Umaru ya dawo Minna da zama. Da Sarki Umaru ya ga ba zai iya barin garinsa na Kuta ba, sai ya umurci ]ansa wato Marigayi Ahmadu Bahago da ya je ya wakilce shi, wato ya zama Sarkin Minna. An na]a Marigayi Ahmadu Bahago Sarkin Minna a ranar sha ]aya ga watan Oktoba na shekara dubu ]aya da ]ari tara da hamsin (11/10/1950).

Daga wannan rana da aka na]a shi Sarkin Minna ya zama shugaban Sarakunan }asar Gbagyi guda goma sha bakwai ciki har da Kuta inda iyaye da kakanninsa suka yi mulki. A shekara ta 1962 aka ]aga masarautar Minna zuwa mai daraja ta uku. A wannan shekarar ta 1962 ne kuma aka kara masa na]in a sarkin Minna da Kuta. Haka masarautar Minna ta yi ta ci gaba hart a kai lokacin da aka sake mata tsari, inda aka raba masarautar bisa yanki-yanki kowanne da Hakiminsa kamar haka:

(i) Yankin Kuta – Ya }unshi garuruwan Kuta da [angunu da Fuka da Guni da Gini. Hakiminsu na zaune a garin Kuta.

(ii) Yankin Paiko – Yankin ya }unshi }auyukan da ke }ar}ashin Paiko da Gawu. Hakiminsu na zaune a Paiko.

(iii) Yankin Galadiman – Kogo, wannan ya }unshi }auyukan da ke }ar}ashin Allawa da Kushaka da Gussoro. Hakiminsu na zaune a Galadiman – Kogo.

(iv) Yankin Minna – Wannan ya ha]a da garin Minna da }auyukan da ke }ar}ashin Bosso da Maikunkele da Manta.

(v) Yankin Kafin – koro – Wannan shi ya }unshi Kafin – koro, da Ishau da Adunu.

{ir}iro }ananan hukumomi da gwamnatoci suka yi, ya sa a yau wasu yankunan sun fa]a a wata masarautar. Misali Gawu ba ta }ar}ashin Masarautar Minna a yau ta koma masarautar Suleja.

Garin Minna ya }ara bun}asa ne a shekarar ta dubu ]aya da ]ari tara da saba'in da shida (1976) lokacin da gwamnatin soja ta wancan lokacin ta }ir}iro sababbin jihohi inda aka ba Minna B.abban Birnin Jihar Neja. A dalilin haka kuma sai garin ya }ara armashi, ba}i masu shigowa neman abinci musamman ma Hausawa suka yi yawa wa]ansu sun gina gidajen kansu, sun yi auratayya da 'yan }asa sun kuma zama 'yan gari.

**Garin Kuta:** Wannan gari ya yi fice ba a jihar Neja ka]ai ba, har duka fa]in }asar nan Nijeriya. Sunan da Gbagyin Kuta suka laka~a wa garin shi ne 'Okoh', ]an asalin garin kuma ana kiransa 'Okoizah' wato ']an ko mutumin Kuta'. Garin Kuta ya samo sunansa ne daga dutse wato 'Kuta' da harshen Gbagyi na nufin dutse. Dalili kuwa shi ne ainihin mutanen farko da suka kafa garin, a kan tsauni suka zauna saboda kare kansu daga mahara, daga baya ne suka sauko }asa inda ake zaune a yau.

Wani masanin tarihi wato Galadima (1982) ya bayyana cewa Kuta gari ne na }abilar Gbagyi wanda kashi casa'in da biyar (95%) na mazauna cikinta Gbagyi ne. Sauran }abilu ba su fi kashi biyar ba. Kuta dai bisa tarihi, da]a]]en gari ne da ya yi fice, domin akwai lokacin da dukkan Gbagyin }asar nan sun ta~a kasancewa a }ar}ashin Masarautar Kuta, wannan dalili ma ya sa da Turawan mulki suka zo, sai suka mayar da Kuta Babban Birnin Gbagyi baki ]aya. A yau Kuta ne hedikwata ko kuma babban birnin {aramar Hukumar Shiroro ta Jihar Neja.

Galadima (1982) ya gabatar da wata mu}ala inda ya yi tsokaci a kan tarihin kafuwar garin Kuta. Ya ce tun kafin jihadin }arni na goma sha tara (19th century) Kuta ta kasance a tsare dangane da tafiyar da mulki. Saboda ta kasance tana da sarakunanta Gwarawa. Masana da yawa na danganta tarihin kafuwar garin Kuta da wani da ake kira 'Adamu Bodo' mutumin da ya fito daga }asar Borno wanda a }iyasce daga lokacin da ya zo zuwa yau ya fi shekara dubu ]aya. Wannan suna 'Bodo' Gwarawan Kuta na wannan lokaci suka laka~a masa, wanda yake nufin 'ru~a~~e'. Wato shi Adamu ya shigo Kuta ne a matsayin mafarauci, ba a rasa nama a gidansa har da ru~a~~e. To shi ne idan za a je gidansa sayen nama sai a ce 'bhe ya lo Adamu abu-bhodo da yhi' wato abin nufi 'zo mu tafi gidan Adamu mai ru~a~~en nama'. Kafin zuwan Adamu Bodo, mutanen Kuta na zaune ne a kan tsauni tare da sarakunansu na kowane unguwa, ba su da sarki takamaimai na baki ]aya. Misali: "Sa Kubwatu" wato sarkin Kubwatu da "Sa Gutoko" wato sarkin Gutoko. Su kuma kalmomin "Kubwatu" da "Gutoko" sunayen duwatsu ne a harshen Gbagyi.

Da yake Adamu Bodo mafarauci ne, kuma jama'a sun saba sayen nama a gurinsa, ga shi kuma sun lura cewa mutum ne mai ilimi na zamantakewa da hikimar rayuwa, sai suka amince da shi. Galadima (1982) ya jaddada cewa: "Ganin cewa Adamu Bodo yana da ilimi, ga shi kuma yana da dangantaka da }asar Hausa, sai sarakunan unguwanni suka taru suka yi shawara, suka amince su umurce shi ya shugabance su a matsayin sarki. Da ma Adamu Bodo ya taho ne da matarsa mai suna 'Bakuta'. da jama'arsa.

Da zama ta yi zama, sai aka fara samun auratayya tsakanin jama'ar Adamu Bodo da al'ummar Gbagyi da ke zaune a tsauni, al'adun Gbagyi kuma ya fara samun sauyi. Misali kayan ki]an Gbagyi da ake kira 'Kabulu' ya samo asali ne daga kayan ki]an Hausawa mai suna 'Garaya' da suka gani a wurin jama'ar Adamu Bodo. Galadima (1982) ya ce "Kabulu kayan ki]a ne da ba a danganta shi da kowace }abila in banda Gbagyi. Saboda shaharar wannan ki]an Gbagyi mai suna 'Kabulu', 'yan wasan sun ta~a wakiltar }asar nan Nijeriya a wani bukin gargajiya na }asashen Afirika da aka gudanar a }asar Aljeriya a shekara ta dubu ]aya da ]ari tara da sittin da tara (1969)

wato (All Africa Cultural Festival held in Aljers). Haka ma domin karramawa, an ta~a buga hotonsu a kan kan-sarki na aikewa da wasi}u.

Bayan Adamu Bodo ya rasu a matsayin Sarkin kuta, ]ansa ya haye karagar mulki, tun daga kansa, abin ya ci gaba har zuwa kan jikokinsa. Kafin jihadin Shehu Usmanu [anfodiyo. Sarkin da ya fi fice a }asar Gbagyi ga baki ]aya shi ne Sarki Abubakar wanda aka fi sani da "Dada Pinada". Galadima (1982) ya bayyana cewa a zamanin "Dada Pinada" ne garuruwa da }auyuka da yawa suka kasance a }ar}ashin mulkin Kuta. Daga cikin garuruwan da ke kai caffa a wannan lokaci sun ha]a da: Bosso da Alawa da Fuka da Galadiman-kogo da [angunu (Sarkin Pawa) da Guni da Kurmin-gurmana da Maikunkele da Paiko. A zamanin Sarki Abubakar ne ya sake na]a Hakimai duk da cewa kowanne na cin gashin kansa. Bayan wannan sarki, sarakuna kamar "Dada Gbangomin da "Dada Mangola", sun ci gaba da fa]a]a }asar Kuta.

A duk tsawon zamanin da wa]annan sarakuna ke mulki, }asar Kuta ta kasance a }ar}ashin mulkin Ha~e, wato }asar Zazzau. Tarihi ya nuna cewa can sukan kai harajinsu da kuma gaisuwar sallah. Wannan ma ya sa a lokacin jihadi da aka ya}i Zagi-zagi wasu suka koma }asar Abuja, wato Suleja a yau, }asar Kuta ta ci gaba da kai gaisuwar sallah da harajinta Abuja. A ta}aice, wannan dangantaka da ta wanzu tsakanin Masarautar Kuta da ta Zazzau ta taimaka sosai wajen }ulla zumunci tsakanin Gbagyi da Hausawa.

A }arshen }arni na sha tara (}.19) an yi wasu Sarakuna biyu wato "Dada Fugabe" da "Dada Usman [angunu da suka sake tsarin masarautar domin sau}a}a gudanar da mulki, inda suka na]a mutane bakwai a mu}amai daban-daban don su taya su tafiyar da mulki. Mu}aman su ne:

i. Madaki

ii. Galadima

iii. Wambai

iv. Dami-Dami

v. Makama

vi. Sarkin-Fada

vii. [angaladima

A duk wannan lokacin mutanen Kuta na zaune ne a kan tsauni. A shekara ta dubu ]aya da ]ari tara da talatin da uku (1933) Sarkin wannan lokaci Dada Ibrahim da jama'arsa suka bar kan tsauni suka sauko }asa a inda Kuta take a yanzu. Galadima (1982).

Bayan unguwanni na Gbagyi kamar: Godna da Zhenuwhi da Guto da Iddah da Kobwatu da Tawali da Kamfanin-[anjuma da 'Agbadaphe' wanda ake kira unguwar sarki a yau, akwai Unguwar Zogale da Limanci da Sabon-Gari inda galibi mazauna unguwannin ba}i ne kuma Hausawa har ma da sarkinsu. Ko da yake a yau a sanadiyyar auratayya an caku]e an zama ]aya.

**Garin Suleja (Abuja na da):** Suleja wanda kafin shekara ta alif ]ari tara da saba'in da shida (1976) aka sani da suna Abuja, gari ne da ya kasance a kudu maso yammacin yankin }asar Zazzau ko Zariya. Ba kamar Kuta da Minna da mazaunansu Gbagyi ne zalla ba kafin shigowan ba}i, Sueja ta }unshi ba}i na }abilu da dama. Wa]annan }abilu sun ha]a da Gbagyi wanda galibi sune a }asar Suleja, sai Gwandara da Bassa da }abilar Koro da Gade da Ganagana. Gbagyi da Koro tasu ta fi zuwa ]aya wato suna abota da juna duk inda suke zaune a }asar Suleja a gansu tare. Tarihi ya nuna cewa kafin zuwan Hausawa }asar Abuja, Koro (Kwarawa) su ne ke mulkin Gbagyi duk da cewa Gbagyi sun fi yawa. A yankin Bwari da ke Birnin Tarayya wanda da can garin na }ar}ashin Suleja ne, akwai wani }auye da ake kira Ija. A }auyen akwai ~angaren Gbagyi, akwai kuma na Koro. Wannan shi ya sa aka sami sarakuna biyu wato: Sarkin Ija Gwari da Sarkin Ija Koro. Wannan ya nuna cewa }asar Suleja ta Gbagyi ce duk da cewa akwai }ananan }abilu. Dalili kuwa shi ne idan aka lura, kusan kashi tamanin na garuruwan Birnin Tarayya da ya ha]a da: Kwali da

Kuje da Gwagwalada da Bwari da Rubochi da Dutse da Kubwa da Ija Deidei da Karu da Nyanya da {auyen Garki da dai sauransu, Gbagyi ne mazauna cikinsu.

Na'ibi (1969) da Haladu (1990) da Ru}ayya (1986) sun nuna cewa Hausawa sun shigo }asar Suleja (Abuja) ne a farkon }arni na goma sha tara (}.19). Dalilin zuwansu kuwa shi ne, wai an yi wani mutum mai suna Muhammadu Makau wanda ya yi sarautar }asar Zariya daidai gabatowar shekarar da Fulani suka kawo ya}i ga sarakunan }asar Hausa wanda shi ne sanadiyyar barinsa Zariya tare da mutanensa ya komo wani anguwa a cikin Abuja da ake kira Zu~a. "Zu~a" sunan wani dutse ne babba, mai alamar fuskar mutum a kusa da garin Suleja. A kan hanyarsa daga Zariya zuwa Zu~a, Sarki Makau ya biya wani gari da ake kira Kauru. Da yake maya}an Fulani na biye da shi, sai mutanen Kauru suka }i bu]e masa }ofar gari saboda haka sai suka je Kajuru. A Kajuru ne Sarki ya sa aka bu]e masa }ofa, anan kuma suka gwabza ya}i da Fulani. Daga Kajuru Makau ya yi }aura ya koma Zu~a. A Zu~a ne ya yi ta ya}i har ya sami nasara a kan mazauna wurin. Daga nan sai ya nufi Jiwa wanda ke cikin Birnin Tarayya a yanzu. Bai yi niyyar ya}an su ba, amma saboda }ananan maganganu da ya ji suna yi wai Fulani ne suka koro shi daga Zariya, sai ya ya}e su. Wannan ya}in ya so ya kawo sa~ani tsakanin Sarki Makau da mutanensa don ya ce bai yarda a mayar da wa]anda aka kama bayi ba. Daga jiwa sai ya juya akalar ya}insa zuwa }asar Lapai a shekara ta 1825. A wannan ya}i, an ja daga domin Sarki Makau bai sha ta da da]i ba, an ji ma abokin ya}insa Jarmai Musa ciwo, shi kuma nan ya gamu da ajalinsa.

Bayan an kashe Sarki Makau kuma Jarmai Musa ya ji rauni, sai Abuja wanda yake }ani ne ga Sarki Makau ya tara jama'arsa baki ]aya ya koma da su Izom inda Gwarin yamma suke zaune. A Izom ne aka na]a shi Sarki. Abuja ya yi mulki a Izom na tsawon shekara uku kafin ya yi tunanin kafa sabon birnin }asarsa wanda ya kasance nesa da }asar Lapai. A yayin da Madawaki Jama'arsa suka kakkafa unguwanninsu a gabashin tafkin da ake kira Wuciciri, Sarki Abuja da sauran Dagatai sai suka kafa nasu a yammacin tafkin. Duk hakan ya faru ne a }arni na goma sha tara (}.19), domin an ce a shekara ta 1823 ne Sarki Abuja ya gina ]akin farko da ake kira "Zauren Zazzau". Irin

wannan gini shi ne na farko da aka gina a garin Suleja (Abuja), daga shi kuma sai aka gina ganuwar garin a shekara ta 1830. Tun daga wannan lokaci ne Abuja wanda shi ne Suleja a yau ya kafu.

Kafin a }ir}iro sabon Birnin Tarayya kusan kashi tamanin da biyar (85%) na garuruwan Birnin Tarayya (Abuja) wa]anda yawanci mazaunansu na asali Gbagyi ne suna }ar}ashin }asar Suleja ne. Dalilin da ya sa ma ke nan da za a sa wa Birnin Tarayya suna sai aka sa sunan Abuja. Ita kuma Abuja ta ainihi ta koma Suleja. Sunayen guda biyu sun samo asali ne daga sunayen sarakuna na da. An samo "Abuja" daga "Abu" da yake shi jan mutum ne sai aka }ara "ja" ya zama "Abu-ja". Haka ma "Suleja" daga Suleman ne aka }ara "ja" ya zama "Suleja" a lokacin da Suleman Barau ke sarauta.

**Birnin Gwari:** Wannan gari Birnin Gwari, gari ne wanda asalinsa na Gwarawa. Ba kamar Kuta da Minna da Suleja da ke jihar Neja ba, Birnin Gwari yana cikin jihar Kaduna ne. Masana tarihi sun yi rubuce-rubuce a kan kafuwar garin da al'ummarta. Misali, Mahdi (1978) a cikin littafinsa, ya yi bayanai cewa kafin }arni na goma sha bakwai (}.17), Birnin-Gwari da ke makwabtaka da }asar Katsina da kuma Zazzau ta kasance }asa ce da Allah Ya yalwata ta da }asar noma mai albarka da kuma ]imbin namun daji wanda sune dalilan da suka haifar da zaman Gbagyi a garin. Hausawa su suka bai wa garin suna Birnin-Gwari don nuna cewa }abilar Gbagyi ne masu garin kuma mazauna cikinta.

Dangane da tarihi, al'ummar Gbagyi tun kafin 1800 A.D. suka fara zama a garin Birnin-Gwari bayan sun baro }asar Borno. {abilar Kamuku wanda tare suka yiwo hijira da Gbagyi, su suka kasance ma}wabtansu na kusa, sai dai su suna da unguwarsu da ake kira Bagoma wanda a halin yanzu ta ha]e da Birnin-Gwari. Amma tun farkon zaman Gbagyi a Birnin-Gwari har zuwa shekarar 1760, su ne ke mulkin garin.

Mahdi (1978) ya }ara bayyanawa cewa ba wani abu ya }ara ha~~aka garin na Birnin-Gwari ba, sai ha]uwarsu da ba}i musamman Hausawa. Tarihi ya nuna cewa wani Bakatsine da ake kira

Malam Sharif ne ya yi sanadiyyar cu]anyar Hausawa da Gbagyi mazauna garin, wanda da tafiya ta yi tafiya ]ansa ya zama Sarkin Birnin-Gwari.

Malam Sharif ya baro Katsina ne don yawon bayar da magunguna na gargajiya da asirai musamman na tsaro da jarunta. Malam Sharif ya yi suna sosai a }asar Gbagyi musamman a wajen Sarakuna wa]anda ya taimaka wa da asirai da magunguna. Bayan ya gama zagaye masarautar Gbagyi da ke Kuta da Alawa, sai shi da iyalinsa suka koma Birnin-Gwari da zama, kasancewar garin na iyaka ne da }asar Hausa musamman Zariya da Katsina. Da isar Malam Sharif Birnin-Gwari, Sarkin garin da jama'arsa wa]anda dukkansu Gwarawa ne sun kar~e shi hannu bibbiyu ha]e da tanadar masa da wurin zama. Da zama ta yi zama, aka zo aka na]a [an Malam Sharrif mai suna Waike sarkin Birnin-Gwari. Waike ya samu Sarautar garin ne da goyon bayan Gwarawan garin ba don komai ba, sai don hangen irin rawar da mahaifinsa ya taka dangane da tsaron gari. Na]a Waike Sarkin Birnin-Gwari ke da wuya sai ya fara kai hari a garuruwa da }auyukan Gwarawa  har ya yi nasara a kan su suka amince su zama }ar}ashin masarautarsa. Masana tarihi sun bayyana cewa wannan shi ne farkon mulkin Hausawa a }asar Gbagyi wanda ake zato ya faru ne tun wajen shekara 1760.

Kasancewar Sarki Waike Bahaushe kuma mutumin Katsina, ya taimaka masa wajen samun goyon baya daga masarautar Katsina. Kuma wannan ya ba Hausawa damar zama a garin tare da }abilar Gbagyi. Mahdi (1978) ya nuna cewa wani abu ya }ara bun}asa Birnin-gwari wanda kuma ya haifar da shigowar Hausawa a garin shi ne matsalar da masarautar Yawuri ta samu a farkon }arni na goma sha tara (}.19) wanda ya sa fatake suka daina bi ta Yawuri a kan hanyarsu ta zuwa Gwanja, maimakon haka sai fatake da 'yan kasuwa suka mayar da Birnin-Gwari zangonsu idan suka fito daga }asar Hausa za su Gwanja.

Ha]uwar Gbagyi da Hausawa ba}i ya haifar da bun}asar garin wanda a yau Birnin-Gwari na ]aya daga cikin manyan garuruwan jihar Kaduna kuma tana da Sarki mai daraja ta ]aya wato (Alhaji Zubairu Jibrin Mai Gwari).

### 1.8 Borin Hausawa

Samuwar Iskoki wani imani ne da kowace al'ada ta mutanen duniya ta yi imani da shi. Imanin mutanen duniya game da Iskoki abu ]aya ne ta fuskar kasancewarsu ~oyayyi, buwayayyi, masu ban tsoro, masu karkatar da mutane, kuma masu }arfi a kan mutane. Bunza (2006:1). Cikin hanyoyin addinin gargajiya na Hausa akwai "bori", wato bautar Iskoki. Bori da]a]]iyar al'ada ce a wurin Hausawa. Sun fara ta ne tun duka suna Maguzawa har zuwa yanzu da

kusan dukkansu Musulmi ne ba su daina ba. Hausawa sun ]auka ban da ma mutane, duniya tana

cike da wasu ~oyayyun halittu masu ]abi'a irin ta mutane. Domin haka ma suke kiransu "Mutanen

~oye", a bayan shigowar addinin Musulunci aka kira su aljannu, bayan: Alkur'an (sura :72, aya:1

-16), amma babban sunansu shi ne Iskoki. A cewar Hausawa; mu mutane ba ma ganin Iskoki, amma su suna ganin mu. Haka kuma su iskoki siffarsu ba guda ]aya ce kamar tamu ba, sukan riki]a su fito a siffar dabbobi ko macizai ko su zama Iska kawai kamar goguwa da dai sauransu. Allah ya ba su wata daraja a kan mutane, suna iya taimakonsu, suna iya cutarsu, suna ma iya kashe su.

An ce Iskoki suna da yawa, sun fi mutane yawa, domin wai su kullum haihuwarsu ake, amma ba sa mutuwa. Iskoki suna warwatse ko'ina cikin duniya, amma sun fi zama a gidajen tururuwa, da kan duwatsu, da kan tsamiya, da }ogon kuka, ko cikin shuri. Kasancewa Iskoki na warwatse ko'ina cikin duniya, suna da babban birni da ake kira Birnin Jangare. A cikin birnin akwai Sarki da Waziri, da Madaki, da [an Galadima, da sauran sarautun gargajiya na Hausa.

Iskokin sun kasu kashi biyu; akwai farare, akwai ba}a}e. Fararen su ne masu kirki, masu taimakon mutane. Suna bayar da dukiya, da sarauta, sa'annan suna bayar da maganin cuce-cuce.

Ba}a}en kuwa su ne ma}etata masu neman mutum da sharri, wa]anda ba sa taimakon mutane sai dai a kan sharri, kamar a yi wa wani magani ya mutu ko ya haukace ko kuma ya lalace.

Daga cikin irin wa]annan Iskoki akwai masu zama tare da mutane, su yi abota da su, su dinga hawa kansu suna gaya masu magungunan wasu cuce-cuce, suna kuma gaya musu labarin gaibi. Wa]annan mutane su ake kira 'yan bori. Kenan idan wasu suna neman wata bu}ata a wurin Iskoki sai sun biyo ta kan su wa]annan mutanen.

Da yawa mutanen da kan zama 'yan bori, sukan gaji Iskokin ne daga wurin iyayensu ko wasu danginsu. Misali idan wani ]an bori ya mutu, an ce Iskokin da ke kansa kan koma kan wani ko wata daga cikin danginsa.

Mutun kan zama ]an bori kuma ba tare da ya gaji borin ba, sai idan wata Iska ta yi sha'awar zama tare da shi sai ta zo ta hau kansa. A hanyoyin nan biyu, kafin mutum ya zama ]an bori sai an yi masa girka. Wato a sami wani ]an bori ya zaunar da iskokin nan daidai a kan mai son ya zama ]an bori.

Tun da da]ewa, yawanci, Hausawa musamman mata da yara sun ]auka Iskoki sun fi yawa a duniya. Kafin zuwan addinin Musulumci, Hausawa sun ]auka kowane mutum yana da wata Iska tare da shi, ko da ba ta mayar da shi ya zama ]an bori ba, duk da haka suna tare. Ban gaskiya ga haka shi ya sa idan Bahaushe yana zaune ba ya son wani ya zo ya tsaya a kansa. Wai idan ya da]e a tsaye sai Iskokin da suke kansa su tashi. Kuma wannan shi ya sa idan mutum biyu suna yawan fa]a da juna akan ce iskokinsu ne ba sa ha]uwa wuri ]aya.

Yawan Iskokin da suke da shi a duniya ba dukkansu ne ke hawa kan mutane a hau borinsu ba. Misalin Iskoki ]ari da hamsin ne kawai ake hawa borinsu. Daga cikin su akwai masu sunaye da

]abi'u irin na mutane, kamar su; Sarkin Maka]a [anfau, da Sarkin Aljan, da [an Galadima, da Uban Dawaki, da Sarkin Rafi, da Malam Alhaji, da Bagobiri, da Bagwariya, da Bature, da Ba'auzini, da Inna Bafillatana, da sauransu. Akwai kuma masu siffa da halaye irin na dabbobi kamar su Kure, da Ba}o, da Dorina, da Giwa, da Damisa; akwai kuma masu kamar macizai kamar; Uwar gona, da Gajimare, da Duna, da Danko da sauransu. Sai kuma masu halaye da ]abi'un tsuntsaye kamar su Hankaka, da Mikiya da sauransu.(Ibrahim,1982) da (Yahaya da wasu,1992).

Bayan zuwan addinin Musulumci, galibi Hausawa sun musulumta sun daina bautar gumaka da Iskoki kamar yadda yake da a zamanin Maguzanci. Wato sun sami wa]ansu hanyoyin Ibada wa]anda addinin Musulumci yake koyar wa. Irin wa]annan hanyoyin bauta sun bambanta da irin nasu na maguzanci. Domin kuwa su wa]annan suna da tsari, kuma daga cikinsu akwai na kullum-kullum, akwai kuma na shekara-shekara. Wa]annan hanyoyin bauta su ne; Na farko Imani, sai Salla, da Zakka, da Azumi, da aikin Hajji. A yau wa]annan hanyoyin ibada sun zauna daram da gindin zamansu a cikin al'adun Hausawa.

Duk da cewa Hausawa sun rungumi addinin Musulumci, har wa yau akwai wasu daga cikinsu da basu daina yin bori ba, sun ]auki harkar bori tamkar sana'a, wato hanya ce ta neman abinci. Wasun su kuma sun ]auka abu ne na gado da ba za su iya rabuwa da shi ba saboda muhimmancinsa ta wajen bayar da magunguna da warkar da cuce-cuce da ba su da ala}a da asibiti.

Bunza (1989:31) ya ce:

> *"A ganina, Kalmar (bori) ba za ta rasa ala}a da kalmar "bore" ba. Watau, idan ana dafa abinci a tukunya, idan an rufe tukunyar da faifai, da zarar ta tafasa, za ka ga wani kumfa na tasowa yana bugun faifan ko abin da aka rufe tukunyar da shi. Idan ba a yi gaggawa aka bu]e ba yana iya kashe wutar. To! da zarar, tukunya ta yi haka sai a ce "ta yi bori".*

Ya ci gaba da bayani cewa watakila kwatanta irin za~ar~akar da kumfa da boren da tukunyar ke yi ne ake danganta shi da irin halayyar ]an bori idan ya hau bori. Domin da ya hau bori, za ka ga kumfa na fita a baki, idanu na zazzarowa yana fizge-fizge da mi}e-mi}e.

Masanin ya ce Bori dai da]a]]iyar al'ada ce ba ga Hausawa kawai ba, sai kuma ya kawo ra'yoyin masana da yawa a kan yun}urinsu na fassara ma'anar bori. Misali, Mr. Fremout, E. Besmer ya ce:

*"Bori dai bauta wa Iskoki ne tamkar yadda musulmi ke*
*Bauta wa Allah domin samun wasu fa'idoji".*

A ra'ayin Besmer, wato Bori addini ne na musamman. Duk wani ]an bori, bori ne addininsa. Amma shi Malam Hassan Abdullahi Jaba, cewa ya yi:

*"Bori bauta wa wasu Iskoki ne, wa]anda aka ce suna ganinmu*
*amma mu 'yan Adam ba ma ganin su, idan ba sun bu]e mana ido ba".*

A fahimtar Abdullahi, cewa ya yi bori nau'in bauta ne, kuma Iskokin bori ana iya ganinsu idan sun so mai bori ya gan su. Muhammad Balarabe Umar, ya nuna ma'anar bori ta zarce haka, shi cewa ya yi:

*"Bori na ]aya daga cikin hanyoyin Bauta wa Ubangiji da mabiyansa kan bi ta kan Iskoki watau aljannu don yin bautar. Masu bin addinin bori sun yarda akwai wani abin bauta wa babba, mai, komai mai kowa wanda kowa ke tsoro, kuma ba a ganin shi kuma ba a iya zuwa a yi magana da shi kai tsaye sai dai ta hanyar Iskoki".*

Dangane da wannan batu na bisa, da alamar cewa 'yan bori dai sun san da akwai Allah, amma ba su san yadda yake ba saboda ba su ganinsa kuma ba su da ilmin yadda za a bauta masa. Don haka ne ma sai suke bautar iskoki maimakon su bauta wa Allah (S.W.T.) kai tsaye.

Bunza (2006) ya bayyana cewa a idon manazarta, akwai ire-iren bori da yawa da ke gudana a }asar Hausa idan aka lura da yadda ake aiwatar da shi da dalilin aiwatar da shi. Ga kashe-kashen Borin kamar yadda masu Bori, da manazarta Bori, suka hange shi:

i. Borin Fage.
ii. Borin Magani.
iii. Borin Giri.
iv. Borin Girka

**Borin Fage:** Wannan wasa ne na Bori da ake shiryawa domin }awata wani muhimmin biki. An kira shi Borin fage ne domin an fi yin sa a fage kamar dandalin kasuwa, ko unguwa, ko a daji. A kan yi irin wannan Borin wajen na]in sarautun }asar Hausa, ko ]aurin aure, ko bikin suna, ko wani abu makamancin su. Kamin ranar biki akan sanar da ]an Bori ranar biki ta aika masa goro domin ya shirya. Irin wannan Bori na nuna hikima ne, da }arfin jiki, da dabara, da buwayar Iskokin ]an Bori, da neman suna, da fice a fagen sana'ar Bori. A lokacin wannan biki, an ce yawancin 'yan Bori a kan yi musu asiri domin kunyata su a fage, su kasa gwada kwarewarsu a fagen wasa.

**Borin Magani:** Kafin shigowar addinin Musulunci 'yan Bori na daga cikin wa]anda ake neman taimakonsu na ba da sa'a, da wasu nau'uka na magungunan tsaron kai da kaya. Haka ma a sha'anin sarautu 'ya'yan sarauta na amfani da 'yan Bori, idan ta fa]i a ba su. Ga wani misali a jawabin Malamin wa}a Ibrahim Maidangwale Tubali (Naramba]a), inda ya ce:

*"Wani ya kunna ya ga ba wuri,*
*'yan Bori sun kai shi sun baro,*
*Saruru ya battala abinai,*
*Ya koma bi]at kwabon hwura".*
(Gindin wa}a: Ibrahim na Guraguri)

Wani misali kuma shi ne na ha]uwar Alhaji Gambu Fagada da Sarkin Barayi da aka so Sarki ya je ya gama da Tsoho Tudu (buwayayyen attajiri) sai Sarkin ~arayi ya ce wa Gambo, lokacin da ya so ya bi Tsoho Tudu, ya yi masa sata, sai da ya je wajen 'yan Bori suka ba shi sa'a, yana cewa;

*“An yi Bori, an yi Bori!*
*Na yanke awakina da kaji*
*An ce sa’a ta samu babba”.*

Wa]annan ]iyan wa}a sun tabbata mana cewa, akwai Borin magani wanda ake yi musamman domin neman waraka ga wani, ko neman wata sa’a, ta samun wani amfani, ko tunku]e wata cuta.

**Borin Giri:** A Hausa sunayen }arya fitattu guda biyu ne, akwai }arya, akwai ‘giri’. Borin giri shi ne, Borin da ake hawa domin a fyace koma/koma sosai, a fa]i wani abu da ke damuwar rai a ji. Idan ana }untata wa mace a gida cikin kishiyoyi, takan hau Borin giri, ta bayyana ba}in cikinta, ta nuna abin da ake yi mata ya isa. Idan uwar miji ce ke yi ko uba, takan fa]i sunansu }arara wato a fili domin da ma cikin Bori take, ta nuna in ba a daina ba za ta ]auki mataki. Haka kuma idan an yi sata a cikin gida, mace ta ga ~arawon ta san shi, ba za ta fa]i sunansa ba sai cikin Bori, sai a ce Iskokinta ne suka fa]a ba ita ba.

Haka shi ma Marigayi Alhaji Mamman Shata ya tabbatar da akwai Borin giri inda ya ce a wa}arsa ta Sarkin Bori Sule;

*“Akwai mu da Borin }warai,*
*Akwai mu da Borin giri”.*

Alhaji Umaru Nasarawa Wazirin Gwandu ma ya ambaci Borin giri a wa}arsa ta yabon Sarkin Gwandu Yahaya yana cewa;

*“Giri ko sunanka yaj jiya,*
*Shi tsoro bai barin idonai kwana”.*
(Sa maza gudu)

**Borin Girka:** Duk cikin ire-iren Borin Hausa, Borin Girka shi ne babba. Ba a yin sa sai wurin da ake Girka. Ma’anar Girka kuwa shi ne, zaunar da Iskoki a kan dokinsu su sami fahimtar juna. Kalmar Girka an samo tushensa ne daga tushen “gir” wanda za a iya sarrafa ta zuwa kalmomi irin su: ‘girki’, ‘girke’, ‘girkewa’, ‘Girkakke’. Kamar yadda ake girke randa a wurin da ake ajiye ta

a sha ruwa, ko tulu a wurin da aka yi masa gurbi, haka ake girke Iskoki a kan dokinsu su zauna babu wata hayaniya, ba cuta, ba cutarwa. (Domin cikakken bayani a kan Girka, a dubi babi na hu]u na wannan kundin).

**1.9 Borin Gbagyi**

Kafin shigowar addinin Musulunci da Kiristanci, al'ummar Gbagyi ba su da wani abin bauta na gargajiya da ya wuce tsafi har da bautar Iskoki duk da yake sun yarda akwai Allah mahallici da suke kira 'Shekwo' ko 'Shekwoi'. Kamar Hausawa, suma Gbagyi sun bayar da gaskiya da Iskoki (Aljannu) wannan yasa ma sukan garga]i 'ya'yansu da kada su yi wasa ko su je wasu wurare kamar rafuka da dazuka da wasu itatuwa da tsaunuka da sauransu, saboda irin wa]annan wurare ne Aljannu ko Iskoki ke zama. Gbagyi na kiran Bori "Boghyi", wanda ke da Bori kuma su ce masa "Boghyida". Borin na Gbagyi na asali ya kasu kashi uku; akwai "Gbemu", akwai "Madawa", sai kuma 'Gbunu', kowanne da irin Iskar da ke hawa dokinsu. Musa Shagbah (2011) ya bayyana cewa; Wannan suna 'Bori' kamar yadda Hausawa suke kira, al'ummar Gbagyi tun asali suna da wannan Kalmar da suke cewa "Boghyi" da harshen Gbagyi wato idan an ga mutum yana yin tawaye ko tayar da hankali sai a ce masa "wala gu Boghyi" wato ya hau Bori. A nan sai mu dubi bayanin ire-iren Borin Gbagyin ]aya bayan ]aya.

**'Gbemu'**: Wannan wani irin nau'i ne na Borin Gbagyi wanda a tarihin samuwar Iska shi ne na farko. Koda yake a yau wannan nau'i na bori bai da tasiri domin kusan a ce masu yin sa duk sun daina ko kuma sun mutu. A yadda aka samu bayanin aiwatar da shi cewa aka yi galibi mata aka fi saninsu da yi, domin su Iskan ya fi hawa. Amina (2013) ta ce: Idan Iskar Gbemu ya taso wa mace, sai a ga ta yi shiru na lokaci mai tsawo, tana mazurai wato zazzare idanu, tana kalle-kalle ba tare da ta yi magana da kowa ba. Da zarar haka ya faru, sai a kai ta a saka a wani ke~a~~en ]aki na kewaye mai jinkar ciyawa da hujin rami ta }asa inda ruwa zai fita irin na gargajiyar Gbagyi, ta wannan ramin wata macijiya za ta shigo ]akin ta zauna da matan a ]akin har na tsawon kwanakin da za ta yi

ba tare da ta yi mata wani illa ba ko kuma an yi wa macijiyar ba, sannan a girke tukunya mai ji}on magani da za a ri}a ]iba ana ba ta tana sha har na tsawon kwana bakwai babu kwalliya sai dai zani ]aya da za ta ]aura, babu fita waje, babu cin abinci sai dai wannan ji}on maganin. Idan fitsari ya kama ta, ta wannan hujin rami da ke ]akin za ta yi, idan kuma bayan gida ne, sai dai ta yi a wani }o}o a je a zubar.

Amina (2013) ta ce: A lokacin da mai 'Gbemu' ke cikin ]akin, babu wani wanda zai shiga sai dai mace guda da aka ]aura wa alhakin kulawa da ita, ita ke ji}a mata magani a tukunya , ita za ta ]iba mata maganin ta sha, da ]awainiyar zubar da kashi. A rana na bakwai da za ta fita akan yi wata al'ada, kamar yadda yin hakan ya tanada, wato na girka abincin da za a raba ma jama'a su ci domin murnan fitowar wannan mata mai Iskan 'Gbemu', a matsayin sadaka don sallamar Iskan borin 'Gbemu', ba zai }ara dawo mata ba, sai wata shekarar ta kewayo.

**'Madawa'**: Bori ne da aka san mata ne kawai ke hawa. A lokacin da Iskan 'madawa' ya shiga jikin mace, za a ga ta yi zugum, ta }ura wa sashe guda ido, sannan ta fara kuka na ]an wani lokaci daga baya kuma ta soma wa}e-wa}e iri daban-daban cikin harshen Gbagyi. Wa]annan abubuwa da ta yi, alamu kenan da ke nuna kamuwa da Iskan 'Madawa'.

Haka kuma, ana iya kamuwa da wannan nau'i na borin Gbagyi ta yin gado, wato har idan mahaifiyar mutum tana da wannan Iska sai ta rasu, Iskan kan fita daga jikin mamaciyyar ya koma kan wata danginta da ke a raye. Da zarar Iskan ya shiga jikinta ko da cikin jama'a ta ke, sai kawai a ga ta tuma ta yi tsalle ta fa]o }asa tana buga tafin }afafunta a }asa, tana zazzare idanu, bakinta ya cika da kumfa, sai ta kama ihu kamar haka: 'Ahaiyyee!!!' 'Ayyah!',

'Madawa ~a lo she ko lo, Ayyah!' ma'ana (Idan Iskan Madawa zai haye sama ya hau, Eho!) tana maimaita haka sau da yawa.

A cikin irin wannan hali ne mutanen da ke tare da ita za su tambaye ta abin da ya same ta, sai ta fa]i sunan Iskan mamaciyar da ya shiga jikinta, misali; ‘Ngazhiya’ ko Mama ko ‘Mejelo’ ko ‘Cekutsan’ ko ‘Ngazhi’ da sauransu. Da yake kuma ana iya samun Iskoki zaune cikin wurare daban-daban da suka ha]a da: itatuwa da koguna da rafuffuka da }ungurmin dazuka da Iskan goguwa da rijiyoyi da sauransu, idan Iskan daga itace ya fito, sai ta fa]i sunan itacen, misali; itacen ka]anya (lai shunwa) da itacen tsamiya (tsamiyawyi shunwa) da itacen goriba (gbakobe shunwa) da sauransu.

Amina (2013) ta }ara ba da haske a kan yadda ake kamuwa da Iskan ‘Madawa’. A bayanin ta, ta ce ana gadonsa ne. Domin ita kanta tana da wannan Iska ta ‘Madawa’ wanda ta gada daga Mahaifiyarta. A lokacin da aka haife ta, dabbar da aka yanka na zanen sunanta, ana cikin fe]e ta sai aka taras da ]an gatari da ake kira da harshen Gbagyi “Aze-bhi” a cikin dabbar (Ana iya ganin hotonta ri}e da ]an gatari a shafin rataye na hotuna). Daga nan aka gane tana tare da wannan Iska ta ‘Madawa’ sai iyayenta suka ajiye mata a cikin kayayyakin ‘Madawa’ wanda ta tashi tana amfani da shi wajen hawa borin ‘Madawa’ da taimakon jama’a marasa lafiya da magunguna na cututtuka iri daban-daban da suka danganci Iska.

Wannan fanni na borin Gbagyi na da sutura ta musamman da suke sawa a yayin da Iskan da ke kansu ya motsa, da yake wannan borin ya shafi mata ne ka]ai, sukan yi ]ammara da zani ko wani irin launi, su kama shi su tsuke, su }ulla a baya kamar bante, su sanya farar riga ta sa}i da guraye na rataya jiki. Kayan ki]an ‘madawa’ ya ha]a da: kabulu da goge da sauransu.

Wannan fanni na Borin Gbagyi ba a yi masa Girka sai dai akwai wata al’ada da akan yi na sallama wanda ake kira a harshen Gbagyi ‘Aphya-Aguzheyin ya’ daga shekara sai wata shekarar wato idan Iskan ‘Madawa’ ya hau, sai a dafa abinci a yi yanke-yanke na awaki da kaji a }arshen shekara lokacin da aka ]ebe amfanin gona da nufin cewa an sallami Iskan, ba zai dawo ba sai a wata shekarar.

Borin **‘Gbunu’**, wannan Iska ne da ke iya shigan namiji ko mace. Alamun kamuwa da shi, shi ne za a ga mutum ya yi zugum wato ya zauna shiru yana fuskantar gefe ]aya na tsawon wani lokaci, sannan kuma daga baya ya soma wa}e-wa}e daban-daban. To zarar an ga haka borin ya motsa kenan Iskan ya hau dokinsa.

Bayan da Iskan ya hau ]an borin sai a kawo kayan ki]i wanda tulu ko tukunya ce ]inkakkiya da fata kamar kalangu ana ka]awa da tafin hannuwa saboda Iskan ya hau da kyau, bayan wani lokaci sai ]an borin ya ci gaba da wa}a yana gaishe-gaishe. Bayan haka sai ya soma fa]a wa jama’a da ke wurin musamman ma in akwai marasa lafiya da ya danganci Iska ko maita ko wani abu makamancin haka sai ya fa]i sanadiyyar ciwon da kuma hanyoyi da za a bi a samu waraka.

Irin wannan Iska, ba a yi masa girka, sai dai akwai wata al’ada ta shiga daji da wanda Iskan ya shiga sau ]aya a shekara wato lokacin da ake noman dawa da nufin an je sallamar Iskan ba zai sake dawowa ba sai an adana amfanin gona. Lokacin da za a kai mutum daji, za a tafi ne shiru ko gaisawa da wani babu balle a yi wata magana. A cikin dajin akan yanka kaza a gasa wa mai borin ‘Gbunu’ ya ci da albasa shi ka]ai. Bayan an gama, sai a dawo ana wa}a kamar haka: ‘Gbunu yee!, Gbunu yee!!.

Suturar borin ‘Gbunu’ shi ne: Maza kan ]aura zani na kowani irin launi amma ban da ba}i a }ugu, su rataye wasu zanuwa a ‘yan sandunna da sukan sa~a a kafa]unsu, sukan kuma shafe fuskokinsu da farin }asa wato (jojo). Su kuma mata kan yi ]ammara ne da zanuwa, su jawo su }ulla a baya kamar bante. Sukan kuma rataya wasu zanuwan a kafa]u.

Kayan ki]an ‘Gbunu’ ya ha]a da: Tuluna ]inkakku da fata kamar kalangu da ake ka]awa da tafin hannu.

Borin Gbagyi ya samo asali daga kaka da kakanni ta hanyar bauta a matsayin addininsu na gargajiya. A wancan zamani, duk da cewa sun yarda akwai Allah, sai imaninsu ya fi karfi a kan

bautar gumaka da Iskoki domin neman biyan wasu bu}atu na rayuwa da suka ha]a da: neman kyawu da yawan anfanin gona da neman haihuwa da neman waraka daga cututtuka daban-daban. A nawa hange, ha]uwar Gbagyi da Hausawa da ya]uwar addinin Musulumci, sun taka muhimmiyar rawa a rayuwar Gbagyi a yau. Da ba domin haka ba, abu ne mawuyaci a raba yawancinsu da tsafi da bautar Iskoki.

### 1.10 Na]ewa

Wannan babi, ya bayyana mana cewa, bori a matsayin bautar Iska kuma ]aya daga cikin addinin gargajiya na Hausawa da Gbagyi, da]a]]en al'ada ce. Tattauna a kan tarihin Hausawa da Gbagyi da aka yi, an yi ne domin a fahimci ainihin ko su wa ake }o}arin yin nazarin borinsu. Binciken ya yi }o}arin bayyana yadda Hausawa da Gbagyi suka ha]u, aka samu dangantaka ta musamman a manyan garuruwan Gbagyi kamar: Kuta da Minna da Suleja da Birnin Gwari a jihar Kaduna. Gbagyi dama al'umma ne masu wata ]abi'a na }aunar ba}i da sau}in kai wajen mu'amala da jama'a idan har ba za a mamaye masu filayen noma ba, saboda haka ake ganin halaye irin nasu ya kawo sau}in samar da dangantaka tsakaninsu da Hausawa har ya haddasa sauyi a yanayin aiwatar da borin Gbagyi a yau. Ma}unshin babin, ya ha]a da bayanai a kan ma'anar al'ada da ma'anar bori na Hausawa da na Gbagyi da ire-irensu, an kawo dalilan da suka haddasa yin wannan bincike, da muhimmancin binciken. An kuma dubi farfajiyar bincike, wato wuraren da binciken ya yi iyaka. A can }arshe, an kawo bayanai a kan matsalolin bincike da kuma hasashen bincike.

## BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

## 2.0 Shimfi]a

Masana da Manazarta sun gudanar da ayyuka da dama wa]anda ke da ala}a da wannan aiki. Don haka, wannan waiwaye ya ta'alla}a ne kan litattafan da aka wallafa da ke da ala}a da wannan fage kai tsaye, ko kuma inda aka ta~o wani ~angare na wannan bincike. Haka kuma, za a dubi kundayen digiri na uku da na biyu da kuma na farko da ke da ala}a da wannan aiki. A }arshe, za a yi waiwaye kan mu}aloli da }asidu da aka gabatar a tarurrukan }ara wa juna sani ko aka buga cikin mujallun ilmi har da ma jaridu da suka shafi wannan fage. Saboda haka, waiwayen zai zama wata matashiya ce ta sanin inda aka sa gaba.

## 2.1 Wallafaffun Litattafai

A wannan ~angare, za a dubi ayyukan ne ]aya bayan ]aya don yin bitar su. Yin bitar zai taimaka wajen fahimtar inda aka kwana game da nazarin borin Gbagyi da dangantakarsa da na Hausawa.

Daga cikin wa]anda suka yi rubuce-rubuce a kan abubuwan da suka shafi bori akwai irin su Bunza (2006:21-31), a littafinsa, ya yi bayanai da dama da suka ha]a da: ma'anar bori kamar haka:

*"A ganina, kalmar ba za ta rasa ala}a da kalmar "bore" ba. Watau, idan ana dafa abinci a tukunya, idan an rufe tukunyar da faifai, da zarar ta tafasa, za ka ga wani kumfa na tasowa yana bugun faifan ko abin da aka rufe tukunyar da shi. Idan ba a yi gaggawa aka bu]e ba yana iya kashe wutar. To! da zarar, tukunya ta yi haka sai a ce "ta yi bori". Wata}ila kwatanta irin za~ar~akar da kumfa da boren da tukunyar ke yi ne ake danganta shi da irin halayyar ]an bori idan ya hau bori. Domin da ya hau bori, za ka ga kumfa na fita a baki, idanu na zazzarowa yana fizge-fizge da mi}e-mi}e".*

Bunza, (2006) ya }ara da cewa: A idon manazarta, borin da ake gudanarwa a }asar Hausa yana da rabe-rabe sosai idan aka lura da yadda ake aiwatar da shi da dalilin aiwatar da shi. Ga

kashe-kashen Borin kamar yadda masu Bori, da manazarta Bori, suka hange shi: i. Borin Fage ii. Borin Magani iii. Borin Giri iv. Borin Girka.

Ya kuma kawo bayanai a kan tanade-tanaden girka wanda ya ha]a da kayan aiki da sutura da abinci da yadda ake ha]a kayan girka da dandalin borin girka da yanayin zaman girka da kuma yadda bori ya yi tasiri a rayuwar Hausawa a yau. Ha}i}a, wa]annan bayanai nashi sun shafi wannan bincike da za a gudanar kuma za su taimaka.

DjeDje (2008) ta yi aikinta ne mai suna *Fiddling in West Africa*, a cikin wannan littafi nata, ta yi }o}arin gaske wajen tattaro bayanai a kan kayan ki]an 'yan bori na wasu }asashen Afrika ta Yamma har da Nijeriya inda ta yi bincike na musamman a kan yadda ake ha]a kayayyakin ki]an bori a tayar da saututtuka daban-daban da hanyoyin da ake bi don kiran Iskokin 'yan bori a }asashen Hausa da suka ha]a da goge da garaya da kacakaura da sauransu. Ta kuma bayyana muhimmancin wa]annan kayan ki]an 'yan bori da cewa ta karin sautin ki]a ne ake sanin ko wani irin Iska ne ke hawa dokin ]an bori idan zai hau, domin kowane Iska na da taken ki]ansa.

Mbiti (1991:70 – 81), a littafinsa, ya kawo bayanai da dama a kan Iskoki. Ya bayyana cewa a ganin al'umman nahiyar Afirika, duniya ta }unshi abubuwa biyu: wa]anda ake iya gani da ido da wa]anda ba a iya gani. An yarda cewa ban da Allah mahallici da kuma 'yan Adam, akwai wasu halittu da suka mamaye duniya. Wa]annan halittu su ne Iskoki. Akwai Iskoki daban-daban da dama. Allah ne ya hallice su kamar dai yadda ya hallici kowane abu. Iskoki na da matsayi ta musamman tsakanin Allah mahallici da mutane, kuma ba su yi kama da juna ba. Mutane sun danganta su da 'yan Adam har sukan bayyana halayensu kaman na 'yan Adam da suka ha]a da: tunani da furuci da basira, kuma an yi musu baiwa ta }arfi wanda su ke iya amfani da shi ta yadda su ke bu}ata. Allah ne ya hallice su, }ar}ashin ikonsa su ke, kuma sun dogara ne a kan sa, haka kuma Allah mai girma na amfani da wasu daga cikinsu wajen nuna zatinsa.

Marubucin ya karkasa Iskoki gida biyu duk da cewa wasu na da halaye iri ]aya da kuma wa]anda nasu ya bambanta, wato masu kyau da marasa kyau, kamar na ‘yan Adam a ko’ina cikin duniya. Akwai Iskoki halitattu na sama da na }asa kamar haka: rana da wata da taurari da bakan-gizo da ruwan-sama da hadari da iska da tsawa da wal}iya. Sai kuma halittu na ]an-Adam da aka raba gida biyu kamar haka: matattun mutane da da]ewa (fatalwansu) da matattun mutane da ba su da]e da mutuwa ba. Mutane sun ]auka cewa wa]annan hallitu su kansu su ne Iskoki ko kuma akwai Iskoki a cikinsu da ke sarrafa su. Marubucin ya kawo bayanai a kan halayen Iskoki; masu kyau da mara sa kyau, da ma bayanai a kan siffofinsu da sauransu.

Shi kuwa Nicole (1991), a littafinsa ya kawo bayanai ne kan mafari da aikace-aikacen borin Hausa a addinin Adar da ke }asar Nijar. Ya kawo bayanai masu inganci dangane magunguna musamman na mata da Iska kan shige su ta yadda za a bi a sama musu waraka. Wannan aiki yana da fa’ida a wannan fage na bincike.

Yahaya da Wasu (1992:88), a littafinsu, sun yi }o}ari wajen kawo bayanai masu inganci kan mutanen ~oye wato Iskoki da ya ha]a da bayyana ma’anar kalmar mutanen ~oye wato Iskoki da wuraren zamansu da yadda ake ha]uwa da su da al’adun da ake yi wa Iskoki da nau’o’in Iskoki.

Kirk-Greene da Ryan (1975:34), a bayanan da ke cikin littafinsu, sun ce ‘An danganta asalin al’adar gargajiya na Gwari da na mutanen Borno. Gwari suna da ra’ayin ri}au na cewa su Kanuri ko Bari-bari ne. Kuma a wani lokaci da can, sun yi magana da harshen Kanuri. A yau saboda wasu dalilai, babu alamar wannan zance. Bayanan nasu za su taimaka wajen sanin tarihi da asalin Gbagyi.

Habib da Wasu (1982), a aikinsu, sun kawo  bayyanai muhimmai kan al’adun Hausawa da suka ha]a da tarihin asalin Hausawa misali kamar yadda suka ce: “Shin Hausawa sunan }abila ne ko sunan harshe? Su dai Hausawa, suna ganin kansu }abila ne. To amma duk wanda ya tsaya ya bayyana ma’anar kabila sosai, sai ya ga Hausawa sun }i shiga.

Misali bisa bayanin marubuta, }abila al'umma ce mai asali ]aya, da harshe ]aya, da kamanni (watau }irar jiki) kusan iri ]aya, da al'adun gargajiya iri ]aya, da sauran irinsu. Kuma lallai ne cikin wannan al'umma kowa yana da'awar shi ]an }abilar ne". Sun kuma kawo bayanai a kan tarbiyya da sana'o'i da addini da magunguna da shugabanci da bukukkuwa da dai sauransu. Wannan aiki shi ma zai taimaka wajen cin ma manufa a wannan bincike.

Besmer (1975), ya yi rubutunsa ne a kan tsarin bori da matakan aiwatatar da shi, a wannan aiki nashi ya bayyana ma'anar bori da kuma matakan da ake bi wajen hawan bori dangane da irin Iskan da ke kan ]an borin. Wato bayaninsa na }o}arin nuna cewa ba kawai ]an bori zai hau bori ba ne ba tare da wani dalili ba, saboda haka kafin a samu ]an bori ya hau, sai in fa an ka]a takensa ko kuma ya ji ana ka]a takensa Iskan da ke kansa sai ya motsa sannan ya hau bori.

Har ila yau, Besmer (1977), ya wallafa littafi ne a kan yadda ake tabbatar da ]an bori cikin }ungiya: Nazari na musamman a garin Ningi'. Wannan bincike ne na musamman da marubucin ya gudanar a cikin garin Ningi kan yadda ake tabbatar da wanda Iskoki ko aljannu suka shiga jikinsa, an kuma yi magani an kasa samun sau}i, sai a kai shi gurin 'yan bori su yi masa girka, Iskan da ke kan majinyacin ya zauna a kansa daram. Ke nan shi ma ya zama ]an bori.

Madauci da wasu (1968), sun wallafa littafi da ya kawo bayanai masu inganci a kan bori, a cikin wannan aiki sun nuna muhimmancin bori wajen danganta shi da samar da waraka daga cututtuka, haka kuma ba wai kawai ana hawa bori don nisha]i ko neman abinci ba ne. Har wayau, sun }ara da bayani a kan ire-iren Iskoki da tufafin da akan sa idan Iskar mai bori za ta hau. Wannan aiki na da ala}a na kai tsaye da wannan bincike.

Greenberg, (1941:45), a littafinsa, ya zayyana muhimman abubuwan da ake bu}ata wajen yin girka idan har ana son a samu biyan bu}ata. Daga cikin abubuwan da ya zayyana akwai; tunkiya ko akuya ko }adduwa amma ana iya amfani da kaza idan wa]ancan sun fi }arfin mutum. Ya }ara da cewa; "a dalilin kasa samun }arfin sayan dabbar girka ya sa da can ba haka kawai mutum kan hau

bori ba, sai dai idan Iska ya shafe shi ko ya shige shi.” Wa]annan bayanai nasa suna da ala}a ta gaske da wannan aiki.

Byamyiko (1997) marubucin littafin ya yi sharhi ne kan batutuwa da suka ji~anci asali da tarihin al’ummar Gbagyi wato inda suka samo tushe da bayanin yadda suka ya]u kuma suna zaune a inda ake ganinsu a yau. Da yake akwai tababa tsakanin masana tarihi da manazarta a kan asalin Gbagyi, wannan aikin sa zai taimaka ma wannan bincike wajen gano ainihin asali da tarihin Gbagyi.

## 2.2 Kundayen Digiri

An waiwayi kundaye na digiri daban-daban daga na uku zuwa na biyu da na ]aya da ke da ala}a da wannan bincike. Daga cikin wa]anda aka waiwaya akwai:

### 2.2.1 Kundayen Digiri na Uku

Abdullahi (2008), kundin digirinsa na uku mai suna: “Jiya ba Yau ba: Waiwaye a kan Al’adun Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa”, ya yi maganganu ne masu muhimmanci dangane da matakan da Maguzawa ke bi wajen gudanar da harkar rayuwarsu na aure da haihuwa da kuma mutuwa, wato bisa tafarkin Maguzanci da ya ha]a da tsaface-tsaface da bautar Iska. Alal ha}i}a, a bayanan nasa ya nuna cewa rayuwar Maguzawa, rayuwa ce tamkar ta tsafi da bautar Iskoki wajen tafiyar da al’amarorinsu na yau da kullum. Idan ya kasance za su aurar da ‘ya’yansu mata tilas sai an yi abin da al’ada ta tanada wato tuntu~ar matsafa domin kawar da wani mugun abu ko Iska a tabbatar da ingancin wannan aure. Haka kuma al’amarin yake a wajen bukukuwan haihuwa da mutuwa.

Bunza (1995), cikin aikinsa mai suna: “Magungunan Hausa a Rubuce: Musamman Nazarin Ayyukan Malaman Tsibbu”. Kundin digiri na uku, ya yi }o}arin gaske wajen fito da magungunan Hausa a rubuce sannan ya bayyana yadda malaman tsibbu ke gudanar da ayyukansu na tsibbu tare

da yin wasu ‘yan maganganu na surkulle da sihirce-sihirce wajen bayar da magunguna ko taimakon warkar da marasa lafiya ta hanyar amfani da Rauhanai ko Aljannu.

### 2.2.2 Kundayen Digiri na Biyu

Har wayau Bunza (1989), ya gudanar da nazarin neman Digiri na biyu mai suna: “Haya}i Fid da na Kogo” inda ya nazarci siddabaru da sihirin Hausawa. A wannan aiki nasa, ya kawo bayanai masu inganci da ma’ana a kan asalin Hausawa da addininsu da asalin Kalmar Hausa da bayani a kan ko su wane ne Hausawa da lardunan }asar Hausa da yanaye-yanayenta da addinin gargajiya na Hausawa da ya ha]a camfe-camfe da tsafi da bori da ire-irensa har ma da bayani a kan dalilan bori kamar haka: Nazari da tattaunawa da wasu ‘yan bori ya nuna cewa dalilai uku ke haddasa bori. Akan samu wani ]an bori dalili ]aya ya sa shi wani kuwa biyu ko ma ukun duka. Ga dalilan: (1) Nisha]i (2) Neman Abinci (3) Neman Warkewa.

Nisha]i, kusan shi ne babban dalili na hawan bori. Kusan mafi yawan ‘yan bori ba su hawan bori sai bayan an kai amfanin gona gida. Da zarar an kawo abinci gida, to fa, a }auye yanzu kana jin wata ta hau, nan wata ta hau, wurare daban-daban. Ko kuma abin farin ciki ya samu, ko kuma bayan dare da an ci abinci yanzu kana jin wata ta hau bori.

Wasu sun ]auki bori kamar sana’a ce ta neman abinci da sutura. Sukan dinga yawo unguwa-unguwa, gari-gari neman girka ko buki su hau bori a yi ta yi musu karin ku]i. Kuma kusan duk inda ake yin bori za ka tarar da cewa an tanadi gara sosai kamar kaji da man shanu da shinkafa da waina da dai kayan da]i a yi ta hawan kaya. Don samun cin wannan gara~asa wasu mutane ke shiga bori.

Ga wasu abin ya zama dole ne, domin wata cuta ke kama su a ce dole sai an yi girka, kuma a wurin girka dole sai an hau bori. Kuma ko bayan an yi girka, a duk inda aka ji an sa ki]an al’jannin ]an bori dole ya hau bori ko ya mutu, ka ga ai ko don ku~uce wa mutuwa dole a hau. Wato abin ya zama dole don kare kai.

Ibrahim (1982), kundin digiri na biyu mai suna: “Dangantakar Al’ada da Addini: Tasirin Musulumci kan Rayuwar Hausawa ta Gargajiya”. Ya yi bayani daban-daban a nazarinsa kan addinin gargajiya na Hausawa wanda ya ha]a da; bautar Iskoki da gumaka da kuma bori wa]anda shigowar Musulunci daga baya ya yi tasiri a kan su. Ya kuma kawo ma’anar bori da ire-irensa da sunayensu da kuma yadda ake yi wa mutum girka idan Iskoki sun shige shi an memi magani an rasa kan ciwo sai a tafi wurin ‘yan bori, suma idan sun yi maganin iskokin majiyyaci bai warke ba, sai su nemi yardar ‘yanuwan majiyyacin don a yi masa girka.

Abubakar (1997), a nazarinsa mai suna “Bori a Zariya”, kundin digiri na biyu, ya yi magana ne a kan ma’anar bori da kuma yadda ake gudanar da shi a Zariya. A aikinsa, ya kawo bayanai kan ma’anar bori da ire-iren sunayen Iskoki da tufafin ‘yan bori da yadda ake zama ]an bori da kirarin Iskoki daban-daban da yadda ‘yan bori ke warkar da majinyata daban-daban wa]anda cututtukansu sun shafi ta~uwar Iskoki ko aljannu.

[an-Asabe (2006), ya yi aikinsa na neman digiri na biyu ne kan “Tasirin Al’adun Hausawa a kan na Gwarawa”, inda ya yi bayanai a kan sauye-sauyen da rayuwar al’ummar Gwarawa ya samu a sakamakon cu]anya da Hausawa, a fannoni da suka shafi aure da haihuwa da suna da zamatakewa da shugabanci da sana’o’i da bukukkuwa da harshe da addini da sauransu, amma duk da yake aikin na da ala}a da wannan bincike, mazarcin bai yi magana ta musamman a kan bori ba.

Filaba (1994), a bincikensa mai suna “Karu, Kunape and Kurkundu Kingdoms: A History of Social, Economic and Poltical changes among the Gbagyi in Central Nigeria”, wato: ‘Daulolin Karu da Kunape da Kurkundu: Tarihin canje-canje a Zamantakewa da Tattalin arziki da Siyasa a tsakanin Gbagyin da ke Tsakiyar Nijeriya’, kundin digiri na biyu, ya yi bayanai ne da suka shafi sauye-sauye da aka samu na zamantakewa da tattalin arziki da siyasa a tsakanin Gbagyi da ke zaune tsakiyar }asar nan. Wa]annan canje-canjen da suka samu, sun shafi halin rayuwarsu na yau da kullum.

Wurma (1991), a nazarinsa na neman digiri na biyu mai suna: “Tasirin Hausawa a Tarihin Afirka ta Yamma”, fassarar littafin ‘*The Hausa Factor in West African History*’, na Mahdi Adamu, ya yi kyakkyawan aiki kan tarihin shugabanci a Birnin Gwari da ke Jihar Kaduna, inda kuma ya bayyana irin mamayar da al’adun Hausawa ya yi wa al’adun Gwarawan yankin, kusan ma har sun mance nasu, sun rungumi na Hausawa musamman ta fannin shugabanci inda ya yi bayani cewa kafin }arni na goma sha bakwai (}.17), Birnin-Gwari da ke makwabtaka da }asar Katsina da kuma Zazzau ta kasance }asa ce da Allah Ya yalwata ta da }asar noma mai albarka da kuma ]imbin namun daji wanda sune dalilan da suka haifar da zaman Gbagyi a garin. Hausawa su suka bai wa garin suna Birnin-Gwari don nuna cewa }abilar Gbagyi ne masu garin kuma mazauna cikinta.

A aikinsa, ya }ara bayyanawa cewa ba wani abu ya }ara ha~~aka garin na Birnin-Gwari ba, sai ha]uwarsu da ba}i musamman Hausawa. Tarihi ya nuna cewa wani Bakatsine da ake kira Malam Sharif ne ya yi sanadiyyar cu]anyar Hausawa da Gbagyi mazauna garin, wanda da tafiya ta yi tafiya ]ansa ya zama Sarkin Birnin-Gwari.

Malam Sharif ya baro Katsina ne don yawon bayar da magunguna na gargajiya da asirai musamman na tsaro da jarunta. Malam Sharif ya yi suna sosai a }asar Gbagyi musamman a wajen Sarakuna wa]anda ya taimaka wa da asirai da magunguna. Bayan ya gama zagaye masarautar Gbagyi da ke Kuta da Alawa, sai shi da iyalinsa suka koma Birnin-Gwari da zama, kasancewar garin na iyaka ne da }asar Hausa musamman Zariya da Katsina. Da isar Malam Sharif Birnin-Gwari, Sarkin garin da jama’arsa wa]anda dukkansu Gwarawa ne sun kar~e shi hannu bibbiyu ha]e da tanadar masa da wurin zama. Da zama ta yi zama, aka zo aka na]a [an Malam Sharrif mai suna Waike sarkin Birnin-Gwari. Waike ya samu Sarautar garin ne da goyon bayan Gwarawan garin ba don komai ba, sai don hangen irin rawar da mahaifinsa ya taka dangane da tsaron gari. Na]a Waike Sarkin Birnin-Gwari ke da wuya sai ya fara kai hari a garuruwa da }auyukan Gwarawa  har ya yi nasara a kan su suka amince su zama }ar}ashin masarautarsa. Masana tarihi sun bayyana cewa

wannan shi ne farkon mulkin Hausawa a }asar Gbagyi wanda ake zato ya faru ne tun wajen shekara 1760. Dangane tarihin ha]uwar Hausawa da Gbagyi, wannan aiki yana da ala}a da wannan bincike.

Badejo (1980), ya yi nazari ne mai suna "Bori Spirit Possession Religion As a Dance Event: A Pre-Islamic Hausa Phenomennon", wato 'Bori a matsayin addini na raye-raye'. Kundin digiri na biyu. Bayanai a cikin wannan aiki ya ta~o yadda Hausawa ke gudanar da harkokin bori ne kafin zuwan addinin musulumci wato sun ]auki bori a matsayin addininsu na gargajiya da suke aiwatarwa ta hanyar ka]e-ka]e da raye-raye musamman a yayin hawa bori dole sai an ka]a taken ]an bori kafin Iskarsa ya hau. Kuma ta hanyar ka]e-ka]en ne ake sannin kowane Iska ]an bori zai hau ko ya shigi majiyyaci kafin a zaunar da shi a kansa ba tare da gardama ba wato a lokacin yi masa girka.

Gobir (2002), ya yi bincike ne na neman digiri na biyu a kan: "Iskoki a Idon 'Yan Bori da masu Ru}iyya". Wato bayanai ne da suka ji~anci yadda 'Yan bori da masu ru}iyya suka fahimci mutanen ~oye wato Iskoki, ya kuma fito da hanyoyi da masu ru}iyya kan bi wajen fitar da Iskoki a jikunan mutane idan sun kamu da kuma hanyoyin da 'Yan bori kan bi don yi ma majiyyata girka Iskan da ya shige su ya zauna a kansu daram.

### 2.2.3 Kundayen Digiri na [aya

Abubakar (1977), ya gudanar da bincikensa ne don neman digiri na ]aya a kan: "The Coming of Zegi-zegi and its Effect on Koro/Gwari Relationship in 19$^{th}$ century". Bincike ne na tarihin abubuwan da suka faru da dangantakar }abilun Koro da Gwari a shigowar Zazzagawa }asarsu a }arni na sha tara (k.19). Wato a wannan lokaci duk da yake Koro da Gwari sun da]e suna tare da juna duk inda ka ga Koro zaune to za ka ga Gwari wato makwabta kuma abokanan juna ne sosai. A shigowar Zazzagawa tsakaninsu sai aka sami sa~ani na shugabanci, wanda ya haifar da a yau a yankin Ija na }arar Abuja, masarautar garin ya kasu biyu akwai sarkin Ija Gwari da sarkin Ija Koro kowani sarki na mulkin }abilarsa.

Shi ma Alhassan (1987) a kundin bincikensa na neman digiri na ]aya, ya tofa albarkacin bakinsa a kan dangantakar da ke akwai tsakanin }asar Hausa da ma}wabtansu, wanda ya ha]a da }asar Gwari. Wato ya kawo bayanai a kan ha]uwar Hausawa da Gwarawa, da kuma dalilai da hanyoyin da suka ha]a dangantaka. Wannan aiki nashi zai taimaka wa wannan bincike.

Dutse (1989), ya gudanar da bincike ne a kan "Yadda ake hawan Bori da Iskokin da ake kira", kundin neman digiri na farko. Ya yi bayanai ne a kan matakan hawa bori idan mutum ya kamu da Iskoki, kuma kowani ]an bori na da nashi irin Iska da ake kira idan ya hau.

Busa (1992), a Kundinsa na neman digiri na ]aya da ke magana kan "Cuta da Magani a {asar Gwari: Dangantakarsu da na }asar Hausa", Wato ya gudanar da nazari ne kan yanayin cututtuka da magungunan Gwari da yadda suke da nasaba da na Hausawa. Ta fannin magungunan Gwari ya ba da haske kan rawar da masu bayar da magungunan gargajiya da ya ha]a da bokaye da magora da 'yan bori kan taka wajen gano cututtuka da bayar da magunguna domin samar da waraka. A cikin bayanansa ya kawo misalai na cututtuka da magunguna na Gbagyi da ke da dangantaka da na }asar Hausa.

Dada (1999), bincikensa a kundin neman digiri na ]aya, ya ta'alla}a ne kan "Tasirin Hausa a wa}o}in Gwari: kwatankwaci da wa}o}in Walo Shatan Gwari" a nazarinsa, ya yi magana a kan yadda mawa}in nan Walo Shatan Gwari ya yi amfani da kalmomin Hausa a cikin wa}arsa, wato ya nuna cewa akwai kyakkyawar mu'amala ta zamantakewa tsakanin al'ummun biyu wanda ya kai ga cewa kalmomin harshen Hausa sun yi tasiri a wa}o}in Gbagyi da yake a yau yawancin wa}o}in Walo da wuya bai ha]a da Karin magana ta Hausa ba. Har ila yau kayan ki]ansa da ake kira 'mulo' a harshen Gbagyi wato abin da Hausawa ke kira molo, ya yi kama da garaya da Hausawa ke amfani da shi wajen ki]an 'yan bori. Idan an yi la'akari da bayanin da ke bisa, ke nan za a ga cewa wannan aiki na da fa'ida a wannan bincike.

Sani (1991), ya kawo bayanai masu inganci a bincikensa na neman digiri na farko, inda ya bayyana asalin kafuwar unguwanni da muhimmancin kafa su a garin Minna, haka ma ya ta~o maganganu a kan masarautar Minna da sauran yankunan da suka }unshi masarautar Minna. Wa]annan bayanai nashi ba za su rasa nasaba da wannan bincike da ake }o}arin yi ba ta fuskar dangantakar Hausawa da Gbagyi. Ya bayyana yadda tun asali unguwanni da masarautar garin Minna suke kafin a samu kwararowan ba}i kamar Hausawa su cu]anye da Gbagyi.

Shi Maikanti (1997), a bincikensa na neman digiri na farko mai suna: "Tasirin Al'adun Hausawa da na wasu {abilu mazauna Wushishi: Tsokaci a kan }abilun Nufawa, Gwarawa, Dukkawa da kuma Kambari". A cikin wannan aikin, an bibiyi ma'anar al'ada da ka]an daga cikin tasirin da al'adun Hausawa da na wasu {abilu mazauna Wushishi a kan wasu }abilu har da Gwarawa, wanda manazarcin ya ta~o bayanai a fannin aure da sutura da addini ne kawai bai yi tsokaci na musamman kan bori ba.

## 2.3 Ma}alu

A wannan kudiri na bincike, an dubi wasu ma}aloli da aka gabatar a cikin mujallu, da suka shafi wannan fage na bincike kai tsaye ko a fakaice. Daga cikin wa]anda aka duba akwai:

Maikanti (2010), aikin da ya yi a kan 'Borin Girka', ya yi bayyani ne kan muhimmancin borin girka kafin zuwan addinin Musulumci. Ya }ara da cewa da can bori an ]auke shi a matsayin hanya ce ta neman waraka ta gargajiya mai sau}i, amma shigowar addinin Musulumci da wayewar zamani, sai aka fi ba asibiti muhinmmanci. A cikin aikinsa, ya yi magana ne kan ire-iren bori, da matakan da ake bi wajen yi ma ]an bori girka da kuma ire-iren amfani da ake yi da bori wajen warkar da cututtuka daban-daban.

Shi kuma Besmer (1973b), ya yi aikinsa ne kan "Praise-epithets and Songs Texts for Some Important Bori Spirits in Kano". Wato kirare-kirare da wa}o}in wasu Iskokin 'yan bori a Kano. A

nan ya yi bayani ne cewa a Kano idan Iskan ]an bori zai hau dokinsa, akwai kirare-kirare da karin sautin wa}o}i na masamman da ake yi ma ]an borin ba wai haka kara zube ake ka]a take ba. Saboda haka akwai take na kiran kowani irin Iska da ya shigi majinyyaci ko ]an bori da zaran an ka]a wannan take har kuma ya dace da na Iskan da ya hau sai bori ya hau idan kuma bai dace ba duk irin taken da za a ka]a bori ba zai hau ba. Haka kuma Besmer a (1973a) ya rubuta ma}ala mai suna: "Avoidance and Joking Relationships in Hausa Supernatural Spirits". Wato hani da dangantaka ta barkwanci na Iskokin Hausawa. Wato ya lura cewa 'yan bori sun karkasa kansu gida-gida, kowani kashi na da rawa iri hu]u, kowani rawa na da halayen yin sa, kowani hali ya danganci irin Iskan da ke kan ]an bori. A yayin rawan bori tufafin da ya sa idan har bai dace da Iskan da ya hau kansa ba sai a canja masa da wani launi har sai an tabbatar da irin Iskan da ya hau kansa. Har ila yau a kan yi amfani da wasu kayayyaki wajen gane kowani irin Iska ne ya hau kan ]an bori kamar takalma (sandal) na Iska mafarauci da gaturu na Iskokin daji da farin babban-riga na malam Alhaji. Wato a nan manazarcin ya kawo bayanai ne na hannunka mai sanda a kan abin da bincikensa ya gano ta yadda a yayin ka]e-ka]en taken Iskokin 'yan borin Hausa akan danganta sautukan ba tare da an yi ma kowanne nashi na musamman ba. Haka yana haddasa matsala a lokacin kiran Iskoki domin tabbatar da wanda ke kan ]an bori har ma a samu a raba ko kuma a zaunar da Iskan a kansa ko kuma a yi masa girka.

Arohunmolase (1999:60), ya yi nazari a kan "Nigerian Indigenous Curative Medicine: Efficacy and Problems". Manazarcin ya yi magana ne a kan magungunan gargajiya masu samar da waraka na Nijeriya, a bayaninsa, cewa ya yi "ba zai dace ba mutum kawai ya ya yi tunanin cewa magungunan Turawa na zamani su ne hanya ka]ain a samar da waraka", magungunan gargajiya daidai suke idan ma ba su ]ara na zamani ko na Turawa ba wajen kawar da cututtuka ko ciwowuka a tsakanin al'umma. A al'adar Hausawa, mutane sun yi imanin cewa duk ]an Adam lafiyayye ne, sai dai kawai wasu Iskoki ne ke bi suna barazana ga lafiyar mutane. Saboda ake zuwa neman magungunan gargajiya na Hausa domin samar da waraka da tsaro ko kariya daga miyagu. A ta}aice

manazarcin ya yi }o}arin nuna amfani ko muhimmancin maganin gargajiya ne musamman na Hausawa.

Uba (2006), a ma}alarsa mai suna: “kwatanta Bori da Ru}iyya wajen neman waraka”. Ya kawo bayanai da dama kan ma’anar bori da ru}iyya, ya kuma yi magana kan asalin ru}iyya da bori, da dalilan yin ru}iyya da bori, har ila yau, ya bayyana yadda ake ru}iyya da bori, a }arshe ya yi magana kan kamanci da bambancin ru}iyya da bori.

### 2.3.1 {asidu

An waiwayi }asidu da aka gabatar a tarurrukan }ara ma juna sani. Da farko, akwai Bunza (1998), }asidarsa mai suna “Matsayin Kai” da {imarsa a Idon Bahaushe”, ya kawo bayanai ne muhimmai a kan mizanin da Hausawa suka aza ‘kai’ da kuma yadda suka ]auki ‘kai’ da muhimmanci. A bayaninsa, ya nuna cewa Hausawa sun yarda kowane mutum yana da wani Iska a tare da shi. Ko da bai mayar da shi ya zama ]an bori ba, suna tare. Shi ya sa idan Bahaushe yana zaune ba ya son wani ya zo ya tsaya kansa, saboda kar Iskan da ke kansa ya tashi.

Bunza (2004), a }asidarsa mai suna “Magana da Iskoki ta Bakin Dokinsu” da ya gabatar a Jami’ar Bayero, ya yi magana ne a kan ire-iren maganganu da ‘yan bori kan yi da Iskoki ta irin Iskan da ]an bori ya hau, musamman idan ana son a yi ma wanda Iska ta shafa ko majinyyaci girka Iskan da ya shige shi ko ya rabu da shi ko a samu yarjejeniya na zama tare ba tare da matsala ba.

Bunza (2005), a }asidar da ya gabatar mai suna “Booru}iyya”: (Tazarar Bori da Ru}iyya a Idon Manazarta) a Jami’ar Bayero, ya yi magana ne kan asali da ma’ana da yanayi na bori da ru}iyya kamar yadda manazarta suka dube su. A nan ya bayyana ma’anar ru}iyya da cewa: “Ru}iyya, addu’ar da akan yi wa maras lafiya ce da a ke jin aljannu suka hawo kansa.” Daga wannan ma’ana da aka bayar a sama, za a fahimci cewa ru}iyya ba wata aba ba ce illa addu’a da ake yi wa mara lafiya wanda ake zaton Iskoki suka sa masa ciwon. Haka ma ya kawo ma’anar bori

kamar yadda masana al'ada suka dube shi kamar haka: Bori bauta ma Iskoki ne tamkar yadda musulmi ke bauta wa Allah domin samun wasu fa'idoji. Bori dai bauta wa Iskoki ne, wa]anda aka ce suna ganin mu amma mu 'yan Adam ba ma ganinsu idan ba sun bu]a mana ido ba. Bori na ]aya daga cikin hanyoyin bauta wa Ubangiji da mabiyansa kan bi ta kan Iskoki, watau aljanni don yin bautar. Masu bin addinin sun yarda akwai wani abin bauta wa babba, mai komai mai kowa, wanda kowa ke tsoro, kuma ba a ganin shi, kai tsaye, sai ta hanyar Iskoki.

Bisa wa]annan ma'anoni, za a fahimci cewa bori wata hanya ce da masu yin sa ke bi domin bautar Ubangiji ta hanyar aljanu da kuma neman waraka daga wani ciwo da ya shafi aljanu. A ta}aice ana iya cewa ru}iyya da bori duk hanyoyi ne da ake hul]a da aljanu domin neman waraka.

Shi ma Gobir (2013), a }asidarsa mai suna "Iska a tunanin Bahaushe a }arni na 21st", da ya gabatar a taron }ara wa juna sani a Jami'ar Bayero, ya yi magana ne a kan sifofin Iskoki da rabe-raben sunayensu da wuraren da ake samunsu da ma'anar cuta a tunanin Bahaushe da yadda Bahaushe ya ]auki iska da }ima da daraja da tunanin Bahaushe na zaton cewa duk cuta da za ta sami mutum da hannun iska a ciki, shi yasa ma bai ba da kai bori ya hau ba, wajen tunkarar cutukan Iskoki a asibitocin zamani.

Ibrahim (1986) a }asidarta mai take "A Study of Some Aspects of Ritual and Ceremonial Costume of The Hausa in Kano, Kaduna and Sokoto States", ta yi magana ne a kan tufafin gargajiya na 'yan Borin Hausa da ke Kano da Kaduna da Sakkwato. Ta yi }o}arin kamanta wasu tufafi na bukukuwa da na yin bauta na wasu sassan }asar Hausa. Ta yi nazarinsu ne domin gudun shu]ewar wa]annan al'adu kamar dambe da kokawa da bori da kuma rawar tsafi wa]anda ake sa}a tufafin dominsu nan gaba a dalilin cu]anya da Hausawa ke yi da wasu {abilu. Saboda a yau kusan ba a ganin su a cikin gari sai a karkara. Domin kuma duk da yake Hausawa sun amshi Musulumci, da can suna da tufafi na musamman na bukukuwa muhimmai. A yau wa]annan tufafi da al'adu na gargajiya sai dai a tsince su a }auyukan }asar Hausa. Ta }ara da cewa an samu tasiri na tufafin

gargajiya na Hausawa daga }abilun da su Hausawan suka ba alhakin taimakawa su sa}a masu kamar Nupe da Gwari da wasu }abilu. Saboda haka binciken nata ya mayar da hankali ne wajen tattarawa da tantacewa da kuma kwatanta wasu tufafin bukukuwan gargajiya na wasu sassa na }asar Hausa. Saboda kada wata rana nan gaba a neme su ko sunayensu ma a rasa.

Shugaban {ungiyar [alibai (2005b) a }asidarsa "The Gbagyi People and Historical Conciousness", wato 'Al'ummar Gbagyi da Fahimtar Tarihinsu' da ya gabatar a taron bikin ranar }ungiyar [alibai Gbagyi, reshen Jami'ar Ahmadu Bello Zaria. A jawabinsa, ya jawo hankulan al'ummar Gbagyi ne a kan muhimmancin raya al'adunsu da fahimtar tarihinsu. Wato a bayaninsa, Shugaban ya nuna damuwarsa ne a kan yadda wasu [alibai da ke kiran kansu Gbagyi basu damu da furta yarensu ba ko suna tare da 'yan uwa Gbagyi sai su gwammace su yi Turanci ko Hausa a ganinsa haka ba daidai ba ne kuma ba zai taimakesu ba. Ya }ara da cewa "harshe wani abu ne na al'umma rayayye muddin idan har al'ummar ta raya shi, idan ba a raya shi ba sai ya mutu". Saboda haka ya yi kira gare su da su yi kishin harshensu na uwa kuma su fahimci tarihin asalinsu domin su ha]a kai su zama tsintsiya ma]aurinki ]aya. A ta}aice manufarsa idan haka ya samu to da wuya a al'adun wasu }abilu su mamaye ko su yi tasiri a kan nasu.

### 2.3.2 Mujallu da Jaridu

Cikin jaridu da bincike ya gano na ]auke da bayanai kan tarihin Gbagyi akwai:

Guardian magazine (March, 20th 1986) –H.D. GUNN. "Pagan Peoples of the Central area of Northern Nigeria 1953". A wannan jarida an yi sharhi ne kan rayuwar al'umma arna da ke zaune a yankin arewa maso tsakiyar Nijeriya. Wa]annan mutane, a wannan zamani ba abin da suka fi mai da hankali a kai kamar tsafi wato, bautar gumaka da Iskoki. Wato a ta}aice tsafi da bautar gumaka da Iskoki shi ne addininsu na gargajiya, sai a shigowar Larabawa da Turawan mulkin mallaka ne aka samu shigowar sabbin addinai wato: Musulumci da Kiristanci.

Shekwo (1986), ya yi nazari ne a kan ‘Tarihin asalin Gbagyi’ da aka buga a mujallar Guardian, a ciki ya kawo yankuna da nahiyoyi da za a sami Gbagyi zaune da kuma bayanai a kan asalin harshen Gbagyi. Marubucin ya yi da’awar cewa al’ummar Gbagyi asalinsu daga daular Kanen Barno na da ne da aka gina a jihar Barno na yanzu. Ya ce: “Gbagyi sun taso ne daga Barno a shekara ta dubu ]aya da ]ari shida wato (1600 A.D.) sanadiyar jhadin addini da aka kai saboda kafircewarsu”.

Wa]annan su ne aikace-aikacen da suka gabata da bincike ya gano masu ala}a da wannan aiki ta kusa ko ta nesa, ana sa rai za su taimaka kwarai wajen tsara wannan aiki da ingancinsa.

## 2.4 Na]ewa

A wannan babi, an yi magana a kan waiwayen ayyukan da suka gabata da suka ha]a da litattafan da aka wallafa da ke da ala}a da wannan fage, haka kuma an dubi kundayen digiri na uku da na biyu da kuma na ]aya. A }arshe an waiwayi ma}alu da }asidu da aka gabatar a tarurrukan }ara wa juna sani ko aka buga cikin mujallun ilmi da jaridu da suka shafi wannan fage. Ayyukan da aka bibiya a wannan }udirin share fage sun taimaka sosai wajen gane inda aka fito da kuma inda ake da inda za a nufa. Burin wannan bincike shi ne ya samar da wani kundi da zai kasance madafa a wannan fage da kuma bayyana ire-iren kamanci da bambanci na borin al’ummun biyu da za a iya samu a wannan fage.

## BABI NA UKU: HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

### 3.0 Shimfi]a

Hanyoyin gudanar da bincike na da muhimmanci sosai a yayin da aka zo fagen nazari, saboda wa]annan hanyoyi su ne za su taimaka wa mai bincike wajen neman bayanai sahihai, su aza shi bisa turba mai kyau ba tare da ya kauce ba bisa yun}urinsa na tattara bayanai.

Wannan babi, yun}urinsa shi ne ya bayyana hanyoyi da aka bi wajen gudanar da bincike. Mai bincike ya kewaya cikin jihohin da Gbagyi ke zaune da ya ha]a da: jihohin Neja da Kaduna da sauran inda za a samu Gbagyi a zaune domin tattara bayanai a cimma nasarar gudanar da bincike.

Manufar wannan bincike ne ya gano borin Gbagyi kamar yadda suke aiwatarwa domin a kwatanta shi da na Hausawa. Domin samun sahihai ko ingantattun bayanai, wajibi ne a shirya yadda za a samu bayanai da ake bu}ata da kuma irin kayan amfani wajen tattara bayanai. A nan, }o}arin da aka yi shi ne, nuna kayayyakin amfani wajen tattara bayanai da kuma irin hanyoyin tattara bayanai da mai Bincike ya yi amfani da su.

### 3.1 Ganawa

Wata muhimmiyar hanya ta gudanar da bincike ita ce ganawa. Idan binciken na bu}atar

haka, wajibi ne a kai ziyara domin gudanar da tambayoyi da kuma hirarraki da masana bori na Hausa da na Gbagyi, a kuma nemi su nuna yadda ake aiwatar da borin domin ]aukan hoto na kati da ma na bidiyo, idan da dama, a na]o hirarrakin da aka yi da su a kasseti ko kuma wayar salula. Ganawa da masana harkar bori kai tsaye zai ba mai bincike haske da fa'idoji masu yawa, musamman da yake zai je, ya ji, ya kuma gani ma idanuwansa sahihan bayanai a kan batun da yake gudanar da bincike a kai, ya kuma ba shi dama ya tattara bayanai masu inganci ba tare ya ji daga wani daban ba ko kuma ya karanta a litattafai ba.

An yi amfani da dabarun tara bayanai kamar na ganawa da mutane, da yin tambayoyi da kuma nazarin yadda yake.

A dabara ta ganawa, manazarcin ya gana da wa]ansu shahararrun ‘yan bori har guda biyar kamar haka: Adamu na Kambari Kuta da Wasa Sarkin Bori Kuta da Musa Mai Bori Shagbah da Amina Ma’aji Bosso da Lamunko mai Bori Dutsen-Kura.

Ganawar da aka yi da wa]annan ‘yan bori ya taimaka wajen warware wasu matsaloli wa]anda suke da rikitarwa a game da sha’anin bori musamman na Gbagyi. Haka kuma mai binciken ya sami ganawa da ‘yan kallo wa]anda su ba ‘yan bori ba ne, sha’awa ce kawai ta kai su. Har ila yau, mai binciken ya sami ganawa da wa]ansu majinyata wa]anda aka kai su wurin ‘yan borin domin yi masu magani. Kana mai bincike ya samu ganawa da sauran jama’a domin samun ra’ayoyinsu a game da bori.

A dabarar yin amfani da tambayoyi, mai binciken ya yi amfani da tambayoyi wajen neman }arin bayanai dangane da wannan binciken. Mai binciken ya tsara tambayoyi a rubuce wa]anda ya rarraba wa mutane domin su cika, wato, su ba da amsa da kuma ra’ayoyinsu. Kodayake, an sami matsala ga wa]anda ba su yi karatu ba misali a garuruwan Gbagyi na Jihohin Neja da Kaduna. A irin wannan halin, mai binciken ya ri}a tambayarsu suna gaya masa amsa yana cikawa kamar yadda da za a ga misalan tambayoyin a rataye na biyu.

A dabara ta ganin zahirin abu kuwa, mai bincike ya je da kansa, a inda ake aiwatar da borin ya gani da idonsa }uru-}uru. Domin Bahaushe ya ce “Gani ya kori ji”. Wato dukkan abin da aka gani da ido }uru-}uru, ya fi a ce da kai, ai wane ne ya gaya maka!. Wato daga bakin wani ne ka ji. Don haka mai bincike ya ziyarci kusan dukkan fitattun gidaje da wuraren da ake aiwatar da wannan aiki na bori. Haka kuma, mai binciken bai tsaya ga gani da idanuwansa ba kawai, ya ma ]an shiga harkar aiwatar da borin. Saboda a duk lokacin da ake aikin girka, idan mai binciken ya tafi kallo da neman bayanai sai ya ]auki ]awainiyar rubuta sunayen Iskokin da ake zaunar da su a kan majinyata.

### 3.2 Sakamakon bincike ta dabarar yin amfani da tambayoyi

Sakamako ya nuna cewa cikin tambayoyi ]ari da aka raba wa jama'a domin su cika an samu ra'ayoyi mabambanta game da wa]ansu muhimman tambayoyi kamar haka:

1. A da can, Hausawa sun ]auki Bori a matsayin addini ne ko al'ada?
2. Akwai dangantaka tsakanin Hausawa da Gbagyi kafin zuwan addinin Musulumci ko sai bayan zuwan addinin?
3. Shin ana aiwatar da borin Gbagyi na asali a yau?
4. Idan ba haka ba, me ya haddasa sauyi?
5. Akwai kamanci a borin Hausawa da na Gbagyi ko babu?
6. Shin akwai bambanci a borin Hausawa da na Gbagyi ko babu?
7. Bayan shigowar addinin Musulumci da ma na Kirista, wasu al'ummun Hausawa da na Gbagyi sun daina bori ko har zuwa yau suna yi?
8. Bori na da muhimmanci ga al'umman Hausawa da na Gbagyi ko babu? Idan da shi,
9. Rubuta muhimmancin bori guda ]aya?
10. Mene ne rashin muhimmancin bori?

Dangane da tambaya ta farko, mutane tamanin cikin ]ari (80%) sun ce; addini. Saura ashirin, goma (10%) sun ce; Al'ada, sauran goma (10%) kuwa shiru suka yi, ba su ce komai ba. Kenan, wannan sakamakon ya nuna cewa jama'a sun fi amincewa da cewa bori tun da can a matsayin addini yake a wurin Hausawa kafin su kar~i addinin Musulumci.

Sakamakon tambaya ta biyu kuwa shi ne: Mutane casa'in da biyar (95%) sun ce bayan shigowar addinin Musulumci, saura mutane biyar (5%) kuwa ba su sani ba.

Tambaya ta uku da ta hu]u kuwa sun sami amincewar jama'a duka wato amsoshin mutane ]ari (100%) ya zama ]aya na cewa: ba a aiwatar da borin Gbagyi na asali a yau kuma bisa dalilin cu]anyarsu da Hausawa.

Tambaya ta biyar da ta shida a nan, sun sami amsa daga mutane casa'in da bakwai (97%) na amincewa da cewa: akwai kamanci da kuma bambanci a yadda ake aiwatar da borin Hausawa da na Gbagyi.

Tambaya ta bakwai ta sami yardan mutane duka wato (100%) sun amince cewa har ila yau duk shigowar addinan nan biyu wato: Musulumci da Kiristanci wasu Hausawa da Gbagyi ba su daina yin bori ba.

Dangane da tambaya ta takwas, mutane kashi hamsin (50/100) bisa ]ari sun amince cewa bori na da muhimmanci, saura kashi hamsin (50%) basu amince ba.

### 3.3 Ganawa ta Baka da Tattaunawa da Gbagyi da Wa]anda ba Gbagyi ba

Har ila yau a dabara na tattaunawa da jama'a, mai bincike ya gana da al'umman Gbagyi wa]anda suka yi karatu da wa]anda ba su yi ba. Binciken ya gano ra'ayoyi daban-daban a kan borin Gbagyi da dalilan da ya sa har wa yau suke aiwatar da shi.

A matsayin ]an kallo, mai binciken ya nuna ne shi bai san komai ba game da borin Gbagyi domin samun nasarar bincike. Binciken ya yi iyaka ne a za~a~~un garuruwan Gbagyi da ya ha]a da: Kuta da Minna da Suleja a jihar Neja da kuma garuruwan Gbagyi da ke jihar Kaduna inda har wa yau suna aiwatar borin Gbagyi.

Mai binciken ya na]i bayanai a kan borin Gbagyi har ma da hotuna domin kafa hujjar tabbatar da binciken. Da yake a yau duniyarmu ta ci gaba, ilimin fasaha ya }aru, an yi amfani da na'urorin zamani kamar Bidiyo da Kamera. Wato na'urar ]aukar hoto na kati.

Tambayoyin da aka gabatar sun ta'alla}a ne a kan: Wa? da Me? da Yaya? da Wanne? da Yaushe? da Wani lokaci? Wa]anda masu bayar da amsoshin suka bayar cikin sau}i, wasu a wuraren ayyukansu, wasu a kasuwanni, wasu a tashoshin mota, wasu a cikin motoci da dai sauran wurare.

A nan, yin amfani da wayar salula ko kuma wayar tafi da gidanka saboda ]aukar muryar wasu mutane a ~oye ya zama wajibi. Galibi masu amsa tambayoyin tsofaffi maza da mata ne da suka }i yarda a ]auki muryoyinsu. Haka kuma ya kasance cikin harshen Gbagyi suka yi magana. Daga baya aka zauna aka fassara zuwa Hausa.

A yun}urinsa na neman bayanai, mai binciken ya yi }o}arin sajewa da jama'a ta hanyar yin abota da su domin cire shakku ko tsoro a zukatansu, sannan suka bashi bayanan da yake bu}ata cikin ruwan sanyi.

A yayin ganawa ta baka, mai binciken ya fi mayar da hankali ne a kan tsofaffi maza da mata wa]anda ake zaton sun fi sanin yadda ake aiwatar da borin Gbagyi a da can da kuma yadda ake yi a yau. An kuma tattauna da manyan mutane maza da mata da kuma matasa da yara masu sama da shekaru ashirin, domin sanin ra'ayoyinsu.

An gabatar da tambayoyin ne a cikin tsari mai sau}i domin a gwada zurfin sanin masu amsawa, an kuma ba masu amsawa daman bayar da amsa ba tare da wata tsangwama ba. Ga misalai na irin wa]annan tambayoyin:

1. Mene ne sunan Bori da harshen Gbagyi?
2. A wani lokaci ake aiwatar da shi?
3. Wa ya kamata ya aiwatar da borin?
4. Me yasa?
5. Su wane ne ba su dace su aiwatar da borin ba?
6. Me yasa ba su dace ba?

7. Akan yi gadon bori ne ko haye?
8. Ta yaya ake zama ]an bori?
9. Wasu irin tufafi ne ]an bori ke amfani da su?
10. Borin Gbagyi kashi nawa ne?
11. Yaya ake aiwatar da su?
12. A ina ake aiwatar da su?
13. Tsawon zuwa wani lokaci ake aiwatar da borin?
14. Akwai tasiri na wani daga ciki ko daga waje da aka samu a kan borin Gbagyi? Idan akwai,
15. Su mene ne tasirin?
16. Me yasa suka yi wa borin Gbagyi tasiri?
17. Yaya yawan tasirin yake?
18. Borin Gbagyi na da wani amfani?
19. Fa]i ]aya daga cikin amfanin borin?
20. Mene ne gaba ]ayan ra'ayinka/ki a kan borin Gbagyi?
21. Ka/kin san wata }abila da ke aiwatar da bori irin na Gbagyi?
22. Bisa ra'ayinka/ki, yi sharhi a kan borin Gbagyi?

Al'umman Gbagyi ]ari biyar da sittin da uku (563) ne aka gana da su daga sassa daban-daban na }asashen Gbagyi. Cikin Gbagyin da aka gana da su, ]ari biyu (200) a jihohin Neja da Nasarawa da Babban Birnin Tarayya Abuja suke. Sauran kuma an gana da su ne a jihar Kaduna.

Cikin Gbagyin da aka gana da su, mutane ]ari uku da ashirin da biyar (325) duka sun yi karatun firamare ko sakandare ko gaba da haka. Arba'in da biyar (45) daga cikinsu, na da digiri na farko ko fiye. Wa]anda ke da ilimin gaba da sakandare kuwa, kamar N.C.E., su hamsin da uku (53) ne. Mutane tamanin da biyar (85) na da ilimin malanta na grade II ko na }are Sakandare. Mutane ]ari da biyu (102) kuma na da ilimin }are makarantar firamare.

A Birnin Gwari da Kujama da Bwari da wasu garuruwan da musulmai ke zaune, an samu mutane arba'in (40) da suka ba da amsan tambayoyin bincike, masu ilimin Ajami ko Arabiyya. Sauran mutane ]ari hu]u da talatin da hu]u (434) masu gwargwadon ilimin ya}i da jahilci ne ko kuma ma sam basu da ilimin Boko balle na Arabiyya. Ba su iya rubuta ko karanta harsunan Gbagyi ko Hausa ko Ajami ko kuma Arabiyya ba.

Daga cikin Gbagyi ]ari uku da ashirin da tara (329) masu ilimi, ]ari ]aya da casa'in da bakwai (197) mata ne, ]ari da talatin da biyu (132) maza ne. A kowane matsayi na zurfin ilimi, kuma masu shekaru tsakanin ashirin da saba'in (20-70 years).

Kuma daga cikin Gbagyi ]ari hu]u da talatin da hu]u (434) masu ilimin ya}i da jahilci da kuma wa]anda basu yi karatun ba sam-sam da aka gana da su, ]ari da ashirin da bakwai (127) maza ne, ]ari uku da bakwai (307) mata ne duk masu jerin shekaru tsakanin ashirin da saba'in (20-70 years).

**3.3.1 Jadawalai masu nuna adadin Gbagyi da aka gana da su, da shekarunsu da jinsunansu da kuma zurfin iliminsu.**

| | |
|---|---|
| Adadin wa]anda aka tambaya | = 763 (masu amsa tambayoyi) |
| Zurfin Ilimi | = Digiri na farko da ma fi haka (49)<br>= Ilimin gaba da sakandare (53)<br>= Grade II da Ilimin Sakandare (85)<br>= Ilimin firamare (102)<br>= Wa]anda suka iya harsunan Gbagyi da Hausa da Ajami da Arabic (40)<br>= Jimla = 329 |
| Shekaru | = Duka shekarunsu tsakanin ashirin da sittin da biyar |

| | |
|---|---|
| | (20 – 65 years) |
| Jinsi | = Maza =132<br>= Mata = 197<br>= Jimla = 329 |

**Gbagyi mara sa ilimi da suka amsa tambayoyi**

| | |
|---|---|
| Adadin wa]anda aka tambaya | = 434 (Masu amsa tambayoyi) |
| Zurfin ilimi | = Ba su yi karatu ba na kowane iri |
| Shekaru | = Duka Shekarunsu tsakanin Ashirin da Saba'in (20 – 70 years) |
| Jinsi | = Maza = 127<br>= Mata = 307<br>= Jimla = 434 |

**Jadawalin Gbagyi masu amsa tambayoyi a ta}aice**

| | |
|---|---|
| Jimlan adadin wa]anda suka amsa tambayoyi | = Masu ilimi =329<br>= Mara sa ilimi = 434<br>= Jimla = 763 |
| Shekaru | = Masu ilimi da Mara sa ilimi tsakanin Shekarunsu ashirin da saba'in (20 – 70 years) |

| | |
|---|---|
| Jinsi | = Maza = 259<br>= Mata = 504<br>= Jimla = 763 |

**Ganawa da tattaunawa da aka yi da wa]anda ba sa jin harshen Gbagyi a garuruwan: Kuta da Minna da Suleja da kuma Kudancin Kaduna.**

An gabatar da tambayoyi ga wa]anda ba sa jin Gbagyi a garuruwan Kuta da Minna da Suleja a Jihar Neja da garuruwan kudancin Jihar Kaduna domin a gwada zurfin saninsu game da borin Gbagyi ta yadda suke aiwatar da shi. Misalai na tambayoyin su ne kamar haka:

1. Yaya sunanka/ki?
2. Wace kabila ne kai/ke?
3. Ka/kin san da wani abu Borin Gbagyi?
4. Yaya ake kiran bori a harshen ka/ki?
5. Bori iri nawa kuke da shi?
6. Wasu irin mutane ke hawa bori a kabilar ka/ki?
7. Da wani lokaci ake hawa borin?
8. Tsawon wani lokaci yake ]auka?
9. A ta}aice, yaya ake aiwatar da borin?
10. Mene ne amfanin bori a kabilar ka/ki?
11. Akwai wani }arin bayani muhimmi a kan borin kabilar ka/ki?

An gana da mutane ]ari uku da tamanin da uku (383) wa]anda ba Gbagyi ba da suka ha]a da: Hausawa da Kadara da Koro da Nufe, a garuruwan Kuta da Minna da Suleja duk a cikin Jihar Neja. A kudancin Jihar Kaduna kuwa an gana da: Kagoro da Jaba da Chawai da Kataf da Kaje da kuma Kadara.

Daga cikin adadin da aka ambata a bisa, wa]anda ba Gbagyi ba, saba'in (70) Kagoro ne, hamsin (50) Nufe, talatin (30) Kadara, arba'in da biyar (45) Kaje, hamsin da ]aya (51) Kataf, sittin da biyar (65) Koro, arba'in (40) Jaba.

Cikin mutane ]ari uku da tamanin da uku (383) da aka tambaya, mutane ]ari biyu da saba'in da biyu (272) ne ke da ilimin firamare da na sakandare da abin da ya fi haka. Mutane arba'in tara (49) daga ciki kuma na da digiri. Mutane ]ari da ashirin da takwas (128) kuma suna da N.C.E. da Difloma, casa'in da biyar (95) na da ilimin malanta (Grade II) da na Sakandare.

Binciken ya gano mara sa ilimi a cikin kabilu goma da aka tambaya, guda ]ari biyu da sha ]aya (211). Daga cikin kabilun da ba sa jin Gbagyi, ]ari uku da tamanin da uku (383), ]ari ]aya da arba'in da shida (146) maza ne, ]ari biyu da talatin da bakwai (237) mata ne. Shekarunsu kuma tsakanin ashirin da saba'in (20 – 70 years)

**Ga jadawali da ke bayyana kowannensu**

Masu ilimi wa]anda ba sa jin Gbagyi:

| | |
|---|---|
| Adadi | = 383 |
| Zurfin ilimi | = Digiri na farko zuwa abin da fi haka (49)<br>= N.C.E., Difloma (128)<br>= Grade II da ilimin Sakandare (95)<br>= Jimla = 298 |
| Shekaru | = Duka tsakanin ashirin da sittin (20 – 60 years) |
| Jinsi | = Maza = 146<br>= Mata = 237<br>= Jimla = 383 |

**Jadawalin mara sa ilimi kuma wa]anda ba sa jin Gbagyi**

| | |
|---|---|
| Adadi | = 111 |
| Zurfin ilimi | = Ba su da kowanne |
| Shekaru | = Duka tsakanin ashirin da biyar da saba'in (25 – 70 years) |
| Jinsi | = Maza = 62<br>= Mata = 49<br>= Jimla = 111 |

**Jadawalin wa]anda ba su ji harshen Gbagyi ba a ta}aice**

| | |
|---|---|
| Adadi | = masu ilimi = 272<br>= mara sa ilimi = 111<br>= Jimla = 383 |
| Zurfin ilimi | = masu ilimi = 272<br>= mara sa ilimi = 111<br>= Jimla = 383 |
| Shekaru | = masu ilimi da mara sa ilimi, tsakanin shekaru ashirin da biyar da saba'in (25 – 70 years) |
| Jinsi | = Maza = 146<br>= Mata = 237<br>= Jimla = 383 |

**Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba**

Mutane dubu ]aya da ]ari ]aya da arba'in da hu]u (1144) daga cikin Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba aka gana da su.

Daga cikin adadin Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba da aka gana da su, mutane ]ari biyar da casa'in da tara (599) masu ilimi ne da suka mallaki a}alla ilimin Firamare ko Sakandare zuwa abin da fi haka, da kuma ilimin Arabiyya ka]an.

Mutane casa'in da takwas (98) daga cikin mutane ]ari biyar da casa'in da tara (599) jimlar adadin gaba ]ayan masu ilimi, suna da digiri na faarko da abin da fi haka. Mutane ]ari da tamanin da ]aya (181) sun sami ilimin gaba da na Sakandare wato N.C.E. da Difloma. Mutane ]ari da saba'in da takwas daga cikinsu suna da ilimin na malanta wato (Grade II) ko na Sakandare. Mutane ]ari da biyu (102) suna da ilimin Firamare, mutane arba'in (40) suna da ilimin Arabiyya.

Daga cikin Gbagyi masu ilimi da wasu }abilu ]ari biyar da casa'in da tara (599) a Jihar Kaduna, suna da ilimin Firamare ko na Sakandare zuwa abin da ya fi haka. Suna kuma da sani ka]an na ilimin Arabiyya, ]ari biyu da hamsin da tara (259) maza ne, ]ari uku da arba'in (340) mata ne. Kuma suna da Jerin Shekaru tsakanin ashirin da saba'in (20 – 70 years)

A nan, jadawali ne da ke nuna adadin Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba da aka gana da su tare zurfin iliminsu da shekarunsu da kuma jinsinsu.

**Jadawalin Gbagyi da na wa]anda ba Gbagyi ba a ta}aice**

| | |
|---|---|
| Adadi | = 599 |
| Zurfin ilimi | = Digiri na farko da abin da ya fi haka (98)<br>= Ilimin gaba da Sakandare (181) |

| | |
|---|---|
| | = Grade II ko ilimin Sakandare (178)<br>= Ilimin Firamare (102)<br>= masu jin Gbagyi da Hausa da Ajami da Arabiyya (40)<br>= Jimla = 599 |
| Shekaru | Tsakanin ashirin da saba'in (20 – 70 years) |
| Jinsi | = Maza=259<br>= Mata =340<br>= Jimla = 599 |

**Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba, da masu ilimin ya}i da jahilci, da wa]anda ba su da ilimi.**

An gana da Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba su dubu ]aya da ]ari ]aya da arba'in da hu]u (1144).

Daga cikin wannan adadi na sama da aka gana da su, ]ari biyar da arba'in (545) mara sa ilimi ne kuma ba su da ilimi na kowane. Mutane ]ari ]aya da casa'in da takwas (198), masu ilimin ya}i da jahilci ne (Sun ]an iya rubuta da karanta Hausa ko Ajami). [ari biyu da arba'in (240) daga cikinsu maza ne, ]ari uku da biyar (305) mata, dukansu masu shekaru tsakanin ashirin da sittin da biyar (20 – 65 years)

**Wannan Jadawali ne yana nuna adadin Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba, da kuma masu ilimin ya}i da jahilci da mara sa ilimi sam da aka gana da su tare da zurfin iliminsu, da shekarunsu, da kuma jinsinsu.**

| | |
|---|---|
| Adadin masu ilimin ya}id a jahilci da na mara sa ilimi | = 545 |
| Zurfin ilimi | = Ba su da ilimi na kowane iri<br>= Jimla = 545 |

| | |
|---|---|
| Shekaru | = Dukansu tsakanin shekaru ashirin da sittin da biyar (20 – 65 years) |
| Jinsi | = Maza = 240<br>= Mata = 305<br>= Jimla = 545 |

Gaba ]ayan jimla na Gbagyi da na wa]anda ba Gbagyi ba, da aka gana da su shi ne, dubu ]aya da ]ari ]aya da arba'in da hu]u (1144).

Gaba ]ayan jimla da adadin wa]anda ke da ilimi ]ari biyar da casa'in da tara (599). Gaba ]ayan jimla na adadin wa]anda suke da ilimin ya}i da jahilci da na mara sa ilimi shi ne ]ari biyar da arba'in da biyar (545). [ari hu]u da casa'in da tara (499) maza ne, ]ari shida da arba'in da biyar (645) mata ne. Shekarunsu tsakanin ashirin da saba'in (20 – 70 years).

**Jadawali na gaba ]ayan Gbagyi da wa]anda ba Gbagyi ba (masu ilimi da mara sa ilimi)**

| | |
|---|---|
| Adadi | = masu ilimi = 599<br>= masu ilimin ya}i da jahilci da mara sa ilimi = 545<br>= Jimla = 1144 |
| Shekaru | = Dukansu shekarunsu tsakanin ashirin da biyar da saba'in (25 – 70 years) |
| Jinsi | = Maza = 499<br>= Mata = 645<br>= Jimla = 1144 |

### 3.4 Matsalolin da aka fuskanta wajen tattara bayanai

A yayin yawon tattara bayanai, mai bincike ya fuskanci matsaloli kamar haka:

1. Rashin samu ko cin karo da wani littafi ko mujalla ko kundin bincike ko jarida ko }asida ko mu}ala da ya yi magana kai tsaye a kan borin Gbagyi.
2. Mai bincike ya rasa ganin wani aiki da ya gabata da aka yi takamaimai a kan borin Gbagyi. Yawanci ayyukan da aka yi, a kan tarihi ne da kuma harshe. Ka]an kuma da aka yi a kan al'adu, ba su da ala}a da borin Gbagyi.
3. Rashin hanyoyin shiga wasu garuruwa da }auyukan Gbagyi saboda rafuka da koguna musamman cikin damina, ya ]an jinkirta binciken.
4. Mai bincike ya fuskanci rashin ji ko iya wasu harasa na kudancin Kaduna da na wasu garuruwan Jihar Neja inda har wa yau suna aiwatar borin Gbagyi kuma su ba sa jin Turanci balle Hausa. Saboda haka, dole ya sa aka nemi masu fassara domin fahimtar bayanansu.

### 3.5 [akunan Karatu

An ziyarci ]akunan karatu inda aka ajiye litattafai da kundayen digiri da ma}alu da mujallu da }asidu da kuma jaridu domin neman ingantattun bayanai masu ala}a kai-tsaye ko a fakaice da wannan fage da ake nazari a kai. Domin wajibi ne ga duk wani mai bincike ya ziyarci ]akunan karatu na sassa ko na tsangayu ko na makarantu, saboda a nan ne zai sami bayanan da yake bu}ata. Saboda haka ]akunan karatu sun taimaka wajen samun bayanai a kan batu da ake gudanar da bincike a kai.

### 3.6 Yanar Gizo

Yanar Gizo a yau, yana kan gaba a matsayin sahihiyar hanya ta neman bayanai da suka ji~anci al'amuran rayuwa daban-daban da masana suka ~ata dare suka bayyana ra'ayoyinsu a kan batutuwa daban-daban aka ajiye a Yanar-Gizo domin a karanta. Wannan zai taimaka wa masu

nazari ko bincike ta kowane fanni su sami bayanai ingantattu domin bun}asa nasu binciken. Haka ma wannan binciken ba a bar shi a baya ba, domin amfani da Yanar-Gizo ya taimaka wajen bun}asa binciken da bayanai ingantattu.

### 3.7 Na]ewa

A wannan babin, an yi amfani da dabaru daban-daban kamar na ganawa kai-tsaye da yin tambayoyi tare da sakamakon wasu daga cikin tambayoyin, da dabarar ziyara don gani da ido }uru-}uru, sai kuma ziyartar ]akunan karatu da shiga Yanar-Gizo. Wa]annan hanyoyi na bincike da aka zayyana an dube su, an tattaro bayanai da suka shafi fagen nan na bincike, daga }arshe aka yi zaman dirshan domin nazarta da na}altar wa]annan bayanai da aka kalato, aka fe]e, aka kuma tace su domin fito da ha}i}anin abin da aka kira kwatancin borin Hausawa da na Gbagyi. Wato, wa]anan hanyoyin tattara bayanai da mai bincike ya bi, ko da yake ba su wadatar ba sosai kamar yadda aka bu}ata kwarai da aniya, saboda wasu matsaloli da aka fuskanta kamar: rashin iya rubutu da karatu ko kuma rashin ilimi na wa]ansu Gbagyi da aka gabatarwa tambayoyi a rubuce da kuma }arancin nazarce-nazarce a kan borin Gbagyi, a nan, zai kyautu al'umman Gbagyi su tashi tsaye tsayin daka su nemi iya karatu da rubutu ko da na ya}i-da-jahilci ne, kuma a }ara }aimi wajen yun}urin nazarce-nazarce a kan borin Gbagyi. Yin haka, shi ne zai samar da sahihai kuma ingantattu har ila yau, wadatattun bayanai da hanyoyin tattara bayanai nan gaba. Duk da haka, wa]annan hanyoyi, sun yi rawar gani wajen taimaka a tantance ayyukan da wasu suka yi da bayanan da jama'a suka bayar, wanda kuma ya ba mai bincike }warin gwiwa wajen ]aukan matsayi.

## BABI NA HU[U: KWATANCIN BORIN HAUSAWA DA NA GBAGYI

### 4.0. Shimfi]a:

A wannan babin, za a kwatanta borin Hausawa da na Gbagyi domin gano kamanci da bambancinsu ta fannonin da suka ha]a da: sunayen Iskoki/Aljannu, da halayen 'yan bori (Iskoki) na

Hausawa da na Gbagyi. Haka kuma, za a dubi yanayin tufafinsu, da girka da kayan ki]a. Sai kuma a dubi amfanin ‘yan borin da ya ha]a da: gano cuta da magani da warkarwa da kuma tsari daga cutarwar mutane da aljannu.

### 4.1 Kwatancin Borin Hausawa da na Gbagyi

Neman ci gaban al’ummar Gbagyi, shi ne ya yi sanadiyyar cu]anya da Hausawa wurin tafiyar da harkokinta, saboda haka ne aka samu al’adun Hausawa sun yi tasiri a kan na Gbagyi ta ~angarori da yawa, musamman Bori da ake gudanar da bincike a kai.

Babu yadda za a kwatanta borin Hausawa da na Gbagyi ba tare da an yi magana a kan zuwan Musulunci ba a }asar Hausa. Da yake da can ]aya daga cikin hanyoyin addinin gargajiya na Hausa ita ce “Bori”, watau bautan Iskoki. Sun fara ta ne tun lokacin da suke duk Maguzawa kuma har wa yau da kusan dukkaninsu Musulmi ne wasun su ba su daina ba. Saboda haka, Hausawa sun sadu da Gbagyi ne bayan sun kar~i Musulunci imani da Bori ya fara raunana.

Kamar yadda Bunza (2006:7) ya ce:

> Abin ban sha’awa da wuya Iska ya hau kan wani ko wata a }asar Hausa a ce, Bayarben Iska ne, ko Inyamuri, ko Banufe, ko Batangale, ko Bagware, ko Babarbare, da dai makamantansu. Wa]annan }abilu da makamantansu Hausawa sun sadu da su bayan sun kar~i Musulunci imani da Bori ya fara raunana.

Idan za a yi la’akari da wannan zance na Bunza da ke bisa, ha]uwar Hausawa da Gbagyi har borinsu ya yi tasiri a kan na Gbagyi, bai faru ba sai bayan da Hausawan suka Musulunta kuma ka]an daga cikinsu ne ke gudanar da harkar bori.

Da yake tun asali al’ummar Gbagyi addininsu tsafi ne wanda ya ha]a da bautar gumaka da Iskoki, ba su }ar~i addinin Musulunci ba sai bayan jihadin Usman [anfodiyo }arni na sha takwas (}.18) zuwa na sha tara (}.19) bayan Hausawa sun Musulumta suna ya]a addinin Musulumci har

suka shigo }asashen Gbagyi musamman a zamanin Sardaunan Sakkwato Mai Martaba Sir, Ahmadu Bello, bayan imani da Bori ya raunana, amma saboda tsananin imanin da suke da shi na amincewa da akwai Iskoki, wasu daga cikin Hausawan ba su bar harkar bori ba, sun ci gaba da yinsa a matsayin hanyar neman abinci da taimakon jama'a da suka kamu da cuce-cucen Iskoki.

Bunza (2006:29) ya }ara bayar da hasken wannan batu na bisa inda ya ce:

> *"Babu shakka, duk wata al'ada da aka share }arnuka ana yi, barin ta na da wuya sosai, kuma ko an dangane ta, an yi ban kwana da ita, nasonta zai ci gaba da bayyana a ]abi'u, da ayyukan ma'abotanta. Tarihi ya bayyana, tun kafa }asar Hausa Bahaushe cikin hul]a da Iskokin }asar Hausa yake fararensu, da ba}a}ensu, domin biyan bu}atarsa ta rayuwa daban-daban".*

Hausawa sun ce "zama da ma]aukin kanwa shi ke kawo farin kai", saboda haka cu]anya da Hausawa suka yi da Gbagyi da kuma ganin yadda Hausawa 'yan bori suka shigo da bori kuma suke aiwatarwa a }asashensu, sai wasu daga cikin Gbagyi suka yi sha'awa, a hankali suna kwaikwayon na Hausawa har ga shi a yau nasu na asali ya sauya musamman a cikin garuruwa da biranen Gbagyi. A yau al'ummar Gbagyi duk da yake yawancinsu sun rungumi addinin Musulumci da na Kirista, ka]an da ke aiwatar da bori, suna yi ne garwaye da salon na Hausawa.

Tun lokacin da Gbagyi suka sha}u da Hausawa, Sarakunansu ne aka fara Musuluntarwa. Misali, a zamanin Sardaunan Sakkwato, Mai Martaba Sir, Ahmadu Bello, da ya kawo ziyara }asar Gbagyi ya Musulumtar da Sarakuna da yawa har da }asar Kuta, ya kuma taho da malaman addinin Musulunci ya zaunar da su a kowani gari saboda su koya ma jama'a addini. Saboda haka, a zamanin Sarki Ahmadu Bahago sai ya umurci dukkan ilahirin matsafa ko bautar gumaka da Iskoki da su daina, ya sa aka tattara wasu gumakan aka }ona, wasu itatuwa da duwatsu da aka gaskata akwai Iskoki ana bauta masu a wannan lokaci duk sai aka tarwatsa su, wasu aka }ona. Sannan ya umurci jama'ar }asar su shiga addinin Musulumci su koma bauta ma Allah (S.W.T.) shi ka]ai, ya kuma

gina masallatai a yankinsa. Sardaunan Sakkwato Sir, Ahmadu Bello shi ne ya kafa harsashin tushen tubalin ginin masallacin Juma'a a garin Kuta a shekara ta 1964. A wannan lokaci ne wani mawa}i mai suna Ali [an Saraki ya rera wata wa}a yana fa]in:

"Duk arnan Kuta sai Sallah suke,
don darajar Ahmadu Bello ne,
mai Ministoci da Sarakuna".

A sanadiyyar ha~~akar addinin Musulumci a }asar Gbagyi, jama'a da dama sun Musulumta musamman a cikin manyan biranen Gbagyi kamar; Kuta da Minna da Suleja (Abuja a da) da Birnin Gwari, amma har wa yau a cikin yawancin }auyukansu ba a bar bautar Iskoki ba sai dai suna yi ne a bisa salon yadda suka ga Hausawa na yi. Domin idan aka yi la'akari za a ga cewa sunayen Iskoki ko aljannu da kayan ki]a da tufafi da kayayyaki da yanayin girka na 'yan borin Gbagyi a yau duk ]aya ne da na Haussawa, sun yi watsi da nasu na aslali sai dai abin da ba za a rasa ba a cikin }auyukan Gbagyi, yana iya yuwuwa a samu wasu na kamanta na asali.

### 4.1.1 Sunayen Iskoki/Aljannu

Iskoki ko Aljannu wasu ~oyayyun halittu ne masu halaye da ]abi'u daban-daban. Bisa al'ada Hausawa sun ]auka bayan mutane wa]anda ake hul]a da su ta yau da gobe, duniya tana }unshe da wasu ~oyayyun mutane wa]anda ba kowa da kowa zai iya ganin su ya zauna lafiya ba. Iskoki ko Aljannu su ne ake kira 'mutanen ~oye'. [an Adam ba ya ganin Iskoki (mutanen ~oye) amma su suna ganin sa, kuma suna iya shiga ko'ina, kuma suna iya bin ta ko'ina suke bu}ata. Iskoki suna zaune a wurare daban-daban, an ]auka irin wa]annan wurare na zamansu suna }unshe da }wa}wamai da suka samu a dalilin Iskokin. Iskoki ko Aljannu an ]auka suna iya riki]a zuwa siffofi da kamannu da halaye iri-iri, wani lokaci sukan fito a siffar mutane ko dabbobi ko su zama macizai ko su zama iska irin na guguwa su tashi sama ko su shiga cikin jikin ]an Adam da sauransu. Haka kuma Hausawa na da'awar cewa mutanen ~oye suna da wata mallaka ko wani iko a kan

mutane, suna iya yi musu duk abin da suke so, musamman ga shi ba su ganin su. Ashe ke nan suna iya cutar da mutane ko su yi musu wani aibi, ko ma su sabartar da ransu ko su taimake su ta ba su magani ko su warkar da su daga abubuwan da ke damun su.

Kamar yadda ake fa]i, Iskoki suna da yawa matu}a, wani }aulin ma an ce har sun fi mutane yawa a bayan }asa, sannan ga su da tsawon rai, a kullum haihuwa suke yi, sannan ba su saurin mutuwa, sukan yi ]aruruwan shekaru a duniya. Masu ilmin mutanen ~oye suna cewa Iskoki suna warwatse a ko'ina cikin uwa duniya, suna da wuraren zama mabambanta, amma wai suna da babban birni da ake kira Birnin Jangare. A wannan gari ne suke da Sarkin Iskoki (aljannu) da Wazirin Iskoki da Galadima da Madaki da Sarkin Ki]a da Majida]i da sauran mu}amai.

Akwai Iskoki farare wa]anda suke taimakon mutane, sannan da ba}a}e masu cutar 'yan Adam ta hanyar cusa musu rashin lafiya iri-iri. Haka kuma akwai Iskoki da ke yin abota da mutane, wani lokaci har su dinga gaya musu magungunan cuce-cuce da 'yan'uwan su Iskoki ke cusa wa mutane ko wani sammu da aka yi wa wani mutum da sauran hanyoyin warkar da cututtuka. Ibrahim da wasu, (1992:88). Haka zalika, Gbagyi ma sun tabbatar kuma sun yarda da wa]annan bayanai da suka gabata.

Bunza, (2006:2) ya ce: A al'adar Bahaushe, akwai wasu abubuwa da ake son a ~oye sunansu na asali a furta wani daban da ake iya ganewa. Sunayen Iskoki na daga cikin wa]annan abubuwa da ake yi wa lullu~i. A }asar Hausa, sunayen Iskoki an kasa su zuwa kashi biyu, na gargajiya da aka taras tun gabanin saduwa da Larabawa da wa]anda aka samu bayan saduwa da Larabawa. Yanzu bari mu dubi rukuni na farko na sunayen da aka samu na gargajiya tun gabanin saduwa da Larabawa ('yan kasuwa da masu ya]a addini). Daga cikin sunayen akwai:

i. Iska
ii. Mutantani
iii. Mutanen ~oye
iv. Mutanen kogo

v. Kayehi
vi. {wan}wanmai/{wan}wamai
vii. Masu abu
viii. Suwa

Daga cikin wa]annan sunaye na Iska, shahararre shi ne ‘Iska’. Manazarta al’ada suna ganin dalilan da suka sa Bahaushe ke ce musu ‘Iska’ suna da yawa. Daga cikin dalilin akwai:

a. Kasancewar su kamar Iska ba a ganin su.
b. Kasancewar su ba su da jiki irin na jinni da tsoka.
c. Kasancewar su kamar Iska ana jin su a jiki ba tare da an gan su ba.
d. Kasancewar su halittun da ba su tare wuri kamar Iska.
e. Kasancewar su masu }arfin gaske irin Iska.
f. Kasancewar su sanadiyar ha]a guguwa da Iska.
g. Kasancewar su masu shiga jiki kamar yadda Iska ke yi.
h. Kasancewar su masu tsananin sauri irin Iska.
i. Kasancewar su ana samun su ko’ina kamar Iska.
j. Kasancewar su masu yawan shawagi/jewa]i irin Iska.

A nan, marubucin ya bayyana cewa abubuwan nan goma da Bahaushe ke kwatanta Iskoki da su shi ya sa yake kiran su ‘Iska’. Sauran sunaye kuwa ‘yan rakiya ne ba a cika amfani da su kamar yadda ake amfani da sunan ‘Iska’ ba. Duk da haka, kowane allazi da nasa amanu, Hausawa na da dalilin kiran kowane suna da sunan da aka kira shi. Sannan sunayen gargajiya da aka ambata ba su rasa ala}a da abubuwa kamar haka:

**i.** **Mutantani:** Wai sun yi kama da mutane amma ba mutane ba ne, don haka aka ciro su daga ‘mutum’ ya koma ‘mutantani’ kamar mutum ba mutum ba.

**ii.** **Mutanen ~oye:** An ce wai, asalinsu mutane ne amma aka ~oye su ga barin ganin mutane domin a razana mutane idan suna son su yi fitina ko wuce gona da iri. A koyaushe muna tare da su, su suna ganin mu, amma mu ba mu ganin su. Don haka ake kiransu mutanen ~oye.

**iii.** **Mutanen Kogo:** Wai a tarihin Bahaushe a riwayar bokayen }asar Hausa, lokacin da Annabi Adamu (AS) ya haifi ‘ya’ya Allah Ya nemi ya zo da su wani wuri a gan su. Gabanin ya isa wurin ya za~e masu kyau mata da maza ya ~oye cikin kogon Tsamiya ko Kuka. Da ya isa da sauran ya nuna. Ya dawo ya ]auki wa]anda ya aje a Kogo ya tarar sun zama “Iskoki”. Ya bar su nan a kogo ya tafi abin sa, don haka ake

ce musu Mutanen Kogo.

iv. **Kayehi:** Tsofaffi da suka }ware da sanin halin Iska da ayyukansu da ‘yan Bori, da masu Tsafi, su suka fi amfani da wannan sunan. Kayehi na nufin buwayayye, mai aikin al’ajabi, da ban mamaki, da buwaya, da ya sa~a wa al’ada, da abin da hankalin tuwo ke iya hasashe. Daga cikin abubuwan da ya sa ake kiran su Kayehi akwai tashi sama, da sauri, da }arfinsu, da buwayar ]an Adam da suka yi.

v. **{wan}wanmai:** Bahaushe na ce wa Iska {wan}wanmai saboda dalilai biyu. Na farko cikin }wan}wamin }wa}walwa suke shiga su gigita mai hankali. Na biyu, ba za a kira su da wannan suna ba face idan gadon su aka yi daga iyaye (musamman wajen uba).

Vi. **Masu abu:** Wannan sunan yana nuna isa ne ga Iskoki a kan komai suka sa gaba za su

yi, za su yi shi kamar }yaftawar gira yadda suke son a gan shi kai tsaye nan take, Sha yanzu magani yanzu. Wa zai iya wannan in ba masu abu ba?

vii. **Suwa:** ‘Yan Bori da matsafan da suka kai matu}a ga bauta wa ‘Iska’ ba su ambaton sunayen can bakwai domin tsananin girmamawa da biyayya ga Iska sai dai su ce, “suwa”. Suna haka ne wai gudun kar su ambaci sunan da zai sosa musu rayuwa su yi ~anna ko su yi hushi da su, ta yadda idan aka neme su wata bu}ata su }iya. Da zarar an ce “suwa” wanda ya yarda da su ya san su wane ne ake zance a kan su.

Akwai kuma sunayen da zamani ya haifar su ne sunayen da suka yi fice saboda tasirin ba}in al’adu cikin gargajiyar Bahaushe. Dukka sunayen an same su ne bayan cu]anyar Hausawa da Larabawa ‘yan kasuwa da masu ya]a Musulunci. Larabawa ‘yan kasuwa su suka fara ziyartar }asar Hausa don cinikin bayi, da hauren giwa da sauransu. Tun kafin Musulunci ya bayyana gare su suna bai wa Iskoki muhimmanci. Sun yi imani da su, da Musulunci ya zo ya }ara tabbatar mu su da imaninsu. Daga cikin sunayen su ne:

i. **Aljani:** Daga Kalmar Larabci ‘aljinnu’

ii. **Jinnu:** Kai tsaye daga Kalmar “jinnu”

iii. **Iblishi:** Daga sunan Shai]an ‘Iblis’, uban aljanu.

iv. **Rauhani:** Sunan da ma'abota tsibbu ke yi masa. An samo shi daga kalmar Larabci ta "ruh".

v. **Ira'izai:** Sunan ya samo asali daga harshen Larabci ne.

Wa]annan sunayen sun yi fice bayan bayyanar Musulunci zuwa yau a bakunan Hausawan }asar Hausa. Kowane suna daga cikin na gargajiya ko na zamani Bahaushe na amfani da shi.

**Akwai kuma sunayen fitattun Iskoki kamar haka:**

Kafin bayyanar Musulunci a }asar Hausa Iskoki tamkar 'yan uwan mutane ne ta fuskar hul]a da bauta. Sunayensu sanannu ne fitattu ga kowane Bahaushe sai dai Bahaushe ya fi ganin wasu daga cikin su sun fi shahara fiye da wasu ga sunayensu da ayyukkansu. Daga cikin sunayen Iskoki da suka yi fice }warai , da buwaya, da girmamawa ga Bahaushe akwai:

i. **[antsatsumbe:** Gajere ne takadari, da jan fa]a, da son wasan kokuwa da mutane.

ii. **Doguwa:** Sananniyar Iska ce mai ban tsoro da firgita mutane.

iii. **Inna:** Ita ce uwar Iskoki duka, don haka ake jin tsoron ta. Tana haddasa cutuka da yawa.

iv. **Hajon Ruwa:** A kogi aka fi samun ta da tsakar rana ko dare. Ta sha wahalar da masunta.

v. **Julukukuwa:** Sananniyar Iska ce , ko'ina ana samun ta.

vi. **Jinnakaji:** Sananniyar Iska ce, ko'ina ana samunta, da ita 'yan dabo ke }arya.

vii. **Tsurut-Tsurut:** A masussuki take zama, ana yi mata kirari da, "Iskokin masussuki kashe mai koda" (sana'ar sussska).

viii. **Gungungun:** Iskan ma'abota tsafe-tsafe ne, da shi ake samun nasarar maganin gaba.

ix. **Najabilo:** Iska ne mai }arfin gaske, kuma shi ke haddasa cutar hauka, da ragaita, a dambale, a lalace.

x. **Jitakuku:** Manyan Iskokin kogi ne, su ne ke buwayar Kabawa a gurbi idan ana kamun kifi.

xi. **[andanguna:** An ce gajere ne }warai shi ne uban Iskoki kamar yadda Inna take zama uwa gare su.

xii. **Atakurma:** {aramin Iska ne kuma gajere }warai da bai cika cutarwa ba, ya fi son wasa da ‘yan yara da mata.

**Ga wani rukuni na sunayen {abilu Iskoki:**

Kamar yadda ‘yan Adam suke dangi-dangi haka Bahaushe ya yi imanin cewa Iskoki Suke. Abin ban sha’awa shi ne, Bahaushe ya aminta da }abilun Iskoki dangi-dangi amma ba dukkanin }abilun ake samu a }asar Hausa ba. {abilun Iskokin da aka fi sani da sabawa da su a }asar Hausa su ne;

i. Bature
ii. Balarabe
iii. Bafulatani
iv. Ba’adare

Ba abin mamaki ba ne samun Iskoki na wa]annan }abilu cikin Iskokin }asar Hausa. Dalili na farko shi ne, wa]annan }abilun sun fi kowace }abila hul]a da Bahaushe tun kafin saduwarsa da addinin Musulunci. Turawan mishon, da ‘yan ciniki bayi sun da]e a }asar Hausa da ba}ar anniyarsu Bugu da }ari, ga mulkin mallaka da Ingila ta yi wa }asar. Wa]annan duk dalilai ne na samun ba}in Iskokin Turai su biyo Turawa zuwa }asar Hausa. Hul]ar Bahaushe da Bature ita ce ta farkon hul]ar Bahaushe da wata jar fata a doron }asa. Larabawa masu cinikin bayi daga Morocco, da Misra, da Libya, da Tunis, su ne na biyu. Bayan rusa haramtacciyar sana’ar bayi a }asashen duniya, sai Larabawa masu ya]a addinin Musulunci suka bayyana. Dukkanin wa]annan sun yi hul]a mai tsawo da Bahaushe wadda ke haddasa tasirin Iskokin }asar Larabawa ya shiga ga Iskokin }asar Hausa. Hausawan

wancan lokaci suna jin Turanci, da Larabci, don haka Iskokin Turawa, da Larabawa, dole su hau kan su, kamar yadda suke hawa na Turawa da Larabawa.

Haka kuma hul]ar Bafulatani da Bahaushe, hul]a ce tsakanin makiyayi da manomi. Duk wata }abila da ta zo }asar Hausa ta tarar da Fulani da Hausawa tare, musamman Fulanin Soro (Fulanin Zaure/gida), da Rahazawa, da Gudalawa. Auratayya tsakaninsu da]a]]iya ce. Ba abin mamaki ba ne, a samu Iskoki Fulani sun hau kan Bahaushe, kamar yadda za a samu Hausawan Iskokin sun hau kan Fulani. Adarawa kuwa, su ne manyan ma}wabtan }asar Hausa, kuma masu kawo mata ziyara a kai a kai. Tsakanin Adarawa da Hausawa akwai hul]ar aure, da kasuwanci, da ta addinin gargajiya, mai yawa kafin bayyanar Musulunci. Iskokin }asar Adar sun mayar da }asar Gobir, da Kabi, kamar }asarsu. Hausawan wannan yanki sukan sha samun Adarawan Iskoki su hau kansa, kamar yadda Bahaushen Iska kan hawa kan Ba'adare.

Abin ban sha'awa da wuya Iska ya hau kan wani ko wata a }asar Hausa a ce, Bayarben Iska ne, ko Inyamuri, ko Banufe, ko Batangale, ko Bagware, ko Babarbare, da dai makamantansu. Wa]annan }abilu da makamantansu Hausawa sun sadu da su bayan sun kar~i Musulunci Imani da Bori ya fara raunana.

**Sai kuma sunayen Iskoki na [abi'u da Halayya:**

Sunayen Iskoki na }asar Hausa da ke da ala}a da sunayen 'yan Adam yawa gare su kamar yadda sunayen 'yan Adam ke da yawa. Sunayen nasu sun ha]a da sakakkun sunaye irin na sauran mutane, da kuma sunayen sarauta, da sunayen sana'a, da na ]abi'u (irin su kwarto ko maye), da dai makamantansu. Ga ka]an daga cikin su kamar yadda manazarta suke kallon su:

| **Suna** | **Asalin Wurin da aka ciro shi** |
|---|---|
| a. Kure<br>b. Ba}o<br>c. Gajimari | Fitattun la}abai ne ake yin amfani da su a }asar Hausa. |

d. Bahago
e. Duna
f. Gajere
} La}abin daga sifar Iskokin aka samo su.

g. Wanzam
h. Sakke
i. Magina
} Daga sana'o'in }asar Hausa aka samo wa]annan sunaye kamar yadda ake kiran masu sana'ar a gargajiya.

j. Sarkin Maka]a
k. Sarkin Rahi
l. Sarkin Aski
} Sunayen sarautun sana'o'in gargajiya ne da ake samu a }asar Hausa.

m. Sarkin Fawa
n. Nana A'isha
o. Nana Kadija
p. Malam Alhaji
} Tasirin Musulunci ya haifar da wa]annan sunaye. An samo su daga Moroko da Tunis da Misra.

q. Ifritu
r. Haruta
s. Maruta
} Alkur'ani ya ambaci wa]annan Iskoki a kulkin ba}i.

Bunza (2006:1-8).

Hira da Musa mai bori Shagbah (30/072011) ya ce: Kafin ha]uwar 'yan borin Gbagyi da 'yan borin Hausawa, ba su san sunayen Iskoki kamar yadda Hausawa ke kiransu a yau ba, sai dai da harshensu suna kiransu 'Aguzheyin' ko 'Anuwada' kuma sunayen sun danganci irin halin da 'yar bori ta nuna ne a lokacin da ta hau. Misali idan borin 'Gbemu' ne ta hau za a ga yatsun 'yar bori na }wankwandarewa, idanunta su jujjuye kamar na kuturun Iska wanda ake kira 'Kutulu aguzheyin' da harshen Gbagyi ta haka za a gane cewa Iskan da ya hau kan ta kuturu ne, idan kuma borin 'Madawa' ne zai hau aka ga 'yar bori na kuka tana magana da Filatanci ko Turanci sai a ce 'Ogo aguzheyin' ko 'Nisala aguzheyin' wato Iskan da ya hau kan ta Bafilatani ko Bature ne da dai sauransu. Daga baya da aka samu cu]anya sai 'yan borin suka yi sha'awar yadda Hausawa ke aiwatar da borin su da kuma sunayen Iskoki sai suka koma suna amfani da sunayen Iskokin 'yan borin Hausawa.

### 4.1.2 Halayen 'yan bori (Iskoki) na Hausawa da na Gbagyi

Da 'yan Borin Hausawa da na Gbagyi duk sun yi imanin cewa halayen Iskoki da ke hawa kansu iri ]aya ne. Gbagyi na kiran kalmar 'Bori' da harshensu "Boghyi" ne. A borin Hausa akwai Iskoki Farare akwai kuma Ba}a}e wa]anda 'yan borin Gbagyi ake kira 'Aguzheyin Buyhi' da

‘Aguzheyin zhyi’. Koda yake sunayen Iskoki da ke hawa kan ‘yan Borin Gbagyi da aka sani na asali ba su da yawa kuma ire-iren borinsu uku ne wato; “boghyi Gbemu” da “boghyi Madawa” da “boghyi Gbunu”. A yau a dalilin ha]uwarsu da Hausawa, sun ari sunayen Iskokin ‘yan Borin Hausawa sun mayar da su nasu.

Bunza (2006:9-10), ya ce:

> Kamar yadda Bahaushe ya yi imani da samuwar duniyar mutane haka ya yi imani da samuwar duniyar Iskoki. Yadda duk aka samu rabe-rabe ga jinsin mutane haka za a samu ga Iskoki domin su duka ‘yan Adam ne ma~uyarsu da sifarsu kawai ta bambanta.
> Ta fuskar jinsi Bahaushe ya kasa Iskoki gida biyu, Maza da Mata.
> Ta fuskar shekaru kuma ya kasa su zuwa: yara da manya da tsofafi(tsofaffi).
> A tsarin tunaninsu kuwa, akwai masu hankali akwai mahaukata.
> Ta fuskar ]abi’unsu kuwa Bahaushe ya yarda akwai na kirki akwai ashararu cikinsu. A matsayi na gaba ]aya da Bahaushe ya yi wa Iskokin }asar Hausa ya kasa su zuwa manyan kasusuwa guda biyu:
> i. Farfarun Iskoki (Aguzheyin buyi) a harshen Gbagyi
> ii. Ba}a}en Iskoki (Aguzheyin zhyi) a harshen Gbagyi

**Farfaru/Farare:**

> Bahaushe kan ce komai ya yi fari yana da kyawo in bayan kurkunu. A wurinsa fararen Iskoki su ne, Iskoki masu sau}in hul]a, abokanen kowa, masu saurin fahimtar abu, marasa cuta da cutarwa ga jama’a. Iskoki ne masu ]a’a da ladabi da biyayya ga ma’abotansu da jama’ar garin da suke.

**Ba}a}en Iskoki:**

> Ba}in launi abin zargi ne a }asar Hausa. Ba}a}en Iskoki su ne miyagu masu cuta da cutarwa. Masu rikita hankali da tayar wa jama’a hankali. Su ne Iskokin da ke saka manyan cutuka ga jikin ‘yan Adam. Masu wuyar sha’ani da warkarwa.

Alal ha}i}a Ibrahim (1982), ya raba iskoki kashi biyu kamar haka:

> ‘Farare’ da ‘Ba}a}e’,. Fararen su ne masu kirki, masu taimakon mutane, ba su son dukiya ko sarauta. Suna bayar da maganin cuce-cuce, ciki har da ‘ba}a}en’. Ba}a}en kuwa su ne, ma}etata, masu neman mutum da sharri, kamar a yi wa wani magani ya mutu ko ya sami ta~in hankali, da sauransu.

Shi ma Isma’ila (1991), ya nuna cewa Maguzawa sun kasa Iskoki zuwa gida biyu:

> Gona da Daji. Su Gona su ne masu sau}in kai da da]in hul]a, sa~anin wa]anda ake kira Daji, masu mugunta da sharri. Ya }ara da cewa ba wai ‘fararen’ iskoki su ne Gona ba, ko kuma ‘ba}a}en’ su ne Daji ba. Rabe-raben farare da ba}a}e daga baya ne Hausawan da ke zaune a Arewacin Nijeriya suke kiransu ba}a}e da fararen.

Gobir (2013), ya nuna cewa, ]aya daga cikin malaman Ru}iyya mai suna Usmana Al’iwadi

ya kasa aljannu kashi tara, kamar haka:

1. **Aljanin Soyayya: (Aye Aguzheyin)** a harshen Gbagyi: Shi ne, mafi ha]ari da sharri cikin nau’o’in aljannu, kuma mafi tsanani ga ri}e jiki.
2. **Aljanin Ruwa (Gawas):** (**Nuwa Guzheyin)** a harshen Gbagyi: Wani lokaci akan same shi da tsanani, wani lokaci kuma yana da sau}in kai, kuma yana zaune cikin teku ko rafi ne.
3. **Tsuntsu Aljani: (Olu Guzheyin)** a harshen Gbagyi: Wannan shi ne, mai tashi sama kamar tsuntsu.
4. **Aljanin Ban [aki: (Apasheba Guzheyin)** a harshen Gbagyi: Shi ne aljanin da ke zama a ban]aki, kuma yana da sharri, har ma Manzon Allah (SAW) ya umurci al’ummansa da yin addu’a idan za su shiga ban]aki don neman tsari daga sharrin irin wannan aljani.
5. **Aljanin Ma}abarta: (Azabi’aba Aguzeyin)** a harshen Gbagyi: Yana daga cikin shai]anun aljannu; dalilan shigarsa sun ha]a da: Hargowa ko abkawa, ko kwana ma}abarta, da kuma rashin yin addu’a idan an je shiga ma}abarta.
6. **Aljanin Cikin Gida (Amirul Baiti): (Aphimi Aguzheyin)** a harshen Gbagyi: Shi ne aljanin da ke zaune tare da mutane a cikin gidajensu, ya ci abinci tare da su, ya kuma sha tare da su, ya kwanta tare das u. Kusan kowane gida ba a rasa irin wannan aljani a cikinsa. Idan masu gidan masu ibada ne, zai zama mai ibada, idan kuma masu sa~o da sauraren ka]e-ka]e ne sai ya }ara zuga su a kan hakan. Yakan kuma yi

‘yan sace-sace cikin gidan, har a yi zargin yara ko matan gidan, domin ya haddasa fitina. Hadisin Manzon Allah (SAW) ya zo da haka, cikin Bukhari.

7. **Aljanin Sihiri: (Abhozhizhi Aguzheyin)** a harshen Gbagyi: Shi ne aljanin da ke hidima ga masu sihiri ko tsafi daga cikin mutane da aljannu. Wannan irin aljannu mugun shai]ani ne mai taurin kai. Shi ya sa masu sihiri ke son amfani da shi, don kada a yi saurin samun warwarewar matsalar.
8. **Abokin Aljani (Alkarin): (Nugudo Aguzheyin)** a harshen Gbagyi: Aljanin aboki wato }arinun, iri biyu ne: akwai na asali, wanda ake samu ga kowane mutum, tun daga ranar da aka haife shi. Shi ke sa mutum waswasi, da son sha’awa, da son auka wa sa~o. Akwai kuma }arinun mai gittowa ya auka wa mutum, ya shiga jikinsa, kuma shi ke sa ciwon farfa]iya. An samo Hadisi a Muslim, daga [an Mas’ud, ya ce, Manzon Allah (SAW) ya ce:

   ***Ba wani daga cikinku face an wakkala masa }arinun daga aljannu”.***
   ***Suka ce, “har kai ya Manzon Allah”? Sai ya ce “har ni, sai dai Allah***
   ***Ya taimake ni a kansa ya musulunta, bai umurnina said a alheri.***
9. **Jinjirin Aljani: (A~iphe Guzheyin** ko **A~iputu Aguzheyin)** a harshen Gbagyi: Shi ne aljanin da ke gito ma yara, kuma shi ke sa jarirai yawan kuka
   da dare, ko zabura daga barci.
   Wa]annan bayanai na masana, sun nuna mana cewa, Iskoki sun kasu kashi biyu, da na }warai da kuma miyagu. Wato dai kamar ]abi’ar ]an Adam suke. Akwai masu kirki, akwai masu zamba. Akwai Musulmi akwai Kafurrai, akwai masu sau}in kai ga mu’amala akwai kuma masu tsaurin kai. Haka ma bayanin yake a halayen Iskokin borin Gbagyi.

### 4.1.3 Tufafin ‘yan Borin Hausawa da Gbagyi

A Borin Hausawa, fitattun kayan da aka fi fita da su a fagen Bori su ne:

a. Hular ijiya (‘ya’yan wuri).
b. Warki.
c. Sandar dargaza.
d. Bulala.
e. Zobba a hannu da }afa.
f. [amaru da dagumai.
g. Ba}in zani.
h. Akan sa }unshi ga hannu da }afa.
i. Akan sa tozali.

j. Akan yi ala da goro ga le~e (ya yi ja).

k. Akan shiga fage da turaren wuta.

Suturun ‘yan borin Gbagyi a wancan lokaci kafin ha]uwarsu da Hausawa sun ha]a da:

a. Tufafi na sa}i (farare ko ba}a}e). (‘Asaci jhe’) a harshen Gbagyi.

b. [amaru da dagumai. (‘Gighigba’) a harshen Gbagyi.

c. Guraye na rataya a jiki da mara. (‘Apashipaya’) a harshen Gbagyi.

d. Sanduna. (‘Abusi’) a harshen Gbagyi.

e. ]an gatari. (‘Azebyi’) a harshen Gbagyi.

f. Farin }asa (jojo) (a shafa a fuska). (‘Khibui’) a harshen Gbagyi.

g. Warki. (‘Gighigba-Apa’) a harshen Gbagyi.

h. Turaren wuta. (‘Awutuyha’) a harshen Gbagyi.

A halin da ake ciki a yau, a sanadiyyar cu]anya da Hausawa, duk irin sutura na Bori da Hausawa ke amfani da shi, haka ma Gbagyi da shi su ke yi. Domin idan an lura a jerin tufafin borin Hausawa da na Gbagyi da aka ambata a baya, za a ga cewa ashe tun asali wasu kayayyakin da ‘yan borin Gbagyi suke amfani da su kusan su ne ‘yan borin Hausawa ke amfani da shi misali warki da ]amaru da dagumai da sanduna da bulala da ba}in zani da sauransu. Saboda haka a lokacin da Gbagyi suka ha]u da Hausawa, sai bai zama masu wani abu mawuyaci ba su yi amfani da na Hausawa da yake sun saba kusan iri ]aya ne.

### 4.1.4 Girka

Kamar yadda aka riga aka yi bayani a baya cewa tun farko ba a yin girka a borin Gbagyi sai dai a kai majiyyaci ko wanda Iska ya shiga ko ya ta~a daji a yi ‘yan yanke-yanke na kaji da awakai da girke-girken abinci a yi ‘Sallame’ ko koriya abin da Gbagyi ke kira ‘Aphya-Aguzheyin ya’ wato sallamar Iskoki ko Aljanun da ke kan mai shi ba zai kuma daminsa ba, ba kuma zai dawo ba sai

shekara ta kewayo bayan an ]ebe amfanin gona idan Iskan ya dawo a sake maimaitawa. To, amma bayan ha]uwar }abilar Gbagyi da Hausawa, sai aka sami sauyi maimakon yin sallame ko koriya kamar yadda suka saba sai suka koma suna yin Girka wato zaunar da Iska a kan dokinsa kamar yadda ‘yan borin Hausawa ke yi har zuwa yau.

Masana da Manazarta Bori sun yi bayanai da dama a kan ma’ana da yadda Hausawa ke aiwatar da Girka. Misali:

Bunza (2006:27) ya yi bayani a kan “Girka” kamar haka: ‘girka’ shi ne, zaunar da Iskoki a kan dokinsu su sami fahimtar juna. An samo tushen kalmar girka daga tushen, “gir” wanda za a iya sarrafa ta zuwa kalmomi kamar ‘girki’, ‘girke’, ‘girkewa’, ‘girkakke’. Tamkar yadda ake girke randa a wurin da ake ajiye ta a sha ruwa, ko tulu a wurin da aka yi masa gurbi , haka ma ake girke Iskoki a kan dokinsu su zauna ba tare da wata hayaniya ba, babu cuta , babu cutarwa. Ya kuma shimfi]a wasu daga cikin dalilai da kan sa a yi wa mutum girka kamar haka:

i. Ya zamo cikakken ]an Bori mai cin gashin kansa.
ii. Zaunar da Iskoki a kan dokinsu (]an bori) su zauna da Lumana.
iii. Kore ba}on Iska a kan doki ya daina damuwar Iskan da aka girke.
iv. Gano sanadiyar aukuwar wata ba}uwar cuta da Iskan da ya zo da ita.
v. Sama wa sabon ]an Bori Iskan da za su ri}a mu’amala da shi wajen Bori da waninsa.
vi. Gano irin ki]an garaya ko goge da Iskan sabon ]an Bori ke so a matsayin takensa.
vii. Ku~utar da lafiyar jiki, da hankalin ]an Bori, daga miyagun ta}adarun Iskoki.

Akwai tanade-tanade da ake yi na Girka. Idan maras lafiya, ko mai lafiya za a yi wa shi, sai an tanade su , an kuma shirya su, kafin a shiga yin Bori. Kayan aiki sun ha]a da:

a. Tabarmi biyu sababbi.
b. Manyan randunan ruwa biyu sababbi.

c. Tulunan ruwa biyu sababbi.

d. Masakli biyu sababbi.

e. Faifai hu]u sababbi, biyu na rufe randa, biyu na yin tirare ga uban Bori da wanda za a yi wa Girka.

Akwai Sutura ta Girka kamar haka:

a. Ba}a}en zannuwa biyu.

b. Ba}a}en huluna biyu.

c. Sababbin kaya ]aya (na fita Girka).

d. Sabon warki ]aya na mai Girka.

Akan tanadi abinci kaman su:

a. Manyan goro biyu, ja da fari.

b. Kaji biyu da}wale, ba}a da fara.

c. Kayan abincin marmari iri-iri.

d. {waryar zuma ]aya, ko ma]i, ko alewa.

e. Tandun man shanu, ko man gya]a, ko man ka]e.

Kayan Girka sun ha]a da:

a. Saiwowi, da ganye da ~awon itace, casa'in da tara (99).

b. Dogon itacen tumfafiya na gyaran ruwa.

c. Jar kanwa ta saka wa a tsimin Girka.

d. Kwalolo ko ludayin shan magani.

e. Kayan yaji iri-iri.

Bayan wa]annan abubuwa da aka ambata na Girka, sai wani muhimmin abu wanda shi ne; Yanayin Zaman Girka kamar haka:

a. Ba a wanka sai an }are.

b. Ba a salla balle alwala.

c. Ba a magana da baki sai ima'i (ishara) ko maganar Boboniya.

d. Ba a cin abinci da hannu baki ake sakawa.

e. Idan za a sha ruwa, ko magani, uban Girka zai bayar ]an Bori sai ya mi}e hannaye a baya.

f. Ba a shiga ]aki sai ta baya da baya.

g. Ba a sa wata sutura sai ta Girka.

h. Ba a zuwa yawo a ko'ina ko kashi gidan ake yi.

i. Ba a kwana ko'ina sai cikin ]akin Girka.

Bunza (1989:41) ya yi bayani cewa; da asuba za a fara ka]a garaya a yi wa wanda za a yi wa girka wanka da ruwan magani, kuma a yi masa turaren haya}i. Mai ki]an garayar zai fuskanto wanda ake yi wa girka. Nan da nan sai boka ya yanka kajin biyu a ]auki farar a ]ora kan wanda ake yi wa girka ya sa~e ba}ar a kafa]a. Boka zai ]auki farar kaza ya gewaya ga kansa sau uku.

Daga nan za a fara kiran aljannu ]ai]ai da ]ai]ai duk wanda aka ga mai girka ya taka ko ya motsa jikinsa in marar lafiya ne, sai a ce wannan aljani ne. In ya tsimu zai zazzare ido da sau batu, baki na kumfa, wani lokaci har da kuka. Wanda ake yi wa girka zai fara surutai kan abubuwan da aljannu ke so, boka na fassara wa sauran jama'a. Kuma boka zai ro}i wasu aljannu su tafi wasu su tsaya. In ji 'yan bori, wai wanda ake yi wa girka zai gan su }iri-}iri da idonsa.

Bunza (2006:27) ya ce: "Tsawon kwanakin Girka daga kwana uku ne zuwa bakwai ba a cika wuce su ba. Ranar da za a fara ita ce 'ranar shiga'. Ranar da za a }are ita ce, 'ranar fita'. Yanayin rawar Girka, za a yi amfani da itacen tumfafiya a ri}a dukan }afafun wanda ake yi wa Girka idan ya yi kuskuren taka rawa. Haka kuma idan Girkar rashin lafiya ce, duk taken Iska akan yi, idan an ga

sau}i a jiki, wannan Iskan ne ya kawo cutar. Idan kuwa zama ]an Bori kawai yake son ya yi, duk Iskan da aka fara takenta ya fara ka]a kansa, ita ce Iskar da ke son ya zama dokinta.

Idan aka yi nasarar kamala Girka lafiya lau, ranar fita za a je wajen gari a }ar}ashin wata itaciyar Kuka, ko Tsamiya, ko Gamji, a nan za a fita Girka. Za a yi wa wanda ake yiwa Girka wanka da ruwan maganin da aka yi masa tsimi wa]anda yake sha lokacin da ake yi masa Girka. Za a tu~e shi a yi masa wanka, a sa masa kayansa na gida, daga wannan lokaci ya zama cikakken ]an Bori mai cin gashin kansa.

Shi ma Ibrahim (1982:53-55) ya kawo bayani a kan girka kamar haka; Da farko idan Iskoki suka ta~a mutum zai kamu da wani ciwo ne ko kuma ta~in hankali. ‘Yan uwan mutumin za su shiga neman magani don a lokacin ba su san dalilin ciwon ba. Idan ciwon ya zamana an rasa kansa, watau an yi magani, an yi magani har an gaji ba a warke ba, sai a shiga shawarwarin ko Iskoki ne suka ta~a marar lafiyar. Daga nan sai a tafi wurin ‘yan bori don neman magani. Su kuma ‘yan bori da zuwa wurinsu sai su ce “Ai ciwon ba irin wanda aka saba da shi ba ne. Ciwon namu ne, don Iskoki ne suka ta~a shi”. Sai ]an bori ya shiga ba da maganin iskoki. Idan ya yi, ya yi, ya ga bai warke ba, sai ya nemi yardar ‘yan‘uwan majiyyaci don a yi masa girka. Watau a kira Iskokin da suka ta~a shi, a ro}e su, su kau, su rabu da shi don ya sami lafiya. Idan kuma sun }i, sun ce su zama za su yi a kansa, to sai ]an borin ya shirya su su zauna a kansa. Shi kuma majiyyacin sai ya warke, amma daga wannan ranar shi ma ya zama ]an bori ke nan. Zai dinga hawa bori duk lokacin da wani ya yi masa kirarin Iskokin da suke kansa, ko kuma idan shi ya yi da kansa. Zai kuma tanadi kayayyakin bori wa]anda suka dace da Iskokin da suke kansa.

Idan an yarda za a yi wa wani majiyyaci girka, sai ]an borin da zai yi girkar ya fara tanadin kayan girka. Da farko zai ha}o sauyoyi iri-iri har guda ]ari na yin tsumin girka. Daga nan sai ya zuba sauyoyin nan a cikin wata }atuwar tukunya, ya kawo ruwa ya zuba har bakin tukunyar, sa’annan ya samo alawar ]inya da soyayyen gari ya zuba. Ya kawo rairayi ya kewaye gindin

tukunyar da shi. Sai kuma ya kawo jan zakara ya yanka a gindin tukunyar. Ya figi ]an gashin ya li}a a jiki. Idan tsimin ya kwana biyar  sai majiyyacin ya fara sha. Daga ran nan ba zai }ara shan wani ruwa dabam ba sai an }are girkar.

Idan ranar girka ta taho, sai a kirawo maka]an bori. Amma an fi yi da ki]an garaya, don yawanci su suka fi sabawa da ka]a take ko kirarin Iskoki. Kafin a kai ga haka an riga an tanadi tabarmi (karauni) guda biyu da kaji biyu fara da ba}a. Idan an kawo majiyyacin sai a tu~e masa duk kayan da ke jikinsa. Idan kuma mace ce sai a cire mata yari da abin wuya da warwaron hannunta, sa'annan a sa mata gajeren wando, a ]aura mata farin zane, a kawo wani farin zanen kuma a lullu~e ta da shi. Sai kuma a zaunar da majiyyaciyar a kan tabarmin nan tana duban gabas. Mai girkar za ta kewaya kajin nan guda biyu a kan ta har sau uku. Maka]a za su zauna daga bayanta. Mai girkar za ta zauna a gabanta. Sa'an nan 'Muguro' matar da za ta ri}a ture kan majiyyaciyar don wani Iska da ta hau kanta ta sauka, za ta zauna a gefenta.

Idan an gama shiri tsaf, sai maka]a su shiga ka]a taken Iskoki iri daban-daban. Za su fara da ka]a taken Sarkin Maka]an Sarkin Aljan, sannan na Uban Dawaki, sai kuma na Sarkin Aljan. Daga nan, sai a shiga ka]a taken sauran Iskoki ]aya bayan ]aya. A lokacin da ake ka]a taken Iskokin, za a dinga kula da halin da majiyyaciyar ke ciki. Idan an ga tana tsuma, jikinta na rawa, to Iskan da ya ta~a ta ya zo ke nan. A wannan lokacin duk wata magana ko wata harka da majiyyaciyar ta yi, an ]auka ba yin ta ba ne, Iskan da ya ke kanta ne ya yi.

Idan mai girkar ta gane Iskan da ya ta~a majiyyaciyar ya zo, sai ta shiga ro}on shi don ya rabu da ita ta sami lafiya. A lokacin ne Iskan zai fa]i dalilin da ya sa ya ta~a majiyyaciyar. Idan ya yi niyyar rabuwa da ita, sai ya ce, ai daman wucewa zai yi. Amma ga irin sadakar da yake so a yi masa kafin ya wuce. Kuma a lokacin zai fa]i irin abubuwan da yake so majiyyaciyar ta kiyaye da su idan ta warke. Idan har ta kuskura ta sa~a zai dawo. An ce da zarar an yi wa]annan abubuwa sai matar ta warke ta koma kamar ba ta ta~a yin ciwon ba.

In kuma an ro}i Iskan ya rabu da majiyyaciyar ya }i, ya ce shi zama zai yi a kanta. Shi ke nan sai mai girkar ya fa]i irin kayan da majiyyaciyar za ta tanada saboda wannan Iska da zai zauna a kanta. Misali idan Bafiltana ce ta hau kanta, sai a gaya mata ta nemi kayanta watau zannuwan Fulani da kayan adonsu da }waryar nono tare da faifai da tarde. Idan kuma Malam Alhaji ne sai a ce ta nemi fararen kaya tare da sandar }arfe. Daga wannan lokaci majiyyaciyar ta zama ‘yar bori, kuma za a dinga kiran ta dokin wannan Iska. Za ta sami lafiya daga wannan ciwon, amma kuma duk lokacin da aka ka]a taken wannan Iskan sai ta hau bori, ta dinga fa]ar maganganu da ake ]auka ba maganarta ba ce, maganar Iskan da ke kanta ne. Ita ma za ta dinga bayar da magani kamar kowane ]an bori.

A dalilin cu]anya da Hausawa da Gbagyi suka yi tun da da]ewa, shi ne ya haifar da sauyi a yanayin girkan Gbagyi da tun asali sukan yi wa majiyyaci sadaka ne da nufin cewa an sallami Iska, maimakon haka, a yau sun koma suna yin girka kamar yadda ‘yan Borin Hausawa ke yi.

Ga misali na hira da aka yi da Wasa Sarkin Bori Kuta (29/07/2011) domin tabbatar da cewa Borin Gbagyi da Girka a yau ya kasance kamar na Hausawa ne inda ya ce: “Dalilin yin bori ciwo ne, ko kamun aljanni. Kuma akwai aljani ko Iska ]ari ba biyu wato casa’in da takwas (98), cikinsu akwai farare, akwai kuma ba}a}e. Daga cikin sunayen Aljanin akwai: Barhada da Magajiya da Inna Doguwa da Gajimari da Sarkin Rafi da Bamaguje da Bature da [an-Galadima da Halima da dai sauransu”. Ya }ara da cewa: “Wanda ba a yi ma Girka ba, ba zai yi wa wani ba. Girka da wanka kuma ba su wuce Kwana goma sha hu]u. [an Borin Gbagyi na farko da ake kira ‘Wawa’ ]an Bori Bahaushe ne ya gyara shi wato ya yi masa girka da wani ]an Bori kuma mai suna ‘Kundumi Gwari’, Bahaushe ne ya yi masa girka”.

### 4.1.5 Kayan ki]an borin Hausawa da na Gbagyi

A tsarin Borin Hausawa, idan za fara Bori koda yake ya danganci irin Borin da ake son a yi, akwai kayan ki]a kamar haka:

a. Kalangu.
b. Goge ko Garaya.
c. Kukuma
d. {warya na ki]awa.
e. Kacakaura
f. Caki (buta, duma, galura, gora ko gyan'dama).

Kayan ki]an Borin Gbagyi wato (Aboghyi-nya) da harshen Gbagyi sun banbanta dangane da irin borin da za a ka]a wa take kamar yadda aka yi bayani a baya. Akwai kayayyakin ki]a da suka ha]a da:

a. Kabulu. – [inkakken masaki ne da fata kamar garaya, amma ya fi garaya girma.
b. Mulo. – Wannan abin ki]in shi ake kira 'molo' da Hausa.
c. Akayau – Karafa ne masu zobba da akan ]aura a }afa idan ana rawa suna }ara.
d. Apapah – Kwaraye ne da ake ka]awa tare da molo.
e. Agojei – Wato kamar gogen Hausawa yake ana sa masa izga da mari}in gogawa don }ara.
f. Agula – Kamar dai kacakaura, goruna ne madaidaita da 'yan tsakuwa ko duwatsu ciki ana ka]awa.

### 4.1.6 Amfanin 'yan Borin Hausawa da na Gbagyi

Kafin zuwan Musulunci 'yan Borin Hausawa da na Gbagyi na daga cikin wa]anda al'ummominsu ke neman taimakonsu na ba da sa'a, da wasu nau'uka na magungunan tsaron kai da kaya. Misali: Bunza (2006:25-26) ya ce: "A sha'anin sarautu 'ya'yan sarauta na amfani da 'yan Bori, idan ta fa]i a ba su. Dubi wannan jawabi na Malamin wa}a Ibrahim Maidangwale Tubali (Naramba]a), yana cewa;

Jagora : *“Wani ya kunna ya ga ba wuri,*

*“ ‘Yan Bori sun kai shi sun baro,*

*“ Saruru ya battala abinai,*

Yara : *Ya koma bi]at kwabon hwura”.*

*(Gindin wa}a: Ibrahima na Guraguri)*

Haka kuma ha]uwar Alhaji Gambu Fagada da Sarkin Barayi da aka so Sarki ya je ya gama da Tsoho Tudu (buwayayyen attajiri) sai Sarkin |arayi ya ce wa Gambo, lokacin da ya so ya bi Tsoho Tudu, ya yi masa sata, sai da ya je wajen ‘yan Bori suka ba shi sa’a, yana cewa;

Jagora: *“An yi Bori, an yi Bori!*

*Na yanke awakina da kaji*

*An ce sa’a ta samu babba”.*

Wa]annan ]iyan wa}a sun tabbatar mana da amfanin Bori musamman Borin magani wanda ake yi domin neman waraka ga wani, ko neman wata sa’a, ta samun wani amfani, ko tunku]e wata cuta.

Akwai wasu nau’o’i na Bori da ake yin su domin wasu dalilai na musamman, misali Borin Fage don nisha]i da Borin Giri domin a fyace koma sosai, a fa]i wani abu da ke damuwar rai a ji, da Borin Girka domin yi ma majiyyaci ko wanda iska ya shige shi Girka, wato a zaunar da Iskoki a kan dokinsu su sami fahimtar juna. Ke nan Borin Girka daga cikin wasu amfaninsa, yana ku~utar da lafiyar jiki, da hankalin ]an Bori, daga miyagun ta}adarun Iskoki.

Haka kuma a hirar da aka yi da Amina Ma’aji Bosso (2013) ta ce: “Ainihi shi Bori ciwo ne wanda Iskoki kan jawo wa mutane idan sun ta~e su ko sun shige su sun yi ta fama da rashin lafiya iri-iri da ba a gane irinsa ba sai an nemi Boka ]an Bori ya taimaka wa majiyyacin da magunguna sannan ya samu lafiya”. Ashe amfanin ]an Bori ne yana taimakawa jama’a wajen kare lafiyarsu.

Bori wani tsangaya ne da aka danganta shi da harkar samar da lafiya, yana }unshe da matakai da ake bi na samar da lafiya, wato (gano cututtuka kafin yin jinya) da ya ha]a da kulawa da lafiya da sallamar majiyyaci bayan an yi masa jinya ya warke.

Wannan ]abi'a ya samo asali ne tun kafin shigowar addinin Musulunci a }asar Hausa, kuma Hausawa 'Maguzawa' a Arewacin Najeriya da na Taraiyyar Kudancin Niger sun amince cewa 'Bori' yana ]aya daga cikin sahihiyar hanyar kariya daga kowane cuta da ta shafi Iska. Haka kuma an yarda cewa hanya ce ta samar da waraka daga cututtuka ta bautar Iskoki. Madauci (1968:77) ya ce:

> Idan za tambayi 'yan Bori za su fa]a maka cewa ba suna yin bautar ne don nisha]i ko jin da]i ba, amma saboda taimaka wa jama'a da "kariya" na kowani iri da kuma waraka daga cututtuka na kowane iri. Sukan yi alfahari da cewa sau da yawa a kan kai majiyyaci Asibiti wajen Likita ya kasa warkar da shi, amma idan an kawo shi wajensu sai su warkar da shi ta hanyar Bori.

Wannan ya nuna cewa ba duka cututtuka ne ake iya warkarwa a Asibiti ba, akwai wa]anda dole sai an kawo ma 'yan Bori.

Ana amfani da Bori wajen magani da kuma yin riga-kafin cututtuka kamar: tarin fuka da amai da gudawa da ta~in-hankali da farfa]iya da shan Inna da Kuturta. Wasu cututtuka kuma da 'yan Bori kan warkar su ne: tari da cutar daji da zazza~i da sauransu. Shahararren mawa}in nan Marigayi Alhaji Manman Shata Ya jaddada muhimmancin 'yan Bori a wata wa}a da ya yi mai take "Sarkin Bori Sule" yana cewa:

> Jagora: *Yau wannan zamani*
> *Wannan lokaci,*

*Kowa yake zazza~i*

*Ka ga ana gaida shi,*

*Yana amsawa jifa – jifa*

*Ku zan gun mai Bori 'Sule'*

*(yanzu) sai ka ga warware*

*Yana yawon duniya.*

### 4.1.7 Kamancin Borin Hausawa da na Gbagyi

Kamar yadda aka riga aka fa]a can baya cewa babu yadda za'a yi magana a kan kwantacin borin Hausawa da na Gbagyi ba a ta~o shigowar Addinin Musulumci ba, domin ha]uwar Hausawa da Gbagyi bai faru ba sai da bayan Hausawa sun amshi Addinin Musulumci ne imani da bori ya raunana a zukatansu. Wasunsu kuma da ba su daina borin ba saboda wasu bu}atu na rayuwar yau da kullum kamar taimakon marasa lafiya da magunguna da neman abinci da sauransu, sai suka warwatsu cikin }asashen makwabta har da garuruwan Gbagyi suna aiwatar da bori.

Da yake dama kafin shigowar Musulumci Gbagyi ba su da wani addini da ya wuce na gargajiya wato tsafi da bautar gumaka da Iskoki ta nasu salon bauta, ganin yadda Hausawa 'yan bori ke aiwatar da nasu, sai suka yi sha'awa musamman ta fannin tufafi da kayan ki]a da sunayen Iskoki da halayen 'yan bori (Iskoki) da kuma girka.

Idan an dubi tufafi da kayayyakin da 'yan borin Gbagyi ke amfani da su a yau, za a ga cewa suna amfani da kayan Filani da suka ha]a da tufafi farare na sa}i da }waraye a matsayin kayan Iska Bafulatana da jajayen tufa da takalma (sandal) kamar na Iska mai suna Halima da fararen riguna manya ha]e da sanda na }arfe na Iska Malam Alhaji da dai sauransu. Bayan wa]annan, akwai sauran kayayyaki kamar: hular ijiya ('ya'yan wuri) da warki da bulala da ba}a}en zane da turaren wuta da ]amaru da dagumai da zobba a hannu da }afa da sauransu duk Kaman na Hausawa.

Ta fannin kayan ki]a ma suna da ala}a da juna idan an lura kayan ki]a kamar molo da goge da kabulu da Gbagyi ke amfani da su a yau sun samo asali ne daga ba}i kamar Hausawa da Bare-

bare da suka fara shigowa }asashen Gbagyi don farauta da kasuwanci da neman abinci misali; Adamu Bodo Babarbare ne da ya fara zuwa }asar Kuta da garaya sai Gbagyin Kuta suka gani suka kwaikwaya sannan suka }ir}iro kabulu da goge da ake ki]a ma ‘yan borin ‘Madawa’.

Idan kuma aka juya ta wajen sunayen Iskoki kamancin na Gbagyi da na Hausawa }a]an ne. Mama Habiba Kuta (2013) ta ce: “Kafin ha]uwar Gbagyi da Hausawa da kuma amsar Musulumci, a gargajiyance suna kiran Iskoki wasu sunaye ne kamar: ‘Akula’ ko ‘Anuwada’ ko ‘Aguzheyin’ daga baya da suka amshi Addinin Musulumci a dalilin shigowar Hausawa, sai suka fara kiran Iskoki da sunan ‘Aluzheyin’ wato Aljani ko Jinnu kamar yadda Hausawa ke kiransu ko kuma kamar yadda sunansu yake da Larabci cikin Al-Qur’ani mai girma.

Bayan ‘yan borin Gbagyi sun sha}u da na Hausawa a dalilin zama tare, sai suka fara jin sabbabin sunaye na Iskoki suka ara suna amfani da su musamman fitattun kamar: [antsatsumbe da Doguwa da Halima da Hajon Ruwa da Najabilo da Gungungun da sauransu, da kuma sunayen Iskoki na rukunin }abilu kamar: Bature da Balarabe da Bamaguje da Bafulatani da sauransu, da sunayen Iskoki na [abi’u da Halayya kamar: Kure da Ba}o da Gajimari da Bahago da Duna da Gajere da Wanzam da Sarkin Maka]a da Sarkin Aski da [an Galadima da Nana Kadija da Malam Alhaji da sauransu”.

Kamar yadda aka riga aka bayyana can baya cewa ‘yan borin Hausawa da na Gbagyi duk sun yi imanin cewa halayen Iskoki da ke hawa kansu iri ]aya ne. Akwai Iskoki Farare da kuma Iskoki Ba}a}e, wa]anda Gbagyi ke kira ‘Aguzheyin Buhyi’ da ‘Aguzheyin Zhiyi.

Dangane da halayensu kuwa yadda ‘yan borin Hausawa suka yi imanin Fararen Iskoki su ne masu sau}in hul]a, abokanen kowa, masu saurin fahimtar abu, marasa cuta da cutarwa ga jama’a, su kuma Ba}a}en Iskoki su ne miyagu masu cuta da cutarwa. Masu rikita hankali da tayar wa jama’a hankali. Su ne Iskokin da ke saka cutuka ga jikin ‘yan Adam. Masu wuyar sha’ani da warkarwa. Haka ma ‘yan borin Gbagyi suka yi imani.

Adamu Kambari Kuta (2011) da kuma Amina Ma'aji Bosso (2013) sun ce: Cikin Iskoki na borin Gbagyi da ake da su a duniya akwai masu kirki da kuma marasa kirki wato Farare da Ba}a}e. Fararen su ne masu taimako da bayar da alheri su kuma Ba}a}e ba su taimako sai dai su haddasa cutuka da kuma cutar da jama'a".

Game da girka, babu kamanni da na Hausawa domin kamar yadda aka riga aka yi bayani tun farko a borin Gbagyi ba a yin Girka sai dai a kai majiyyaci ko wanda Iska ya shiga ko ya ta~a daji a yi 'yan yanke-yanke na kaji da awakai da girke-girken abinci, a yi abin da ake kira 'Apya-Aguzheyin ya' da harshen Gbagyi. Wato sallaman Iska ko Aljanni, ke nan ba zai dami mai shi ba, ba kuma zai dawo ba, sai shekara ta kewayo bayan an ]ebe amfanin gona. Sai dai a borin 'Gbemu' ne da al'adar girka ta so ta zo ]aya da na Hausawa. Ita mai borin akan saka ta ne a ke~a~~en ]aki har na tsawon kwana bakwai, a kuma girke mata tulun tsimi na magani da za a ri}a bata tana sha a matsayin abincinta na wa]annan kwanaki, babu cin abinci, babu wanka, ba a fita waje, ba a magana da kowa, ba a sauya tufafi da sauransu, har sai rana ta bakwai da za a yi mata wanka ta canza tufafi. Kusan kaman na Hausawa.

Bayan ha]uwar 'yan borin Gbagyi da na Hausawa, sai aka sami sauyi maimakon yin al'adar su ta sallama kamar yadda suka saba sai suka koma suna yin Girka kamar yadda Hausawa ke yi har zuwa yau.

### 4.1.8 Bambancin Borin Hausawa da na Gbagyi

Da farko dai ire-iren borin Hausawa da aka sani guda hu]u ne wato: borin girka da borin fage da borin giri da borin magani. Borin Gbagyi kuwa guda uku ne kamar haka: boghyi Gbemu da boghyi Madawa sai boghyi Gbunu.

A nan za a dubi bambancin borukan nan biyu na Hausawa da na Gbagyi ta fannonin tufafin bori da kayan ki]an bori da sunayen Iskoki da halayen ‘yan bori (Iskoki) da kuma girka.

Idan aka dubi tufafin ‘yan borin Hausawa sun danganci wa]anda suka dace da Iskoki ne, misali Iskan da ake kira Halima ta }aunaci jajayen sutura da Iskan Bafulatana ita ma fararen tufafi ne na sa}i da kwaraye da Iskan Malam Alhaji ]an bori kan sa doguwar riga fara ko babban riga da sandar }arfe da sauransu. Tufafin borin Gbagyi kuwa zanuwa ne na sa}i ba}a}e ko farare da mata kan ]aura a }irji babu hula misali a borin ‘gbunu’ da borin ‘madawa da suke sa riga fari, su yi bante da zane, su kuma ri}e ]an gatari.

Ta fannin kayan ki]a kuma ‘yan borin Hausa na amfani kayan ki]a kamar: garaya ko goge da kalangu da kukuma da kwarya na ki]awa da kacakaura da kuma caki. Su kuwa ‘yan borin Gbagyi suna amfani da kabulu (siffansa kamar garaya, amma ya fi garaya girma) da mulo (wato molo, shi kuma kamar kuntigi, amma ya fi kuntigi girma) da akayau (}arafa ne masu zobba da ‘dan bori kan ]aura a }afa idan yana rawa suna }ara) da agula (kamar kacakauara, goruna ne madaidaita da ‘yan tsakuwa a ciki ana }a]awa) da shakwu (tukunya ne da aka ]inke bakin shi da fata ana ka]awa da tafukan hannu kamar yadda za a gani a hoyuna na rataye) da sauransu. Akasin irin na Hausawa.

Sunayen Iskokin ‘yan borin Hausawa na da yawa, an kasa su kashi biyu, na gargajiya da aka taras tun gabanin saduwa da Larabawa kamar: Iska da Mutantani da Mutanen ~oye da {wan}wamai da [antsatsumbe da Doguwa da sauransu, da wa]anda aka samu bayan saduwa da Larabawa kamar: Aljani da Jinnu da Iblishi da Rauhani da Ira’izai da Nana A’isha da Nana Kadija da Malam Alhaji da sauransu. Su kuwa ‘yan borin Gbagyi kafin ha]uwar su da Hausawa da kuma amsar Musulumci, suna da sunayen gargajiya da su ke kiran Iskoki da shi kamar haka: ‘Akula’ ko ‘Anuwada’ ko ‘Aguzheyin’ daga baya ne a dalilin ha]uwarsu da ‘yan borin Hausawa, sai suka fara kiran Iskoki da sunan ‘Aluzheyin’ wato Aljani ko Jinnu kamar yadda Hausawa ke kiransu ko kuma kamar yadda sunansu yake da harshen Larabci da kuma sunayen Iskoki kamar: [antsatsumbe da Doguwa da

Halima da Hajon Ruwa da Najabilo da Gungungun da Bature da Balarabe da Bamaguje da Bafulatani da Kure da Ba}o da Gajimari da Bahago da Duna da Gajere da Wanzam da Sarkin Maka]a da Sarkin Aski da [an Galadima da Nana Kadija da Malam Alhaji da sauransu.

Idan aka dubi bambancin da ke akwai a halayen Iskokin ‘yan borin Hausawa da na Gbagyi, sai a ce yadda ‘yan borin Hausawa suka yi imanin Fararen Iskoki su ne masu sau}in hul]a, abokanen kowa, masu saurin fahimtar abu, marasa cuta da cutarwa ga jama’a, su kuma Ba}a}en Iskoki su ne miyagu masu cuta da cutarwa. Masu rikita hankali da tayar wa jama’a hankali. Su ne Iskokin da ke saka cutuka ga jikin ‘yan Adam. Masu wuyar sha’ani da warkarwa. Su kuwa ‘yan borin Gbagyi kafin ha]uwarsu da ‘yan borin Hausawa sun yi imanin cewa duk wani Iska ba shi da kyau, dukkan su masu cutarwa ne shi ya sa sukan yi }o}arin sallaman su maimakon yin girka a zaunar da Iskokin a kan ]an bori.

A borin Hausawa ana girka wato zaunar da Iska daram a kan dokinsa wato kan ]an bori ba tare da matsala ba. A borin Gbagyi kuwa ba a yin girka sai dai a sallami Iska bisa al’ada na yanke – yanken kaji da awakai a daji.

**4.2 Na]ewa**

Bincike da ya shafi kwatancin borin Hausawa da na Gbagyi ba zai ta~a kammaluwa bisa tsari ba sai an nuna sigogin borin biyu da ake son yin nazari a kai, a nuna fannonin da suka yi kama da fannonin da suka bambanta. Abin da aka yi }o}arin yi a nan shi ne iyakance farfajiyar da aka kwatanta borin al’ummun biyu kamar: sunayen Iskoki da halayen ‘yan Bori (Iskoki) na Hausawa da na Gbagyi, wato dangane da irin Iskokin da ke hawa dokinsu da tufafin ‘yan bori da kayan ki]an ‘yan bori da Girka musamman na Hausawa ta yadda ya canja na Gbagyi da kuma amfanin ‘yan Bori. Da yake an lura cewa abu ne mawuyaci a ce sai an kwatanta borin Hausawa da na dukan manyan garuruwa da }auyukan Gbagyi, sai aka za~i wa]annan manyan garuruwan Gbagyi da suka

ha]a da: Kuta da Minna da Suleja a jihar Neja da kuma Birnin Gwari da ke cikin jihar Kaduna, domin samun sau}in bincike a kan kamanci da banbancin borinsu da na Hausawa.

## BABI NA BIYAR: KAMMALAWA

### 5.0 Shimfi]a

Wannan babi wanda shi ne na }arshe a wannan aiki, ya }unshi na]ewa, da kammalawa wato ta}aitaccen bayanin abubuwan da binciken ya gano da shawarwari da suka danganci aiwatar da bori

ga masu sha'awarsa da hukumomin da alhakin bun}asa al'adu ya rataya a wuyansu. Sai manazarta da wannan bincike ya tattaro bayanansa, har ya cim ma manufarsa. Akwai kuma misalai na tambayoyi da aka gabatar wa jama'a domin neman ingantattun bayanai da sunayen 'yan bori da masana bori da aka yi hira da su. A }arshe, an kawo rataye na wasu hotuna na 'yan borin Hausa da na Gbagyi da tufafi da kayan ki]ansu.

**5.1 Na]ewa**

Bahaushe kan ce 'komai nisan dare, gari zai waye'. Da wannan ne wannan bincike mai suna "kwatancin borin Hausawa da na Gbagyi" ya kawo }arshe. An gudanar da wannan bincike ne a babi–babi har guda biyar. A babi na farko, an bayyana ma'anar bori da ire-irensa na Hausawa da na Gbagyi, an kawo dalilan da suka haddasa yin wannan bincike da muhimmancinsa, an dubi farfajiyar bincike wato wuraren da binciken ya yi iyaka, da matsalolin bincike, sai kuma hasashen bincike da tarihin Hausawa da na Gbagyi bisa ra'ayoyin masana tarihi da na masana harshe. An kuma yi bayani a kan dangantakarsu wato, yadda suka yi zamantakewa har suka sha}u da juna, 'yan borin Gbagyi suka kwaikwayi wasu fannoni na aiwatar da bori a wajen 'yan borin Hausawa.

Har ila yau, an kawo ta}aitaccen bayanai dangane da borin Hausawa da kuma na Gbagyi. An kawo su ne domin a samu sau}in kwatanta su, a gano wuraren da suka yi kama da wuraren da suka bambanta.

A babi na biyu, an waiwayi ayyukan da suka gabata masu ala}a da wannan fage na bincike kai tsaye ko a fakaice kamar wallafaffun litattafai da kundayen digiri daga na ]aya zuwa na uku da ma}alu da }asidu da mujallu da jaridu.

A wannan babi, an nazarci yadda marubuta daban-daban suka bayyana ra'ayoyinsu game da bori musamman na Hausawa. Marubuta irin su Bunza da Besmer da Badejo da Nicole da Greenberg

da Madauci, sun fito da bayanai a kan ma'anar bori da matsayin bori kafin da bayan shigowar addinin Musulunci.

A babi na uku, an yi anfani da hanyoyi daban - daban wajen tattaro bayanai da suka taimaka wajen gudanar da wannan bincike wanda suka ha]a da: Ganawa ta baka da tambayoyi da ]akunan karatu inda aka dubi Litattafai da Kundaye da Mujallu da ma}alu da }asidu da Jaridu, an kuma le}a Yanar-Gizo.

A babi na hu]u, inda kanun batu yake, nan ne aka kwatanta borin Hausawa da na Gbagyi a fannonin sunayen Iskoki da halayen 'yan bori (Iskoki) da tufafin 'yan bori da girka da kayan ki]an 'yan bori da kuma amfanin 'yan borin. An yi haka ne domin a za}ulo fannonin da suka yi kama da kuma fannonin da suka bambanta, a kuma ga irin yawan sauye-sauye da aka samu a borin Gbagyi.

A babi na }arshe wato babi na biyar, an kawo bayanan kammmala bincike ne da suka ha]a da; na]ewa da kammalawa wato inda aka kawo abubuwan da binciken ya gano daga farko har }arshe, sai shawarwari.

## 5.2 Kammalawa

A }arshe, wannan bincike ya gano cewa kafin zuwan addinin Musulunci, al'ummun Hausawa da Gbagyi, duk sun ]auki bori a matsayin addinin gargajiya ne, kuma 'yan bori duk da yake suna bautar Iskoki ne, sun yarda cewa akwai Allah (S.W.T.) mai kowa mai komai, amma yadda za su nemi biyan bu}atunsu ne kai tsaye ba su fahimta, sai dai ta hanyar Iskoki. Misali, Badejo (1980), ya yi da'awar cewa bori addini ne kuma hanya ce da mabiya ke bi su sadu da Ubangiji da taimakon Iskoki da suka gabata wa]anda suke zaune a doron }asa. Haka kuma su wa]annan Iskokin su ne suke kula da dukkan wata hanya ko tafarki na rayuwar mabiya. Domin haka, ya zama wajibi wani abu ya kasance akwai jituwa a tsakanin mabiya da Iskoki domin biyan bu}atunsu da bu}atun sauran al'umma da ke zaman tare.

Bayan harha]a bayanai, bincike ya gano cewa tun can kamin shigowar addinin Musulumci da na Kirista, akwai ala}a ta zamantakewa tsakanin Hausawa da Gbagyi. Sauye-sauye da borin Gbagyi ya samu ya faru ne a dalilin cu]anyarsu da Hausawa, kuma ya yi sanadin ~acewar salon na Gbagyi a yau.

Da yake dukkan al'ummun Hausawa da Gbagyi da ma sauran al'ummun duniya sun yarda da samuwar ~oyayyun halittu da ]an-Adam ba ya iya gani da ido wato Iskoki, cikinsu akwai mugaye (ba}a}e) da kuma masu kirki da taimakon ]an Adam wato farare kenan. A nan bincike ya gano akwai taimako da wasu 'yan bori ke yi wa al'umma ta wajen warkar da majinyata da suka kamu da Iska ko wani ciwo da ya danganci Iska, wanda ba za a iya warkar da shi a asibiti ba.

Wani abin da binciken ya gano shi ne, shigowar Hausawa cikin }asashen Gbagyi domin ya]a addinin Musulumci da ma zuwan Turawan mishan don ya]a Kiristanci, gurgunta aiwatar da borin Hausawa da na Gbagyi suka yi, ba }arfafa su ba.

Binciken ya gano kuma cewa har ila yau, kusan dukkan 'yan borin Gbagyi, suna aiwatar da bori ne ta salon yadda suka ga 'yan borin Hausawa na aiwatarwa. A yau, sunayen Iskoki da tufafin 'yan bori da kayan ki]in bori da yanayin girka da sauran su, duk sun koma tamkar na Hausawa.

Bisa ra'ayoyin marubuta kamar: Besmer da Nicole da Yahaya da Gobir da Bunza da Badejo, na cewa bori a matsayin addinin gargajiya na Hausawa, yana faruwa ne a sanadiyyar kamuwa da Iska kuma sai an yi wa majinyaci girka. Bincike ya gano cewa a borin Gbagyi ba haka batun yake ba. Sallamar Iskan ake yi maimakon a yi girka.

Wannan bincike ya gano cewa ayyukan da aka yi na bincike-bincike da nazarce-nazarce a wa]annan fannoni ba su da yawa. Ana iya buga }irji a ce babu wani takamaiman aikin da aka gudanar wanda ya ]auki borin Hausawa ya kwatanta shi da na Gbayi. Don haka, wannan aiki shi ne irinsa na farko a wannan fanni a iya sanin mai bincike.

Kamar yadda aka riga aka ambata a baya, ana fata wannan bincike zai }ara fahimtarwa da ba da haske a kan borin Hausawa da na Gbagyi, ya kuma zama wani harsashi ne na kafa wani sabon bincike a wannan fage. Da fatan manazarta za su ci gaba da yin bincike a kan borin Gbagyi domin cika sa gi~in da wannan bincike ya bari, don amfanin al'umma a yau da gobe.

## 5.3 Shawarwari

Ko ba a fagen bincike ba, a harkokin yau da kullum ma shawara na da muhimmancin gaske. Ganin haka ne aka ga ya kamata a gabatar da shawarwari ga Gwannatin Tarayya da na Jihohi da na }ananan Hukumomi da masana da ma'ilmanta da ]alibai da manazarta da ma al'ummomin Hausawa da Gbagyi baki ]aya.

Kawo duka shawarwarin da ake da su a nan ba zai yiwu ba, saboda haka aka ga ya dace a kawo su a ta}aice kamar haka:

a. Ya kamata Gwamnatin tarayya da ma na jihohi su agaza wa jami'o'i da sauran makarantu da ]alibai masu gudanar da bincike a fannoni daban-daban na harshen Hausa da ku]i domin }ara masu }arfin gwiwan yin bincike ingantattu. Makarantu kuma su gina isassun ]akunan nazari da sayen litattafai masu muhimmanci.
b. Zai kyautu idan Gwamnatin }ananan hukumomin jihohin al'ummun da aka yi nazarin borinsu za su ke~e wani lokaci a duk shekara domin raya al'adu musamman ma bori saboda muhimmancinsa wajen taimaka wa majinyyata da suka kamu da Iskoki wanda ba ciwo ne na asibiti ba.
c. Yana da muhimmanci idan za a yi }o}arin samar da takamaiman tarihin asalin al'ummar Gbagyi domin akwai tababa tsakanin masana da manazarta game da tarihinsu.
d. Al'adun Hausawa na da saurin mamayar na sauran al'ummu da ke makwabtaka da su, su mayar da su Hausawa. Saboda haka ina kira ga al'ummomin da su farka su raya al'adunsu

na gargajiya da kyau, kar su bari al'adun su ~ace saboda muhimmancinsu ga rayuwar al'umma.

e. Masana da manazarta, kamata ya yi su yi:

i. Taron }asa da }asa na bita a kan borin Hausa da na Gbagyi

ii. {ago litattafan karatu kan al'adun Hausawa da na Gbagyi

iii. A taskace su a gidajen rediyo da talabijin da ma fayafayen CD.

iv. A yi yun}urin rubuta kundayen digirin M.A. da PhD a fagen bori

v. A shirya gasar fito da Gwaraza a fagen Al'adu da Adabi da Harshe

vi. Fito da tsarin yi wa gwaraje kyautukan girmamawa

vii. Bun}asa cibiyar taskace al'adu da adabin Gbagyi.

f. A }arshe za a yi kira ga ]alibai da manazarta su san cewa wannan bincike ba wai an }are shi ba ne, a'a' wani harsashi ne na kafa wani sabon bincike kan 'Kwatancin Borin Hausawa da na Gbagyi'.

**Manazarta**


Abdullahi, I.S.S. (2008). Jiya ba Yau ba: Waiwaye a kan Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin digiri na uku (PhD). Sakkwato: Sashen koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman [anfodiyo.

Abdullahi, G.W.(1991). Tasirin Hausawa a Tarihin Afirka ta Yamma. Fassarar Littafin '*The Hausa Factor in West African History*' Na Mahdi Adamu, kundin Digiri Na Biyu, Zariya: Sashen Harsunan Afrika da Al'adu, Jami'ar Ahmadu Bello.

Abubakar, S.Y. (1997). Bori a Zariya, kundin digiri na biyu M.A.; Zaria: Sashen Harsunan Afrika da Al'adu, Jami'ar Ahmadu Bello.

Abubakar, J.(1977). The coming of Zegi-zegi and its effect on Koro/Gwari Relationship in 19th century B.A. Disertation, Department of History, Ahamadu Bello University, Zaria.

Adamu, M.T. (1983). Asalin Tsibbu, Ya]uwarsa Da Tasirinsa Ga Al'ummar Hausawa. Kundin Digiri na farko, Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Alhassan, D.Y. (1987). Dangantakar {asar Hausa da Ma}wabtansu: Musamman {asar Gwari. B.A. Dissertation: Kano: Department of Nigerian Languages, Bayero University.

Arohunmolase, O. (1999). Nigerian Indigenous Curative Medicine: Efficacy and Problems. In Arohunmolase O. (ed) *Nigerian Languages in Scientific and Technological Advancement.* Akure: JBS Printing and Publishing Company.

Badejo, P.A. (1980). Bori Spirit Possession Religion as a dance event: A Pre-Islamic Hausa Phenomennon, M.A. dissertation University of Califonia, Los Angeles.

Bergery, G.P. (1934). *A Hausa-English and English-Hausa Vocabulary*. Oxford University Press.

Besmer, F.E. (1973 a). Avoidance and Joking relationships in Hausa Supernatural Spirits. *In Studies in Nigerian Culture.* Kano: Bayero University.

Besmer, F.E. (1973 b). Praise – epithets and song texts for some important Bori Spirits in Kano. In *'Harsunan Nijeriya'.* Kano: Bayero University.

Besmer, F.E. (1975). Boorii: Structure and Process in Performance, *Folia Orientalia*, 16:101-300.

Besmer, F.E. (1977). Initiation into the Bori Cult: A case study in Ningi Town in Africa, 47: 1- 13.

Bunza, A.M. (1989). Haya}i Fid da na Kogo Kundin Bincike na Digiri na Biyu (M.A.), Sashen Nazarin Harsunan Najeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Bunza, A.M. (1995). Magungunan Hausa a Rubuce: Musamman Nazarin Ayyukan Malaman Tsibbu, Kundin Digiri na Uku (PhD), Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Kano. Jami'ar Bayero.

Bunza, A.M. (1991). Ra]a]i Da Zogin Cuta A Ma'aunin Bahaushe. Mu}alar taron {ara wa juna sani, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Sakkwato: Jami'ar Usman [anfodiyo.

Bunza, A.M. (1996). Nazarin Tsibbu A Barkwance. Ma}ala a Cikin Mujallar Juyayiyin Masana. Ed. Bunza, A.M. & Gusau, S.M. Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman [anfodiyo.

Bunza, A.M. (1999). Language in the context of healing: The Relevance of Incantational Forces In Hausa Healing Art. In Arohunmolase O. (ed) *Nigerian Languages in Science and Technological Advancement.* Akure: JBS Printing and Publishing Company.

Bunza, A.M.(2004). Magana da Iskoki ta Bakin Dokinsu. Taron }ara wa juna sani, Kano: CSNL, Jami'ar Bayero.

Bunza, A.M. (2005). Booru}iyya: (Tazarar Bori da Ru}iyya a Idon Manazarta). Takardar taron }ara wa juna Sani, CSNL, Kano: Jami'ar Bayero.

Bunza, A.M .(2006). *Gadon fe]e Al'ada*, Lagos,Tiwal Nigeria Ltd.

Busa, M.A.(1992). Cuta da Magani a }asar Gwari: Dangantakarsu da na }asar Hausa. Kundin bincike na Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Byamyiko, N. (1997) *Topics in Gbagyi History*, Jos: Idakula Press.

CNHN. (2006) *{amusun Hausa*; Zaria, Ahmadu Bello University Press Limited.

DjeDje, J.C. (2008) *Fiddling in West Africa: Touching the spirit inFulbe, Hausa and Dagbanba cultures,* Bloomington: Indiana University Press.

[an'Asabe, K.M. (2006) "Tasirin Al'adun Hausawa a kan na Gwarawa". Kundin digiri na biyu, Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Danladi, D.(1999). Tasirin Hausa a wa}o}in Gwari, kwatanci da wa}o}in Walo Shatan Gwari, kundin Digiri na farko da aka gabatar wa Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Afirka, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Dutse, Y.A. (1989). Yadda ake hawan Bori da Iskokin da ake kira. Kundin digiri na ]aya, Kano; Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Daura, B. da wasu (1968). *Hausa Customs*, Zaria; N.N.P.C. Ltd.

[angambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa (Sabon Tsari*), Zaria; Amana Publisher Limited.

Fadason, A.A. (2008). *Wasu Al'adun Gbagyin Masarautar Gbagyi*, Kaduna: Nasarawa Printing Press Ltd.

Fagge, U.U. (2000). *Ire-Iren Karin Harshen Hausa Na Rukuni,* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Filaba, M.A. (2009). Gbagyi History and Future. In Gbagyi Journal Vol.2 No.4 (ed) Je'adayibe, G.D., Abuja: Gbagyi Vision Publishers.pp.36-59.

Filaba, M.A. (1994). Karu, Kurape and Kurkundu kingdoms: A History of Social, Economic and Political changes among the Gbagyi in Central Nigeria" M.A. Thesis, Zaria: Department of History. Ahmadu Bello University.

Galadima, N.K. (1982). Kuta Yesterday, Today and Tomorrow. A public address paper presented at Kuta; Youth Association Meeting.

Gobir, Y.A. (2001). Iskoki a Idon 'Yan bori da masu Rukiyya. Kundin Digiri na Biyu, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Sakkwato: Jami'ar [anfodiyo.

Gobir, Y.A. (2010). Hul]ar Soyayya Tsakanin [an Adam da Iska. Cikin *KONJOLLS:* Kontagora Journal of Languages and Literatures. Kontagora: Federal College of Education.

Gobir, Y.A. (2013). Iska a Tunanin Bahaushe a }arni na 21st". Sashen koyar da Harsunan Nijeriya. Sakkwato: Jami'ar Usman [anfodiyo.

Greenberg, J.H. (1941). The Influence of Islam On Sudanese Religion, In Marian, W.S. (ed) *Monographs of the American Ethnological Society,* New York: j.j. Augustin Publisher.

Habib, A. da Wasu (1982). *Zaman Hausawa,* Sokoto state Ministry of Education.

Ibrahim, M.S.(1982). Dangantakar Al'ada da Addini Tasirin Musulunci kan Rayuwar Hausawa ta Gargajiya. Kundin digiri na biyu, Sashen Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Ibrahim, D. B. (1986). A Study of Some Aspects of Ritual and Ceremonial Costume of the Hausa In Kano, Kaduna and Sokoto States. A seminar Paper presented at Ahmadu Bello University,

Zaria.

Jemkur, (1983). The Prehistory of Northern Nigeria. Studies of Nigerian Culture 1. Zaria, Gaskia Press.

Kirk-Greene, A.and Ryan P.(1975). *Some Peoples of Nigeria*, Knaphill Survey: Pikin Publications Ltd.

Koce, S.G. (2002). Gbagyi Culture in Contemporary Nigeria. *Gbagyi Journal* Vol.1 No.2 Abuja: Garkida Press Ltd.

Magaji, R. (2004). Gbagyi People and Contemporary Kaduna: The Gains and Losses. A Paper delivered on the occasion of the Meritorious Awards Presentation and launching of the Igabi Gbagyi Development Union Almanac.

Maikanti, S. (1997). Tasirin Al'adun Hausawa da na wasu Kabilu mazauna Wushishi: Tsokaci a kan }abilun Nufawa, Gwarawa, Dukkawa da kuma Kambari. Kundin Digiri na ]aya, sashen koyar da Harsunan Nijeriya, Sokoto: Jami'ar Usman [anfodiyo.

Maikanti, S. (2010). Borin girka. [un]aye Journal of Hausa Studies. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University, Vol.1, No.3.

Martyn, J.L. "Devil". Microsoft ® Student 2008 (DVD). Redmond, WA: Microsoft Corporation, 2007.

Mbiti J.S. (1991). *Introduction to African Religion, Second Edition*, Halley Court; Jordan Hill, Oxford OX2 SFJ; Heinemann International Literature and Text books.

Meek, C.K. (1925). *The Northern Tribes of Nigeria,* Oxford University Press, London: Humphrey Milford.

Muhammed, D. (ed.) (1990). Hausa Metalanguage ({amus a ke~a~~un kalmomi) vol.1, Ibadan, University Press Limited.

Na'ibi, S. and Hassan (1969). *The Gwari Tribe in Abuja Emirate*, Ibadan: University Press.

Na'ibi, S. and Hassan (1969). *The Gwari, Gade and Koro Tribes*, Ibadan: University Press.

Na'ibi, S. (1962). *A Chronicle of Abuja*, Ibadan; University Press.

Newman, R. (1997). *An English-Hausa Dictionary*, Lagos: Longman Nigeria Plc.

N.N.P.C. (1977). *Labaru Na Da, Da Na Yanzu*, Zaria; Northern Nigerian Publishing Company Limited.

Nicole, E. (1991). *The Hausa Bori possession Cult in Adar Religion of Niger: Its origin and present day function.* In Women's medicine: the Zar-Bori Cult In Africa and beyond. Internatioinal African Institute, Edinburgh University Press.

President (2005 b). The Gbagyi people and Historical consciousness, Being a paper Presented at the Gbagyi Students Association (GBASA) Day, A.B.U. Zaria Branch, at the drama village, on Saturday, 27th August,2005.

Sani, M.G. (1991). Sarauta a Minna, B. A. Dessertation, Department of Nigerian Languages, Kano; Bayero University.

Shekwo, J.A.(1986). The Origin of the Gwari People, The African Guardian Magazine. March 20, 1986.

Skinner, N. (1965). Kamus Na Turanci Da Hausa, Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Smallwood, J.M. (1932). *General Notes on the Gwari Tribes, Keffi Emirate*. SPN17/K3148;1932 AREWA HOUSE. Special memorandum. No, 25".

Temple,O. (1965). *Notes on the Tribes, Provinces, Emirates and States of Northern Provinces of Nigeria.* (ed) C.L.Temple, 2nd edn. London.

Tremearne, A.J.N. (1914). *Hausa Superstitions And Customs*. John Bale, sons and Danielsson, LTD Oxford.

Uba, A. (2006). Kwatanta Bori da Ru}iyya wajen neman waraka. In 'ZOBIAWA' Journal of the Department of Nigerian Languages. Ondo: Adeyemi College of Education: Ife Oluwa Press, Vol 2.

Yahaya, I.Y. da Wasu, (1992). *Darussan Hausa*. Don Manyan Makarantun Sakandare – 3, Ibadan: University Press Plc. By Olaniyan Publishing Company, Akure: Ijapo Estate.

Yahaya,I.Y. da Wasu, (2004). *Jagoran Nazarin Hausa*, Zaria:Northern Nigeria Publishing Company Limited.

Ziky O.K. & et-al (1987). Hausa Performing Arts and Music. A Nigeria Magazine Publication.

**RATAYE NA [AYA**

Hira

Sashen Harsuna da Al'adun Afrika
Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya
Jihar Kaduna – Nijeriya
20 ga Yuni, 2011.

Malam /Malama

**Neman Umarnin Yin Hira da Kai/Ke**

Bayan gaisuwa da fatan alheri. Ina mai farin cikin gabatar da kaina a matsayin ]alibi mai neman digiri na biyu a harshen Hausa a Sashen Harsuna da Al'adun Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

{a'ida ce ga duk wanda ke neman Digiri na Biyu ya gudanar da bincike a kan wani batu da ya shafi fannin ilimin da ]alibi ya ]auka. Don cika wannan }a'ida, na }udiri niyyar gudanar da bincike ne a kan batu mai take "KWATANCIN BORIN HAUSAWA DA NA GBAGYI".

Wannan ya sa nake neman amincewa, ka/ki ba ni ka]an daga cikin lokacinka/ki mu yi hira, mu tattauna a kan wannan batu a matsayin ka/ki na wanda ke zaune a }asar Gbagyi. Hirar an shirya ta ne don a gano borin Hausawa da na Gbagyi wanda zai taimaka wajen tantance irin kamanci da bambanci da aka samu sanadiyyar zaman tare a ~angaren bori.

Ina mai tabbatar maka/ki cewa duk bayanin da ka/kika bayar ba za a yi amfani da shi a wani wuri ba baya ga wannan bincike.

Bayanan da ka/kika bayar za su taimaka a fagen bun}asa ilimi da nazarce-nazarce musamman a ~angaren borin al'ummomin Hausawa da Gbagyi.

Nagode. Da fatan zan sami cikakken ha]in kai don cimma wannan manufa tawa ta kwatanta borin Hausawa da na Gbagyi.

Ka/ki huta lafiya.

Haliru Musa Kuta

**'Yan Borin da Aka yi Hira da su**

Adamu Kambari Kuta: An yi hira da shi a ranar Jumma'a 29 ga watan Yuli, 2011 a garin Kuta.

Wasa Sarkin Bori Kuta: An tattauna da shi a ranar Jumma'a 29 ga watan Yuli, 2011 a garin Kuta.

Musa Shangbah, Sarkin 'yan borin Gbagyi na jihar Neja: An tattauna da shi ranar Asabar 30 ga watan Yuli, 2011 a Kuta.

Amina Ma'aji Bosso: An yi hira da ita ranar Talata 9 ga watan Afrailu, 2013 a gidanta a Unguwar Bosso-Minna.

Lamunko mai Bori Dutsen-Kura: An yi hira da ita ranar Talata 9 ga watan Afrailu, 2013 a gidanta na Dutsen-kura Minna.

**Mutanen da aka tattauna da su:**

Farfesa Sa'idu Muhammad Gasau, Department of Nigerian Languages and Linguistics, Bayero University, Kano ranar 13/12/2012

Farfesa Aliyu Muhammad Bunza, Department of Nigerian Languages, Usman [anfodiyo University, Sokoto ranar 14/12/2012

Dakta Tahir Ahmed Adamu (Baba Impossible), Department of Nigerian Languages and Linguistics, Bayero University, Kano ranar 13/12/2012

Mama Habiba Kuta, ranar Juma'a 1/02/2013 a garin Kuta.

Sarkin Ija-Gwari, an tattauna da shi a ranar Asabar 13 ga watan Afrailu, 2013 a Ija-Gwari (FCT).

Malama Hauwa Muhammad Bugaje, Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria ranar 16/04/2013

Malama Halima Kabir Daura, Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria ranar 17/04/2013.

Malam Adamu Ibrahim Malumfashi, Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria ranar 18/04/2013

Malam Muhammad Rabiu Tahir, Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria ranar 18/04/2013.

Malam Kabir Muhammad [an'asabe, Darekta, Niger State Council of Arts and Culture, Minna ranar 8/04/2013.

Dakta Aliyu Muhammad Busa, Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria ranar 9/04/2013 a gidansa na Minna.

## RATAYE NA BIYU

### Wasu daga cikin Tambayoyin Bincike

Wa]annan suna daga cikin tambayoyin da aka yi wa jama'a domin jin ra'ayoyinsu.

A fahimtarki/ka, me ake nufi Kalmar "Bori?"

A da can, Hausawa sun ]auki Bori a matsayin addini ne ko al'ada?

A ina borin Hausawa ya samo asali?

A ina borin Gbagyi ya samo asali?

Akwai dangantaka tsakanin Hausawa da Gbagyi kafin zuwan addinin Musulumci ko sai bayan zuwan addinin?

Shin ana aiwatar da borin Gbagyi na asali a yau?

Idan ba haka ba, me ya haddasa sauyi?

Akwai kamanci a borin Hausawa da na Gbagyi ko babu?

Shin akwai bambanci a borin Hausawa da na Gbagyi ko babu?

Bayan shigowar addinin Musulumci da ma na Kirista, wasu al'ummun Hausawa da na Gbagyi sun daina bori ko har yau suna yi?

Bori na da muhimmanci ko amfani ga al'umman Hausawa da na Gbagyi ko babu?

Idan an yarda bori na da muhimmanci ko amfani ga al'ummun biyu, to a rubuta biyu daga ciki?.

Rubuta rashin muhimmanci ko amfanin bori guda ]aya da aka sani?.

**RATAYE NA UKU:** HOTUNA





'Yar Borin "MADAWA" ri}e da ]an gatari da ake kira 'Azebyi' da harshen Gbagyi.



‘Yar Borin (Gbagyi) a tufafin Fulani kaman na mai Iskan Bafulatana a Borin Hausawa.



‘Yan Borin Gbagyi cikin jajayen tufafi bayan tasirin na Borin Hausawa.




Wannan hoto na tufafin ‘yan borin Gbagyi (Madawa) ne.



Kayayyakin ‘yar Borin ‘Madawa’ kwatankwacin na Iska (Bafulatana) a borin Hausawa.



Kayyakin borin Gbagyi. (Boehyi-akaya) bayan girka Kaman na borin girkan Hausawa.



Wasu daga cikin tufafin borin Gbagyi masu kama da na Hausawa.




‘Yan wasan “Kabulu” na Gbagyi, da irin kayan ki]an borin “Madawa”.



Maka]in tulu na borin Gbagyi mai suna “Gbunu”.



Hoton mata ‘yan rawan borin Gbagyi a dandali.




Misali na hoton wasan borin Hausawa a dandali.



Maka]in goge da ‘yan rawa a dandalin borin fage na Hausawa



Maka]in ‘yan borin Hausa, Musa [an Gado Saminaka (mai goge 2003)




Musa Shangbah, Sarkin ‘yan borin Gbagyi na jihar Neja.



Maka]an borin Gbagyi, da kwatankwacin irin kayan ki]in borin Hausawa.



Musa Shangbah da yaransa, a yayin wasan bori a dandali.



‘Yan borin Gbagyi, suna wasa a dandali.



Musa Shangbah sarkin borin Gbagyi na jihar Neja, a dandalin wasa.



Suturan ‘yan borin Gbagyi maza



‘Yan rawan borin Gbagyi a dur}ushe suna gaisuwa, a yayin rawa a dandali.



‘Yan rawan borin Gbagyi ]aya ya hau }irjin ]an uwansa, a yayin wasa a dandali.